Ana nan Allah ya bata ciki ta haifi da namiji aka sanya mashi suna Zakariya'u bayan wasu 'yan shekaru kuma ta sake samun ciki ta haifi ya mace aka samata suna Maryamu daga nan sai aka samu cikin Muhammadu, bayansa kuma sai aka samu cikin Mallam Abdulkarimu (Sarkin Zazzau). Abdulkarimu ya yi zamansa a Katsina inda anan ne ya yi Aure ya haifi iya Aliyu saman daga nan shi da dan uwansa Zakariya'u sukayi shawara dasu kara shiga kasar Hausa dan yin wasu Littafai, shi Zakariya'u ya wuce zuwa Sakkwato shi kuma Abdulkarimu ya tafi Kano. Inda ya samu shekara bakwai a Kano, bayan barinsa Kano sai ya nufo Zariya inda yazo gidan limanin kona ya yi karatun wasu littafai har tsawon shekara goma sha shidda a wurin Limanin kona na Zariya bayan samun wannan ilimi sai ya koma hanya zuwa Sakkwato inda ya wuce wurin Shehu Usman Bin Fodio (Mujaddadi) jin labarin bayyanarsa.

Mallam Abdulkarimu ya isko Shehu Usman a sifawa inda ya tadda mujaddadi alokacin da ya rabama Mallam Abdullahi (Kaninsa) da

Mallam Muhammadu Bello (dansa) yankin mulki don jaddada Addinin Musulunci, Mallam Abdulkarimu ya zauna na tsawon wani lokaci da shehu Usman kafin ya turo shi a shekarar 1804.

Mallam Abdulkarimu ya ziyarci Shehu Usman a wurare da dama kamar haka:- Ya ziyarce shi a shekarar 1812 a sifawa, kuma ya ziyarce shi a lokacin da yazo daga Zariya don yarda dashi da akayi akan a bashi sarautar sa'i a shekarar 1814 - 1815 lokacin da mujaddadi ya taso daga sifawa zuwa Sakkwato.

Kuma ya tafi Sakkwato ta re da Sarkin Zazzau Mallam Musa dan ta'aziyar Shehu Usman a shekaran 1817 inda suka taradda an baiwa sultan Muhammadu Bello halifan Shehu Usman.

Kuma shi sultan Muhammadu Bello shine ya nada Mallam Abdulkarimu Sarkin Zazzau a shekarar 1816.

Mallam Abdulkarimu ya gina garuruwa kamar Kachia, Makarfi, Giwa, da Nasarawan Koto, kuma saboda Amana da gaskiya a wannan lokaci yana nan bashi sarautar sa'i saboda sanin halayansa, wato ma'anan sa'i shine mai tara zakka da rabawa.

Kuma ya zauna a garuruwa da dama kamar garin biye dake Giwa ta Zariya sannan ya dan jima a wani gari da ake cema walijo cikin kasar Kachia sannan kuma da garin da ake cema jere cikin kasar Kagarko.[8] Haka kuma Sarkin musulmi Bello yazo Zariya a shekarar 1835 lokacin da Sarkin Zazzau Mallam Abdulkarimu ya nemi da yazo dan yaga wurin da yake so ya gina masallaci.[9]

Kuma Sarkin musulmi Bello yazo ya sa turben qinin kuma yace Allah yayi masa sakaiyya da Alherinsa akan irin wannan aiki.

Sarkin Zazzau Mallam Abdulkarimu ya rasu ya bar 'ya'ya guda Bakwai[10] kuma uku daga ciki sunyi sarautar hakimci, daya kuma ya yi

Sarkin Zazzau qasu kamar haka-Iyan Zazzau Aliyu, Iyan Zazzau Usman, Magajin Cari Muhmudu Baba qana, Sarkin Zazzau Sambo, Mohammadu Dari, Muhammadu Dan Atu, Mu'aliyidini.

SARKIN ZAZZAU MALLAM ABDULKARIMU YA ZAMA SARKIN ZAZZAU (1834 - 1840)

Kamar yadda na fadi a baya cewa Sarkin Zazzau Mallam Abdulkarimu, shine sarki na uku a cikin Sarautar daular Fulani Zazzau, kuma shine na farko a sarautar gidan Katsinawa, wadanda suke sarauta a'yanzu.'

Mallam Abdulkarimu' ya iso Zariya bisa bin umurnin Shehu Mujadadi da yazo ya kasance tare da Mallam Musa da Yamusa, a kasar Zazzau kasancewarsa mutum mai ilmi kwarai da tsoron Allah har sai ya kasance mutane nace masa waliyyi ko kuma Bawan Allah, ganin wadannan halaye da kuma irin yawan ilimi da Allah ya ba shi sai sarkin Zazzau Mallam Musa ya yi masa sarautar sa'i kuma shine ya fara yin wannan sarauta ta sa'i a Zazzau. Sannan kuma gashi Auratayya ya shiga a tsakaninsa da sarkin Zazzau Mallam Musa.

Bayan mutuwan Mallam Musa sai Mallam Yamusa ya zama sarki, kuma Mallam Abdulkarimu yana nan a sa'i har zuwa wani lokaci bayan an sami chanje - chanje na sarauta a tsakanin gidan Mallam Musa da na Yamusa, ana nan kuma har ta kado kan sa'i Abdulkarimu, bayan wasu shekaru kadan sai sarkin Zazzau Yamusa ya rasu, kuma ya yi shekaru goma sha hudu da watanni yana mulki, a wannan lokaci sai rigimar sarauta ta taso a tsakanin gidajen biyu wato gidan Mallam Musa da gidan Mallam Yamusa, daga nan sai aka fahimta da cewa akwai

rigingimu a cikin al amarin Zaben sarkin Zazzau daga waddannan gidaje biyu.

Ganin irin abubuwan da suka faru a baya lokacin mulkin Sarkin Zazzau Yamusa ta yadda ya cire wasu daga cikin ya'yan Mallam Musa daga kan mukamansu ya baiwa ya'yansa sai su mashawartan ga wato)limamin Juma'a da Galadima bokaje) suka yi shawara kuma suka aika da ita Sakkwato da cewan babu wanda ya kamata ya yi sarautar Zazzau sai sa'i Abdulkarimu duk da sanin cewa Abdulkarimu bai yi karfi kamar sauran wadannan mutane ba. To amma duk da haka aka tsaya akan cewa in dai ana son zaman lafiya da ciguba to sai a baiwa SA'I Abdulkarimu Sarautar Zazzau domin shine kawai hanyar da zai kawo sauki gabar sarautar a sauran gidajen, tare da kyakkayawan mulkin Juma'a.

SARKIN ZAZZAU MALLAM SAMBO (1879 - 1888).

Mallam Sambo, (Sarkin Zazzau) yana daya daga cikin ya'yan Mallam Abdulkarimu Sarkin Zazzau, kuma shine ya gaji Sarkin Zazzau Abdullahi ne gidan Barebari wanda ya samu shekara biyar da watanni (1863 - 1879) yana mulki, ko daya ke shi Sarkin Zazzau Abdullahi ya taba yin sarki kafin wannan lokaci kuma ya gaji sarkin Zazzau. Abdussalam kuma ya samu shekara goma (10) da watanni yana mulki, (1860 -1863) daga nan aka fidda shi aka nada Sarkin Zazzau Mallam Abubakar daga gidan Mallawa, shi kuma ya samu shekara uku (3) da watanni yana mulki (1873 - 1876) a wannan lokaci akwai manya manya ya'yan sarki daga cikin sauran gidajen sarauta na Mallawa da Barebari, kamar su Madaki yero da Zubairu dan Sarkin Zazzau Musa,

shi kuma Sambo a wannan lokaci yana rike da sarautar Wambai, ganin cewa gashi Sarkin Zazzau Abdullahi ya rasu sai aka fara shiri a neman wanda za'a nada Sarki a wannan lokaci, inda aka fitar da sunan wadannan 'yan Sarki guda uku (3) daga kowani gidan sarauta, kuma a ka yanke shawaran a tafi dasu Sakkwato domin zabe, kusan dama haka akeyi idan Sarki ya mutu, akan tafi da mutane ya'yan sarki domin zaben wanda ya can-canta a wannan lokaci, wanda ya yi jagorancin su shine Galadima Zazzau Adamu. Suka isa Sakkwato akayi zabe. Mallam Sambo ya'hau gadon Sarauta bayan ga duk irin kaiwa da komowa da akayi daga nan Mallam Sambo ya fara shirye - shirye na tafiyar da aikin mulki, inda ya nada wasu daga cikin 'yan Uwansa sarautu kamar haka: Mallam Babagana a Matsayin Magajin Garin, Mallam Usman a Matsayin Iya, haka kuma ya nada dansa Tsoho a Matsayin Makama Karami, Mallam Lawal a Matsayin Madaki. ...

Sarkin Zazzau Mallam Sambo yana da ya'ya har su hamsin da biyu wadanda yake wasu ba zai yiwu a kawo su ba saboda sun dade da rasuwa, kadan daga cikin yayan da aka samu sune, aka rubuta su a cikin wannan tarihi, a cikinsu an nuna wasu daga ciki wadanda suka rike sarautar Hakimci ya'yansa da basu rike sarautar hakimta ba akwai Mallam Idrisu wanda yake shi ya rike sarautar mai Anguwa, shine mai anguwa Idrisu Auta, kuma shine Autan Mallam Sambo kuma shi an haifeshi a Sakkwato ne, kuma shine ya haifi mai Martaba Sarkin Zazzau Shehu, shi yasa na fada cewa dole sai na dauko ta tushe sanan a fara bada tarihin mai martaba Sarkin Zazzau Shehu Idris.

MALLAM IDRISU AUTA.


Wannan bawag Allah wato Mallam Idrisu Auta wanda aka fi sani da Mai anguwa Idrisu, shi dan Sarkin Zazzau Mallam Sambo ne. Kuma an haife shi a Sakkwato lokacin da Sarkin Zazzau Sambo aka fiddashi aka kira shi Sakkwato daga baya Sarkin Musulmi yasa aka dauko wadannan ya'ya guda biyar da ya haifa a can aka kawo su Zariya wadannan 'ya'ya sune Abdulkadir, Ahmadu, Idrisu Auta, kuma a matan sune Rabi'atu da Hauwa.

Mallam Idrisu Auta ya rayu a nan gidansu dake Rimin Tsiwa cikin Zariya tare da sauran 'yan uwansa. Mallam Idrisu ya rike mukamin mai anguwa har zuwa lokacin mulkin Sarkin Mazzau Ja'afaru, har ila yau kuma Allah ya albarkace shi da Zuri'a daya haifa a cikin su ne aka samu mai Martaba Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris Sarkin na budu a gidan Katsinawa kuma na goma shatakwas a mulkin daular Fulani a kasar Zazzau, sauran wadannan ya'ya sune kamar haka kafin mu nuna a taswira ta kasa.


Mallam Abdulkarim Idris, (Dan Isah Zazzau I), Mallam Uwais Idris (Dan Isah Zazzau II), Alhaji Abubakar Akibiya, Mallam Iguda Idris, Mallam Ibrahim Idris (Dan Madamin Zazzau), mai Martaba Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris, Alhaji Aliyu Idris (Wakilin Fulani), Mallam Akilu Idris.

Haka kuma a ya'ya mata a kwai Hajiya Safiya, Hajiya rakiya, Hajiya Zainab, Hajiya Si'adatu, Hajiya Hafsatu, Hajiya Bilkisu, Hajiya Maimuna, Hajiya Aishatu, Hajiya Salaha, Hajiya Maiyo, Hajiya Sumaye, Rabiatu, Hauwa, Hamdatu, Rabiatu, Halimatu.


Wadannan sune ya'yan Mallam Idrisu Auta kamar yadda aka samu. Ga suna yan a tsari cikin taswira tun daga kakan su Abdulkarimu




Abgesamt sind 'ein Sechstel Zucker, Butter und Mehl' 250 g. Wie viel Gramm ist ein Sechstel von 250 g? Ein Sechstel ist ein Teil von sechs gleichen Teilen.




Wannan shine taswirar Iyan Zazzau Alu.







CEDDERTIASCHR
20 [illegible]
LIBRARY


Wanan itace taswiran Magajin Gari Baba Gana da Tawagansa da suka [illegible]






Wannan itace taswiran Gidan Mallam Muhammadu Dan Atu kamar yadda take a cikin taswira.





Wadannan sune ya'ya da jikokin Madaki Lawal dan Sarkin Zazzau Sambo,
anan ~~mafi~~ anfani da ya'ya ne da jikoki kawai sabode haka in dai mai karatu
yaga kakanshi ko mahaifinsa to ya wadatar.



Tenan sbide cesmiar 'ya'ye da jikokin kaane isobo dan sarkin Zazzau Aliyu Sanyo.

SARKIN MALLAM ZAZZAU SAMBO

MALLAM KASIMU

ABDUL-JALI


SARKIN MAHAMUD RUWA	SARKIN YAKUBU RUWA	SARKIN BELLO RUWA	MALLAM ISIYAKU

SAIDU	AHMAD	DALHATU	IBRAHIM	BELLO
ABDUL-RAHIM	YAKUBU	MAHMUD	BASHARI	ABDUL-KARIM

MOHAMMED	ALIYU	HARUNA	BUHARI	YAKUBU	ABUBAKAR	SHEHU	ABDUL-JALI

ABDUL-JALI	SHEHU	JIBRIL	NUHU	YAHAYA	ALIYU	MAHMUD	MOHAMMED	AMINU	KASIMU	ABUBAKAR	MOHAMMED

[redacted]	[redacted]	[redacted]	ABDUL-[redacted]	[redacted]	[redacted]	[redacted]	[redacted]	[redacted]	ABDUL-JALI	LAWAL	MOH'D



Sauran wadannan mutane ukun ya'yan Mallam Abdul-wahab ya'yansu duka mata ne, saboda haka ya'ya da jikokin Mallam Mohammadu Dikko ne.

SARKIN ZAZZAU
MALLAM SAMBO

MALLAM KASIMU

WAKILI ABDULJALI


MAI ANGUWA SA'IDU	MOHAMMADU SAMBO	MALLAM NUHU	MALLAM KASIMU

MOHAMMADU	SAMBO	AMINU	SANI

ABDULHAMID	SA'ADU

AMINU

MUSA	YAHAYA


SARKIN MALLAM ZAZZAU SAMBO
MALLAM KASIMU
SA'I UMARU
M/TAFARKI ABUBAKAR
MALLAM IBRAHIM
S/TAFARKI ALIYU
MAI RIGAN KATSINA
MUHAMMED M.K.
ALHAJI JIBRIN
SA'I LAWAL
SAMBO
IBRAHIM
SA'I UMARU
ABDULRAZAK
UMARU
JIBRIL
ABDUL-KARIM
IBRAHIM
SEIDU
BASHARI
KASIRU
MOH'D
MOHAMMED
ALIYU
SEIDU
YASIDU
AHMAD
MOH'D
JIBRIL
MUSTA-PHA.

SARKIN MALLAM — ZAZZAU SAMBO

MALLAM KASIMU


MUHAMMEDU MAI RISA | S/HAUSAWA SHEHU | HARUNA BOYI | NASIRUDINI | HUSS GIWA


SANKI BATTANU | MALLAM HARUNA | ALHAJI ABDU | AHMADU

LUKMANU | AHMADU | SULEIMAN | SANI


MAGAJI

WAKILIN FULANI [illegible] | KASIRU | ABDULJALIL | GAMBO | KASIMU | HASSAN | HUSSAINI



SAN FRANCISCO
SAN JOSE
OAKLAND
SACRAMENTO
STOCKTON
FRESNO
BAKERSFIELD




Wannan : Qaswiran Wambai Bubari, Shi kuma yar'sa ɗaya ce kawai mace.




Shi Mallam Dalhatu Allah bai bashi haihuwa ba, ban suwa kanshen rayuwansa.



Wannan [redacted] taswirar Mallam Halidu Dan Makama Gsobo ya haifi da daya ne Yero shi ya haifi Muhammadu Mammale da Malam Baba.




Wannan itace tasirin Mallam Zaccau,
kuma shi Ya'yansa mata guda biyu ne
kuma.




Wannan itace tasvirar Mal. Adiyu Dan Sambo da jikokinsa

Kamar haka a [redacted].




Wannan taswira ta Mallam Saidu ya'yansa Guda Uku ne kawai Maza banda mata.


Kuma a ciki mallam Umaru ne kawai Allah yaba haifuwa gashin nan kamar baka.




Wannan itace taswirar Mallam Ahmadu da ya'yansa da jikokin
gasu kamar haka.



Wannan itace taswiran Mallam Abdulkadir Bam Barkin Bauchi Sambo,
kuma dansa daya ne na biyu sai nasa, daya, ga kuma dansa nan Ibrahim da nashi
ya'yan cikin taswira.




Wannan Itace taswirar mai Anguwa Idrisu Auta da 'ya'ya da jikoki



Wannan shine cigaban 'ya'ya da jikokin Mai Anguwa Idrisu Auta.

CIGABAN GIDAN IDRISU AUTA.



Wannan itace taswirar Mallam Idrisu Auta da ya'yansa da jikoki kamar haka.

APPENDIX 3

SAL MAN DUNA

Ladan Sani muazu 65 years

Abdulqadir Yusuf 61 years

Unguwar Habe ne, a kikin zamanin Habe a kwai wan mai arziki sunansa Duna, kuma shine Sarkin makare Zazzau. To yana da mata ana cemata salma. To a wannan zamani. Idan mutane za su je a sayo kaya waje salma, saboda attajira ce, sai ace kaje Gidan salma na duna a sayo abu Da ganman Anguwan ta samo sunanta Salmanduna.

Wasu kuma sun ce an sa mata saboda makera Duna. Nan inda massalachi yake a unguwar a halin yanzu Nan ne makeran take. Bayan jihadi, sai wani almajiri mai koyarda karatu Anace masa Mallam Musa shine wanda Mallan Musa ya soma sewa a Jekada Yazo ya zauna a unguwar. Ya rasu tsakanin Sarkin Zazzau yamusa da Abdkareem. Yana da yaya guda biyar. (1) Abubakar (2)Mohammadu (3) Daho (4) Abdu Jikan Jatau (5) Nana fatima

Zamanin Sarkin Zazzau Abdulkareem, shi kuma ya nada Mahmudu Salenken da yake malamine.

Ya rike sarautar Har zuwa zamanin Sarkin Zazzau Sidi Abdulqadri, yana Njalisar Sarki, Yana kuma alkalanci ya

Abubarkar yana yaya suna (a)kusamatu (b) Abubakar (c) Abdul

Yayan salenke suna (Shuhaibu Madaki (b)Galadima Turaki, (c) Muhammadu Lawal (d) Abdul (e) Usman Rano (f) Abdulqadri (i) Fatimatu

Dabo yana da yaya (1) Yanusa (2) Muazu (3) Abubakar (4) Ibrahim

Suna da Bayi da gonaki a kakeyi, isauni, yalwa da Tami (Igabi).

GIDAN WAKILIN DAJI

Su kuma yauwan Galadima Ahmadu ne

GIDAN KANWA.

Alhaji Umar Mohammadu 11-4-98 years, Gidan konwa.

Abinda ake sayarwa kenan shine kanwa shi wannan gidan mutane hudu suka kafa shi. Sune Badamisi da Hakimi da kuma mata guda biyu Shi Asalin gidan kuwa baiwa ne irin ta sarki sun zo daga Katsina kakanin nasu gidan daga wani gari kusa da caranci, Zamanin sarki Abdullahi. A lokacin gidan yana kusa da kasuwa ne, Fatake suna sauka suna sayar da kaya.

Shi hakimi Badamasi (1) Abdullahi (2) Abdulqadri (3) Muhammadu da mata guda hudu. Suna sayarda da kanwa kala ka kamar su Jan kanwa, kanwa da kuma in gurmi.

GIDAN TABA

March 1998, Fataimatu Gidan Taba

Suma sun zo araia nc. Asalinsu kuma larabawa ne suka zo suka zauna a Sokoto, da kakansu Musa dan Bagarmi da matanshi Ta Kogi Sukazo Zaria a wannan lokaci. Kakansu yasai musu wannan wauri daganan sai suka ci gaba da yain aikin Taba suna Sayarwa. Yayan su sune.

(a) Garba (b) Aliyu (c) Asbdullahi (d) Shuaibu (e) Abdullahi (f) Shuaibu (g) Shuaibu (h) Muhammaadu Lawal.

Garba yayansa sune (a) Abdullahi (b) Suleiman (c) Fatimatu (d) Hajara (e) Musa
Aliyu – (a) Ibrahim (b) Abdullahi (c) Aishatu (d) Rabiatu da sauransu
Abdullahi – (a) Garba (b) Aishatu 9c) Asma'u (d) Isuhu.
Shuaibu – (a) Ibrahim (b) haruna (c) sa adatu, Moh'd Bello
Usman (Badamasi) (a) Aliyu (b)Ahmed (c) Rabiatu.

DURUMIN MAIGARKE

Alhaji Ibrahim madaki Fawa 7-398 age 73 years.

Asalinsu Fulani daga katsina, sun zo Zaria lokaci sarki Zazzau Abdulkarecm, wanda ya soma zuwa ana cemasa Abubakar. Shi Ya haifi.

(a) Ibrahim mai kwafi (b) Baba Jatau (c) Maude Dan Baki (d) Hana lami, lokacin yayansa aka soma Fawa a gidan.

1. Shi Ibrahim mai kwafi yanyansa sune (a) Abdulkadri (b) Munini da mace sunanta lantana
2. Baban Jatau shine ya haifi Abubakar
3. Maude Dan Baki yanada ya mace ana ce mata Kwado.
4. Hanalami – (a) Abubakar (b) Walad0 9c) Burunga (mace), Gwari

Kusa da gidan akwai gida Abdulqadri wanda yake kanine ga wajen Abubakar.

Da sheanunsa yakare shi kanin sa sai ya tafi Gusau. Yana da yaya da yawa a can yako dinki sai yazo yanayi shi bai yi akin nama ba yayansa sune

(a) Uwa da rabi su

Kafin su zauna awurin ance wurin yana daga cikin gidan maigarke. Wanda uake shine sarki fawa lokacin habe.

ABDU BABAN FAWA:

GIDAN SARKI FAWA.

Sun zo daga Katsina ne daga wajen Bargaren Danja, sai suka tafi Sokoto daganan zamanin sarkin zazzau Abudlkareem suka Shiho Zaria.

Abdulkareem ya basu gidan anan. Sunan wanda ya taso daga Danji anace masa abdullahi shine ya haifi.

(1) Abdu (2) Ahmadu mai kigo (3) Baban Tasalla (Abdullahi) (4) Yanusa.

(1) Abdullahi shine ya haifi (a) Tanimu (b) Ummaru (c) Sarki awa Abdulahi (d) Kura (e) Kande 9f) Kande.

(2) Ahmadu shine ya haifi (a) Mai riga (b) Mai munatu (c) Baroki (d) Mallam Yalu (e) Ualwa.

(3) Abdullahi (Baban Tasalla shine ya haifi Tasalla.

Tanimu shin kuma shine ya haifi (a) aliyu (b) Mahmud Alu (c) Ummaru (d) Hajara.

Ummaru shi kuma ya haifi mallam yakubu (a) Mairo (b) Ahmadu (c) Abbas (d) Mamuda (e) Azumi (f) Alhaji (Jibrin) (g) Lubanhatu (h) Kyauta.

Sarki Fawa Abdullahi shine ya haifi (1) Mijin yawa (2) Ibrahim (3) Jibrin (4) Shuaibu (Informant) (5) Gambo (6) Laraha (7) Fidimatu (8) Salamatu (9) Hulliru (10) Shittu (11) Ibrahim (12) Dalhatu (13) Ummaru (14) Iya.

TARIHIN AHMADU MAI KIGO.

Yayi malam taka zamanin Sarkin zazzau kwassau ne lokachin da wannan gidan yzama Babban makarantan bida Ilimi a Zaria.

Zamanin Sarki Zazzau Alu Dan Sidi ne akayi Mashi sarautar Sarkin Fawa.

TARIHIN MALLAWAN ZAZZAU

Tarihi ya nuna cewa, mallawa wasu mutane ne da suka shigo kasa nan daga kasn mali a, dalihin yada addinin Musulunchi. Kamar yadda tarihi ya nuna, muslunchi yafara shigowa ne ta wasu sassa na kasashen Africa ta yamma, kamar kasar senegal da kasar mali a lokacin karni na goma sha daya, daga nan ya shigo Agades, Barno, da ganan kuma ya wuto zuwa kasar Hausa.

Mallawa sun fito ne daga cikin zuriyar Salmanul, Farisi daya daga cikin sahabban Annabi Muhammadu (S.A.W) Dalilin da yasa aka ce masu mallawa ya samo asali ne da zaman su amali bayan sun yi nisa da shiga kasashen duniya domin wannan aiki na yada addinin Musulunchi. Alocacin da sai yiddina Muawiyya dan safiyanu ya turo ukuba ibn Nafi ya kawo musulunci da littifai don fahimtar da Addini . Sai ya hada mashi da takarda da kuma umurin da ya biyo ta Mali don ya sadu da Sheikh Musa Taori wanda shike Alokacin shugaban wannan Alumma a she karar hijira ta Arbain wato miladiyya 660 karni na bakwai; Bayan sun sadu sai Sheikin Musa yayi mashin jagora zuwa waurin Kungiyar Fulani Torankawa da sullubawa wanda suke karka-shin shugabancin wani shaihun malami Shima mai suna Musa. Bayan kaddamar da wannan sako sai suka shigo kasa hausa daga Futa turo ta kasan malle don yada addini musulunchi tare da wadannan wakilai, Haka kuma daga cikin tsason wannar jinsi ne a aka samu Shehu Usman Ibn Fodio kuma aka sami Mallam Musa da ga cikin daya tsatson, wanda shine ya fara Sarautar Zazzau karka shin mulkin Daular Fulani.

MALAM MUSA

Malam Musa ya kasance tare da Usman Ibn Fodio akan hanyar neman Ilmi tun daga shekaran 1774. Alokacin da Shehu Usman ya tafi dashi kasar Kebbi dn yin wa'azi, bayan dawowarsu kuma ya dangana shi da malamin shi wato Sheik Jibril don neman Ilmin Addini.

Mallam Musa na daya daga cikin mutum bakwai da suka raka Shehu Usman zuwa Agades tare da malamin shi, mallam Jibril a cikin shekarar 1779, yayi karatun littafai da dama wurin Shehu Usman Ibn Fodio; Bayan dan Jimawa kadan sai mallam Musa Yanemi umurni da yana son yatafi Mali. Sabo da Ziyaran wani sheihin Malami a cikin shekarar 1787.

Bayan dawowar Musa a shekarar 1795 ya samu Usmanu yana shirya sabon tsarina zaman kungiyoyin musulumi da rushe kai dodin sarautar habe na kasar Hausa. Haka kuma ya sanya mallam Musa a matsayin wanda zai tabbatar da shiri Tare da tsarin makamai, har zuwa shekaran 1801.

Daganan aka fara shirin kaddamar da jihadin musulunchi. Bayan lokachin da sarki yunfa ya kai ma Shehu hari a tabkin kwatto a shekarar 1804 kuma Shehu yaci nasara a kanshi daga nan sauran sarakuna habe na kasashen Hausa suka fara Azabtar da musulmi a wannan lokaci.

MALLAMMUSA YAZO ZARIA A SHEKARAR 1804

A chikin shekarar 1804, Shehu Usman Ibn Fodio ya baima mutum goma sha hudu yardaddin shi kuma amintattun shi tuta don tabbtar da Jihadin musulunci a kasashen Hausa inda a ka turo Mallam Musa Zariya don wannan aiki na jaddada Addinin musulinci, inda yazo ya kori sarkin. Zazzau na Habe (makau). Bayan da Mallam Musa ya kore shi ya kafa mulkin daular fulani na

musulunchi a zazzau. inda ya raba ma mukarrabanshi (yan-kunan) mulki bisa yarda da Amana. Wadan nan mutane sune kamar Galadima Dokaje, Dallatu Hamza, Limamin Juma'a, Gabdo, Turaki Baidu, Sarkin Yaki mai Zabo, da kuma wasu wadanda aka tarrad da su a kasar ya kumai nada su mukamai.

A wannan lokaci duk wanda Mallam Musa Ya'Baima rikon wani yanki sai ya hada mashi da littafai guda biyu, na daya zai bash littafinnan da Mallam Shehu Ibn Fodioi Ya' Bashi wato Taj AL Din Fima Ya Jibu Ala Al – Mulk – Littafan da ake numa yanda ake mulki da kuma mulkin jama'a. shi wanna littafi shine Littafin da sarkin Kano Muhammadu Rumfa ya roki wani shehun malamin mai suna Al Maghili ya rubuta domin yadda zai tafiyar da mulkin shi a she karar 1483 – 1499.

Haka kuma da littafin nan mai tsarki na Tafsir Jalalaini wanda masha hurin malamin nan kuma waliyyi ya rubuta wato Abdurahman Ibn Abubakar Al Suyti malamin masar. Su wannan Littafai sune Mallam Musa yake rabawa limamin Jumu'ai da Alkalai a wannan lokaci, duk wadannan Abubuwa yayi hakane saboda a sami kyakiyawar mulkin da tsari mai kuwu wanda ya dace da shari'a.

Bayan irin wadannan mutane kuma akwai wasu mataimaka da Shehu Usman ya hada shi da su kamar Mallam Yamusa da Mallam Abdukarimu. Wadanda sune suka kafa gidan Sarautar Barebari da Katsinawa bayan mulkin Musa, kuma kowanne daga cikin su yayi sarautar Zazzau kuma dalilin su ne yasa a ka sami karin gidan sarautu a Zazzau har guda uku, wanda na hudu shine gidan sulluba wa wanda ya samu karkashi Mallam Abdusalami amma a lokaci Mallam Musa babu wani gidan sarauta bayan gidan mallawa a wannan lokaci.

A cikin shekara 1815, Mallam Musa ya tafi Sakkwato (Sokoto) domin ya sami bayanin cewa Shehu Usman yataso daga sifawa ya dawo sokoto bayan kafa garin da akayi a cikin shekarar 1809.

A lokaci da mallam Musa yatafi sun tafi ne tare da Yamusa a lokaci yana rike da sarautar madaki. Da suka isa sokoto sai suka wuce zuwa wurin Shehu Usman Inda suka kwana hudu. A ranar da zasu dawo sai Shehu Usman Ya' kebe Mallam Musa yace mashi wannan saduwa namu itace ta karshe saboda haka kada kayi sakaci da alkawarun da muka dauka, kuma Allah ya Sanya ma zuriyar mu Albarka tare da basu ikon rike Jama'a tsakani da Allah. Kuma har duniya ta tashi zuriyar mu da mu kanmu bazamu bace ba a duniya. Dagannan sukayi sallama kowa nace ma kowa Allah shi gafarta Mallam (Albah shi gatara mallam).

A cikin farkon shekarar 1816, Mallam Musa ya sami sako cewa Shehu Usmanu bashi da lafiya daga nan yatashi Galadima Dokaje da Liman Gabdo da Katuka Usman tsoho sabulu don su tafi Sokoto su duba jikin Shehu Usman. Bayan sun tafi sun isar da Shehu Usman yace masu su koma su fada mashi Allah ya kaddara saduwar mu.

Bayan shekara guda a ranar 3 Jumada Akhir 1232 wanda yayi daidai da 20th April 1817 sai sako ya iske Mallam cewa Shehu UsmanIbn Fodio ya rasu, daga nan Mallam Musa ya tafi Sokoto don ta'azziyya tare da mukarrabanshi.

KWARBAI CIBIYAR MALLAWA

Kwarbai itaine sunan Anguwar da zuriya Mallam Musa Sarkin Zazzau suka zauna kuma ne suka kafa Anguwar tare da Abokan zamansu da makwabtansu. Haka kuma duk inda a ka bullo anguwar Gabas da Yamma, Kudu da Arewa sune zaka gani. Kuma wadannan zuriya na Mallam Musa sune zaka gansu da tsaga guda biyu a hagu da dama da kumatansu.

Bayan rasuwar Mallam Musa an Sani matasloli akan shaanin sarautar gidan karfin malam Musa yarasu, ya' nada ya yanshi sarauta biyu maiza uku mata.

Mallam Sidi an nadashi sarauta Dangaladima, Mallam Zakari an noda shi sarautar Magajin Gari, sannan a cikin ma ta aka nada Atu sarautar iya, A'I kuma Mardanni sai inne wadda aka ba sarautar magajiya.

SARKIN ZAZZAU MALAM SIDI ABDUL QADIR

Mallam Sidi Abdul Qadir shine Babban dan Mallam Musa Sarkin Zazzau KUMA YANA DAYA DAGA CIKIN YAYA BIYAR DA AKA FARA BASU SARAUTAR Hakimaci a lokacin da Mahaifinsu Mallam Musa ke Sarkin Zazzau.

Mallam Sidi shine aka fara nadawa Sarautar Dan Galadiman Zazzau a cikin mulkin daular fulani na Zaria ya kuma a rike wannan Sarautar harna tsawon shekara goma sha bakiwai (17 yrs)

Bayan rasuwar mahaifinshi, da yamusa ya hau, sai Dangaladima sidi ya ci gaba da rike wannan sarautar ta Dan galadima har zuwa karshen Yamusa.

Bayan rasuwar Sarkin Zazzau yamusa sai neman sarauta ya taso gadan gadan a tsakanin Sidi Abdul Quadir da Madaki Hamada dan Sarkin Zazzau Yamusa. Kasancewar irin yadda Yamusa ya cire 'ya 'yan Mallam Musa har su hudu daga sarautar Hakimci sai yasa madaki Hamada ya mike da neman sarauta don ya gaji mahanifinshi, ganin haka, sai yasa Limamin Juma'a da Galadima Dokaje suka aika Sakkwato (Sokoto) da shawarar cewa Mallam Abdulkarimu bakatsine shi ya kamata a baiwa Sarautar Zazzau. A wannan zamani Sarkin Musulmi Muhammadu Bello shi ke kan gadon sarautar tare da wazirin Sokoto Gidado, daga nan aka zartar da haka.

Bayan Abdulkarimu ya zama sarki sai zafin kishi ya dadu a tsakanin Sidi Abdul-Qadir da Hamada. Ganin yadda Abdulkarimu ke da sanyi, sai ya kasance bayi da wani karfi a kan mulkin shi Da ganan Abdulkarimu, ya nemi shawara a wurin sakin Kano Dabo wanda yayi sarkin Kano a shekarar 1819 – 1846; Daga nan sukayi shawara da Galadiman, Kano Ango akan cewa Abdulkarimu ya cire Sidi da Hamada akan mulkinsu na Hakimci yanada yan uwansu.

Mallam Abdulkarimu ya karbi wannan shawara ya sauke Sidi a kan matsyin sa na Galadima da Madaki. Saka makon haka ya dauko Abubakar kanin Sidi wanda ke rike da sarautar Iyan Kurama ya bashi Sarautar Madakin Zazzau. Ya kuma dauko kanin Hamada Mamman Sani ya bashi Sarautar Wanban Zazzau.

Ganin yadda Abdulkarimu yayi musu sai Sidi da Hamada sukayi shawarar cewa su hada kan su, su kauda wata kaza mar kishi tsakanin su saboda wannan abu da Abdulkarimu yayi baya yishi ne don gyara sai don ya haifar da gaba, kuma ita a ta auku a tsakanin ko wani gida, da yan uwansu. Ta faru a gidan Mallam Musa tsakanin Sidi da Abubakar haka kuma a gidan Ya'musa tsakanin Hamada da Mamman Sani.

Ananan sai Allah yayi ma Mallam Abdulkarim (Sarkin Zazzau) rasuwa a 1846 inda Hamada ya zama sarkin zazzau.

Hamada bai samu matsala ba kuma yayi kwana Hamsin da biyar ne kurum a kankaraga ya rawu.

Daganan sai wambai Mamman Sani Ya zama sarki, ganin yadda karfin Sidi ya ke sai kowa ya fara jin tsoro, saboda yaya za'' yi ace ga Sidi wanda shine ya kamata ya zama sarki sannan ace Muhammad Sani ne. Nana da nan aka aika Sakkwato akan a San abinda za''yi. Sannan Sarki Musulimin ya turo wazirin Sakkwato Abdul gadri wanda ya gaji wazirin Sakkwato Gidado a shekaran 1849 – 1849. Da ya zo Zariyar ya baiwa Sidi hakuri kuma ya fada mashi nashi na tafe.

Koda wazirnin Sakkwato Abdulqadri yazo sai ya tarradda Mallam sidi ba ya nan ta kama wani dan kauya, Basawa, inda nan ne yatara ba yin shi da kuma dabbobi waziri yace bi zai nada Maman Sani ta har sai ya ga Sidi sun ya magana.

Bayan da yatafi Basawa ya taradda Sidi ya fada Mashi sa kon Sarkin Musulmi sai Sidi ya masa masa tare da Amincewa. Bayan an nada Mamman Sani sai ya circ kanin Sidi Abubakar daga Sarautar Madaki a shekarar 1846, shi kuma sidi ya ci gaba da rike Sarautar Dan galadima. A lokacin, Sidi ya samu tsawon shekera 40 ya na rike da wannan sanuta ta dangaladima da fisheshi a shekare 1800. Daga nan sai akayi ma Mallam Sidi Abdulgadir Sarautar Zazzay.

Bisa Sanin abinda suka fara a baya, sai kawun Mallam Sidi Limamin Zazzau Gabdo wanda yanan daya daga cikin manyan masu zaban Sarki a lokacin, sai akayi shawara da cewa tsakanin Sidi da kaninshi Abubakar wa ya cancanta ya zama Sarki. Daga nan Mallam Sidi ya samu sarautar Zazzau Umurnin Sokoto a shekarar 1860 tare da sakon tabatarwa 1859 – 1874.

Bisa yadda Sidi suka fahimci Juna da Sarki Zazzau Hamada shi yasa Saidi bai circ kowa daga mukamin shiba, sai ma ya kara musu karfi. Inda yabaima Abdullahi dan Hamada Madaki. Saboda ya cika alkawarin da sukiyi da hamada tun Kafin ya zama Sarkin, ya kuma sake baima daya daga cikin ya yan Hamada sarautar da ya bari na Dangaladima. Ya kuma dauki sarautar iya ya bai Aliyu dan Abdulkareem (Sarkin Zazzau) dama kuma, iya Aliyu surukin shine don Sidi na aure da kanwarshi.

Ganin yadda Sidi yake bada sarauta masu garma ga gidajen barebari da katsinawa sai yan Uwanshi da bayin gidan su, suka Hadu bisa Jagorancin wani kanin shi Mallam Muhammadu

Baki suka tafi sakkwato suka shaida ma Sarkin Musulmi cewa zasu yari Sidi sabdoda yana raya gidajan wasu kuma zai kashe na su. Kuma shi Muhammadu baki ya shirya mayak da zasu yaki sidi saboda bai ba kowa wani mukami ba a gidan su sai Aliyu kaninshi daya tura kontagora zuwa har yaka Nufe tar da mayaka da yawa dan su fadeda kasar Zazzau da kuma yi mata garkuwa.
Jin haka sai Sarkin Musulmi ya turo waziri Ibrahim (Wazirin Sakkwato) don yazo ya gyara Al'amarin kuma ya tabbatar da abinda suka kawo hakane, bayan da waziri yazo, ya gane ma idon shi sai ya koma ya fada ma Sarki Musulmi abin da ya gani shi kuma Muhammadu Baki Mallam Sidi, yasa aka kamashi aka rufe shi har tsawn wani lokaci.

Shi Nuhu da aka bash rikon Durum da sauran bayin su da dukiyayinsa, shi Dan Sarki Zazzau Sidi ne.

Bayan wani dan lokaci sai Wazirin Sokoto ya dawo don yaji dalilin da ya sa Sidi ya sa Abubakar (kaninshi) yayi hijira kuma da dalilin tsare daya kaninishi Muhammadu Baki, Sidi ya hana Wazirin Sakkwato (Sokoto) shiga Zaria sai ya tsaya a wani gari a Arewa naso gabas da Zaria, kuma ya aika ma da Waziri ya fada ma sarkin Musulmi wani abune da ya shafi Zaria babu ruwan Sokoto a ciki saboda haka bawani abinda ya dame shi, sarautanc dai na gajeshi saboda haka ya tsame hannn Sakkwato (Sokoto) ga dukkan wani al'amarin da ya shafi Zaria.

Daga nan Wazirin Sakkwato (Sokoto) Ibrahim ya koma ya fada ma Sarkin Musulmi yadda suka yi da sarki Zazzau Sidi daga nan sarkin Musulmi ya tashi masinja da takarda da ya kawo ma sarkin zazzau Sidi da a na neman sa a majalisar mulki ta Sokoto, Mallam Sidi ya kama hanya yana isa aka cc an fitar dashi daga sarautar aka kaishi wurno aka ajiye shi a cikin garin Sokoto.

SARKIN ZAZZAU MALLAM ABUBAKAR

- AN NADA SHI Iyan kurama – Sarauta ce ta yayan sarki lokacin Habe – lokacin Mallam Musa
- Lokacin Abdulkareem aka canza masa sarauta ya koma Madaki har zuwa karshen lokacin mulkin Abdulkareem.
- Lokacin sarki Zazzau Manmman Sani aka cire shi, yaba dan shi Abdu.
- Yayi Kaura zuwa Sokoto da shiga ayarin Muhammadu Baki.
- Lokacin Abdulssalami aka ba Mallam Abubakar sarautar wambai.
- Lokacin sarautan Mallam Musa aka haifi Abdullahi Dan mamman Sani dan sarki Zazzau Yamusa.
- Lokaci Abdullahi an barshi a sarautar wambai. An fidda da Abdullahi daga sarauta saboda kin bin wadan su ummurni daga wurin sarkin musulmi.
- Sannan aka nada wambai Abubakar ya zama sakin Zazzau. Bayan nadashi, yayi wadannan canje canje.

1. Yayi kokari ya hada kan yan uwanshi saboda haka yaba.
   (a) Dan uwanshi Ali Madaki (Kaninshi) Bayan an cire yaro dan Abdullahi.
   (b) Dan madaki Ali Sadauki aka bashi Turaki Karami (Turaki Sadauki)

Aka baiwa Nuhu sarautar Dangaladima hakimin durum

Bayan muturwar Dangaladima Nuhu (Danwajen Sarki Sidi) sai ya nada dan magajin garin Zakari Dangaladima.

Ya nada yaro Muhammadu danshi a matsayin Galadima

MAGAJIN GARIN ZAZZAU ZAKARI 1808 – 1823

An cire shi bayan rasuwar ubanshi tare da yanuwan sa mata kamar

a. Magajiya inne – matar wazirin Sokoto Gidado
b. Iya – Atu – matar limanin jumu'a Gidado wadda bayan rasuwar waizirin Sokoto ta auri Mallam Abdulkareem.
c. Mardanni Ai

Bayan rasuwar magajin gari Bamurna Danshi yayi sarautar Dangaladima, zamanin Sarki Zazzau Abubakar, ya kuma rasu a zammanin Sarkin Zazzau Sambo.

MALLAM ABUBAKAR DARDAZU

Bai riki wata sarauta ba amma yayanshi shi su sun riki sarautar kamar:

(a) Wali Hilliru
(b) Dangaladima Abbas

Jikokin shi akwai

CIROMAN ZAZZAU MUHAMMADU AMINU

Magajin garin Zazzau Nuhu Bamalli

Ya sadauka da rayuwarsa ne kawai akan neman karatu kuma ya rasu a kan hakane, ya kuma shiga karashe da dama yana neman karatu.

MALLAM MUHAMMADU BAKI

Yanemi sarautar lokacin Sidi bai samuta Malam Muhammadu ya rasu bayan mutuwar Sarkin Zazzau Sidi da shekara biyu, a Durum wurin danshi Wombai Nuhu Dan Sarki Zazzau Sidi, kafin a fidda shi a sarauta.

MADAKIN ZAZZAU MALLAM ALIYU 1873-1883

An bashi sojoji yana ta yaki bai dawo ba sai da yayan sa yayi Sarki, wato lokacin Sarkin Zazzau Abubakar.

Bayan dawowarshi sai aka nada shi madaki. Bayan rasuwara yayar sa Abubakar sai a ka ba Abdullahi sarauta.

Wannan yakawo rigima tsakanin su da Sarki Abdullahi saboda tutar yaki da madaki Ali ya daga. Ganin haka sai Sarkin Musulmi Aliyu Babba ya tura wazirin Abdullahi Bayero da yatafi Kano ya samu Sarkin Kano Abdullahi Maje Karofi ya fada mashi ya sa atafi Zaria don neman sulhu tsakanin Abdullahi Sarkin Zazzau da Madaki Ali.

A wannan lokaci Kano tanada yawan Runduna na Mayaka kuma ana shakkanta ta wurin yaki Bayan Wazirin Sakkwato (Sokoto) Abdullahi Bayero ya idar da sakon Sarkin Musulmi sai ya koma Sokoto da ganan Abdullahi maje Karofi, ya umurci Galadiman Kano Ibrahim Bazazzagi da suzo Zaria su sami Madaki Ali suji, menene ya kawo wannan rikichin.

Da issarsu suka sami Madaki Ali suka fada mashi.

> *Yace ina son a gaya ma sarki Musulim har yanzu Sidi yananan don babu yadda za'a ce bada samin mu ba an nada Sarki daga Sakkwato (Sokoto) an kawo Zaria babu zabe ba yardan jama'a ace an kawo shi, ai ko da Mallam Musa yazo Zaria sai da shehu Usamanu ya sa aka nemi yardan jama'a kaji na bakinsu bakawai a turo shi ba.*

Da ganan Galadiman Kano da Madakin Kano suka yanke shawara da cewa lallai idan Abdullahi ya mutu ko ancire shi to Madaki Ali ne zai zama Sarki.

Bada dadewa ya bar sarautar madaki.

A 1881 A ka cire Sarkin Zazzau Abdullahi sannan Sarki Musulmi yace yazo anada Madaki Ali. Aka sameshi ya tsufa sannan bai da lafiya. Sai yace a ba Wombai Zubaru.

> *"Yace na gode amma yanzu wannan takarda tazo a kurarren lokaci sai dai ina bukatan akwai kanina a sashi a cikin wannan matsayi na neman Sarkin wato Mallam Zabairu dan Sarkin Zazzau Musa."*

Madaki Aliyu yarasu a shekarar da sarkin Zazzau Mallam Sambo ya hau gadon sarauta.

WAMBAI ZAAZAU MALLAM ZUBAIRU (1818 – 1883)

Shi Dan Mallam Musa ne.

Bai taba rike sarauta ba har sai da aka bada sunanshi bayan tumbuke sarkin Zazzau Abdullahi, saboda bai taba rike sarauta shi yasa bai sami sarauta sarkin Zazzau be.

Bayan da aka nada sarkin Zazzau Sambo sarkin Musulmi ya umurce shi da ya nada Mallam Zubairu sarauta wambai a shekarar 1881.

Ya samu shekara uku yana rike da sarautar 1881 – 1883 sai ya rasu sai aka nada Nuhu Dan Sarkin Zazzau Mallam Sidi sarautan wambai a shekarar 1883.

Wambai Zubairu ya sadaukar da ranshi ne wajen karatun addini shi yasa tun farko bai nemi sha'awan mulki ba sai da madaki Ali ya kira shi ya bashi shawara.

Ya tafi kasashe da dama don neman ilmin Addini, ya tafi Barno da Kano da Sokoto kuma ya dade a wandannan wurare don karatu kurum.

Bayan da Abubakar ya yi sarauta sai aka mai dashi Dalatu a sakamakon fidda Malam Ahmadu Dallatun Zazzau, daga gidan Bare bari.

Ya rike sarautar har zuwa zamanin Sarki Zazzau Sambo ya rasu a 1882

DANGALADIMA BAMURNA

Dan magajin gari Zazzau Zakari ne Ya rike sarauta tun daga lokacin Sarkin Zazzau Abubakar har zuwa Sambo 1886. Da ya mutu a kaba Mallam Gabdo.

WAMBAN ZAZZAU MALLAM NUHU 1881 – 1886

Shine Babban Dan Sidi Abdul Qadir, bai rike sarauta ba sai lokacin sarki Abubakar.

Lokacin Abdulsalami aka cire shi daga ma sayin sarauta Durum har lokacin Abubakar da akayi masa sarautar Dangaladima kuma hakimin Durum. Bayan mutuwar sa (Abubakar) yaci gaba da rike mukamin har wani lokacin sai Abdullahi ya dakatar da shi.

Sambo wanda yake rike da Wambai shi yayi sarki sai aka ba Zubairu. Bayan mutuwar Zubairu sai aka ba Nuhu a shekarar 1884.

Yayi yaki da sojojin Ningi anan ne yayi shahada, ya nuna jaruntaka wadda a har gobe akan misali da shi. A lokacin da aka ce ga mayakan sarkin Ningi nan sunzo zasu yaki Zariya sai wasu daga cikin yayan sarkin sukace a yaki Sarkin Zazzau Sambo. Saboda idan ya mutu sai Wambai ya gajeshi. Da aka gaya ma Wambai cewar haka sai yace *"Ni bazan yaki Ningi saboda Sambo bane, ni bukata na shine in karya Alikadarin nan na Galadima Salmanu. Saboda yana neman ya gurbatar mana da gidajen mu gaba daya. Saboda haka nayi shahada, ko na mutu Allah ba zai biya masa bukatarsa ba.*

Dama tun lokacin da Wambai Zubairu ya rasu aka baima Wambai Nuhu wannan matsayi, sai Galadima Salmanu yakai ya komo saboda yana ganin karfin shi zai ragu, tunda a lokacin sai abin da ya zartaddashi za'a yi, kuma akwai Mukamai na sarauta wanda duk ya hada aikin su. Saboda haka Wambai bazai tankwasu ba saboda bashi da tsoro kuma ya kasaita kwarai da gaske.

Bayan shirin da Galadima Salmanu yayi nacewa idan sarki zai tafi ziyara Sakkwato (Sokoto) kamar yadda aka saba sai a far mashi a kasheshi, shi kuma Galadima dama shine mai rikon gari, idan sarkin baya nan, da Sarkin Zazzau Sambo ya fito sai Galadima ya aika a fada ma sojojin yaki cewa ga sarkin nan zuwa kuma ga ta inda zai bi da isar su Wambai ya fara yaki, Sambo ya wuce anan aka kashe Wambai Nuhu a Kofar Garin Tukur – Tukur.

WAMBAN ZAZZAU MALLAM YARO MUHAMMADU 1874 – 1888.

Mallam Yaro Muhammadu dan Sarkin Zazzau Abubakar ya samu sarautar Galadima a lokacin da Mahaifinsa (Sarkin Zazzau Abubakar) ke kan gadon sarauta a shekarar 1874. Bayan mutuwar Abubakar sai Abdullahi yayi sarki don yataba yi aka fiddashi a shekarar 1873. Da ganan sai ya fidda Galadima Yaro Muhammadu daga sarautar Galadima.

Bayan shekara kadan aka fidda Abdullahi daga sarki a shekarar 1881, aka nada Sambo yayi sarki a wannan shekeran, a lokacin wambai Nuhu ke rike da sarauta Wambai . bayan rasuwarshi sai sarkin Zazzau Mallam Yaro Muhammed sarautar Wambai a shekarar 1886. Bai dade ba akan wannan sarauta sai ya rasu, daga nan Mallam Sa'adu ya gajeshi ya zama Wamban Zazzau.

> "Wambai Mallam Yaro Muhammadu yayi biyayya kwarai ga iyayenshi saboda a lokacin mahaifinsa saboda biyayyansa, shine ke kula da gonakinsu da kuma sauran kaddarori. Ba'a taba samun shi da wani laifi ba ya kuma kasance tare da Wambai Zubairu har na tsawon wani lokacin kusan ma ana ganin anan yasamu karin tarbiyya masu kyau, ya rasu a zamanin sarkin Zazzau Sambo a cikin Shekarar 1888, ya kasace tsakaninshi da sambo kafin a fiddashi shekarar daya da watanni, karfin yabar duniya ya fadama Sambo yayi hankali har yanzu yanada magabta."

WAMBAN ZAZZAU MALLAM SA'ADU

Mallam Sa'adu dan Wamban Zazzau Mallam Nuhu ne, ya samu sarauta dan Galadima a lokacin da aka bai ma mallam Yero Muhammadu Sarautar Wambai bayan rasuwar Mahaifinsa, a lokacin sarkin Zazzau Sambo.

Yana rike da wannan matsayi sai Allah yayi ma Wambai Yero rasuwa, sai Dan Galadima Sa'adu ya hau wannan matsayi. Bayan lokakin da Sambo ya sauka a shekarar 1890 sai aka sanya sunan Wambai Sa'adu cikin masu neman sarki.

A wannan lokaci ansa mutum uku daga ko wani gidan sarauta, na farko an sa sunan su Madaki Lawal Dan sarkin Zazzau Sambo, yero Dan Sarkin Zazzau Abdullahi da kuma Wambai Sa'adu Dan wambai Nuhu (da sarkin Zazzau Sidi). Bayan zabe sai yero yazama sarkin Zazzau a shekarar 1890-1897.

Mallam Sa'adu Wamban ya rasu a zamanin sarkin Zazzau Mallam Ja'afaru a cikin shekrar 1938. Inda a sakomakon haka ne bayan fitar sarki yero aka sa sunan Muhammadu Dan Sidi a cikin masu neman sarautan Zazzau a wannan lokaci cikin shekarar 1897.

Wamban Zazzau bai yi sarauta ba saboda ubansa bai taba zama sarkin ba.

MUHAMMADU DAN SIDI

Bai taba sarauta ba. Bai fitowa sai lokacin da cire yero. Saboda yana ciwo kuma ga tsufa, ga larura na rashin ji da na rashin gani. Masu neman sarauta da shi sune kwasau Dan sarkin Zazzau yero da kuma Madaki Lawal Dan Sarki Sambo. Galadima Salmanu na son Muhammadu saboda ya sami galaba.

Kwasau ya shirya mayaka da su yaki Galadima da Wazirin Sakkwato (Sokoto) Muhammadu Buhari, Idan akaba Muhammadu Dansidi sarauta.

Wambai sa'adu yaba Muhammadu shawara ya amsa da cewar baya son sarauta.

Kwasau ya aika ma sarkin Kano Ali yabashi mataimaka dari biyu a lokacin mallawa da barebari kowa na goyon bayar Kwassau.

Akai zabe Kwasau ya cinye zaben ya zama sarki.

APPENDIX 4

BANZAZZAU

Alhaji Sambo Yahaya Age 50 years 15th Dec.1997

Banzazzau ya dauko Asaline daga kofar bai. Wato kofar bayan gidan Sarki. Ita wannan kofa tana nan tun zamanin da akayi ganuwa ta farko.

Samuwar Jama'a a wajen ta farane zamanin Sarkin Zazzau Muhammadu Sani. Shi ya zauna acan Ban zazzau ne lokacin da ya zama Sarkin Bai zauna a fadaba. Daganan zuriyar Mai yaki sukazo suka zauna tare da Sarkin Zazzau Muhammadu Sani. Ya zauna ne a matsayin mai amsa sakon Sarkin Zazzau Mohammadu Sani zuwa Dakace, Dembo, maigana da soba. Mai yaki yana da yaya guda uku, Shehu, Sama'ilu da Musa. Shi kuma Shehu yana da yaya mata guda hudu Zainabu tayi aure a Banzazzau Akwasi tsofafaffin Gidaje a unguwar kamar su. Gidan Sambo, Gidan Dudu, Gidan Magayaki, Gidan Mai unguwa, Gidan mai jan kwari Gidan Ummaru, Gidan Dan Daudu mai raken kan Dutse, Gidan Garba, Gidan Mazidu, Gidan su tanimu, Gidan su Ummaru, Gidan Makama Gidan su Dogari, Gidan su Kwassau.

Sanaan Mutanen Unguwar shine yin kwalekwale, su, Rini, da Dinki, Akwai Rijiyar Rini wasen guda shdda a unguwar.

GIDAN LIMANIN BANZAZZAU

Alhaji Jibrin Ahmed Age 62, 17/12/1997.

Asalin wanda ya kafa gidan shine Mallam Dauda Madugun Adamawa. Kuma shi ya fito ne daga kukawa ne cikin kasar borno. Da isowarsa Zaria yaje gidan Sarki ya nemi Masauki aka kaishi fadamar bono/fadamar Sarkin. Yace nan baiyi masa ba, domin babu ruwa da abincin da dabbobinsa zasu rika ci daganan sai aka kawoshi gabas da gari gaban Dutsen madarkaci nau ne ya samiduk abin da yake nema kuma yace yayi masa dalilin zamansa kenan a wannan Anguwa wato Ban Zazzau.

Tarihi ya nuna cewa Mallam Dauda yazo tare da Mallam Sidi wanda shi buzu ne. tare suka zauna a banzazzau kuma har yanzu, gidan sa na nan a anguwar cike da Zuriyarsa kuma ana kiran gidan gidan mal. Sidi. Lokacin da sukazo sun taros da wasu gidaje kasan a anguwan kamar haka:

Godam Barwa 2. Gidan Mazadu Gwari.

Shine Sarkin Magina kuma har yanzun kufan gininsa yana nan a kofar bai har za yanzu bai fada kuma yana da wani zare wanda idan zai hau garu yaci gaba da gini, ya kan fito dashi daga Aljihunsa ya Jefa Inda yakan kama ya rika takawa yana hawa kamar tsani 3. wasu sunce shi bafillatani ne wasu sunce Balarabe ne zuriyarasa. Suna nan da yawa a nan kasar Zazzau, Daga nan sai gidan tsohon Liman sai kuma gidan Maude Goguwa.

Ainihin Limamin BanZazzau ya rasu wanda gidan sa yu zama kufuyi ayanzu. A sai Mallam Tanko yazama liman wanda sane wurin Mallam Dauda kaji masabbabin dawowar Limanci nan gidan har yanzu. Mallam dauda na da ya ya kamar haka,
Mallam Tanko 2. Mallam Muhammadu da mallam Ahmadu.

Baza aiya sanin ko lokacin wani sarki ne Mallam Dauda yazo Zaria ba. Amma ana kyautata ziton yazo ne lokacin sarkin Zazzau kassau.

RIJIYAR KWAKWARANDO

An wayi gurine an ganta, amma ance ainihinta rijiyar wankin rinin ne na Mallam Dauda Madugun Adamawa, idan a kawo rini anan ake wankewa sai a baza a filin bakin rijiyar. Daga soya ta zama rijiyar ruwan sha kuma mutane daga anguwayi da yawa kanzo sibar dibar ruwa a nan. Kuma idan ta kone a cikin tsakiyar kaka ke nau sai a koma rijiyar buta.

AN MAI ANGUWA 18/12/97 SHEKARU 54

Alhaji Salisu Ibrahim

Wannan gida yana wannan anguwa tun wajen Jihadin Shehu Usman Dan Fodio. Ainihin mai gidan shine Mallam Auta sai yan uwansa. Kuma shi Mallam Auta yana da yaya biyu, 1. Mallam Ummaru, 2. Mallam Haruna.

Mallam Yahaya daya daga cikin zuriyar Mallam Auta, shi Mallam Auta yafito ne daga kasar kano daga Dutse gadawur cikin Jihar Jigawa. Kuma kafin ya zauna a Zaria yakan zone harkan kasuwanci ya koma. Daga baya ne yazo da iyalansa baki daya. Shi dai Mallam Auta yana da yaro biyu, Mallam Ummaru da Mallam Haruna.

MALLAM UMMARU YAYANSA

(1) Alu Ibrahim Ummar (2) Amina (3) Rahmatu da (4) Hadiza. Alhaji Ibrahim shie mahaifin mai anguwa na yanzu; da Alhaji Salisu da mai anguwa. Wanda ya rasu sauran yayansa sune Alhaji da Abdulmumin Ibrahim da Abu. Matan sunyi aure a unguwan.

GIDAN MALLAM UMMARU/AUDU NAMAIRO

Mallam Garba Shekaru 56 years 16/12/97

Mallam Mohammadu Kano shine mai gidan, shi kuma yana cikin Zuriyar Mallam Nasar wanda akace kusan shi ne yu fara zuwa Banzazzau. Wasu sunce shi Nasar Balarabe ne, wasu kuma sunce shi Bafillatani ne domin kuwa hurshen da akaji yana magana dashi shine fillanci kuma wannan mutum shahararrene, domin zuriyar sa suna da yawa.

Shi Muhammadu Kano ya zauna a unguwar Filani kusa da a Gyallesu wurin da aka gina makarantan W.T.C. kuma har yazuwa samun yanci kai 1960, filin na hannun zuriyarsa ne, daga bayane da gwamuati taso ta gina wannanu makaranta sai aka karba a hannausu.

Daga bayane yu dawo cikin gari wato BanZazzau ya fara zama kusa da gidan mai unguwa, daga baya yu dawo inda zuriyarsa suka zauna a yanzu shidai Muhammadu Kano jarumin gaskene wanda yazo Zaria Zamanin sarkin zazzau sani, kuma yana da yaya biyar. Mallam Garba - Adamu, Asma'u Abdul su mairo.

APPENDIX 6

ALBARKAWA

ALIYU SALIHU, AGE 73

Zuriyarsu sune wadanda Fulani suka karbi mulki a wajensu. Shi unguwar Albarkawa ya dauko suna ne daga dan Sarki Habe wanda akace masa Albarka. Shi Albarka shine karamin dan sarkin zazzau Muhammadu Makau. Lokacin da za'ayi Jihadi Sarki Zazzau na Habe Bayanan Da yaji labarin turo Mallam Musa da Yamusa, da tutan Jihadi sai ya turo Madakin sa kuma dansa don kare garin, madaki ya tsaya a kofan Tukur-Kukur. Sai shi kuma ya biyo ta kofar bai, ta haka akaci Zaria da yaki. Danganan sai suka tashi suka koma Abuja.

Akwai wani gida a kusa da kofan Jatau, nan gidan shine Babban gidan yayan sarkin Albarka shine karamin da a wannan gidan, shi bai tafi Abuja ba sai ya zauna a gidan bayananci garin da yaki sai ya rufe kofar gidan. Da Fulani sukacigari, Sarkin Zazzau Mallam Musa yace duk Habe da yarufe kofa a bashi yayi zaman Amana. Albarka ya zauna awannan gidan har lokacin Sarkin Zazzau Yamusa. To in kaka yayi Albarka ya kantafi waje yan uwansa, saboda gudun makirci, sai sarkin zazzau yamusa daga kofan jatau yace yazo yazauna yataso shi kusa da fada. Albarka yana da yaya guda biyar, na farko shine Abubakar Atika shi ya haifi danshi ana cemasa Aliyu (balarabe), shi Aliyu shi ya haifi yaya gudar biyu, daya ance masa Adamu dogo daya anace masa Mallam Abubakar ko maude Gajere. Shi Adamu dogo ya haifi dansa anace masa Sule. Sule bai samu haihuwa ba. Shi Abubakar ya haifi dansa ana cemasa Salihu da mace guda daya ana cemata khadizatu. Shi Salihu shi ya haifi Aliyu (Maibade Tarihi). A yanzu haka ya na yara guda goma sha biyar masu rai.

Sauran yayan Albarka sune suka gina gidaje a unguwar, kamar gidan Mallam Haruna, shi Jikane ga Albarka. Akwai gidan Bani Gidan Bani, dagidan yusufu mai kwake, sarkin Fada, sai gidan Habu. Kusa Gida na na biyar shine gidan su Ahmadu Sarkin Fada cindo.

Dan gantakar Albarka da Ibrahim tsoho. Shi Mallam tsoho kanin matan Albarka ne, shi Albarka yana da yara wadanda yasa a makaranta. To shi Malamin yaran Albarka ya cika bugu Ganin haka sai matan Albarka tace ya kamata ta aika a kira kaninta yazo ya koyar. Shine aka aika wa Mallam Ibrahim tsoho. A lokacin Mallam Tsoho yana kajuru. Yazo yaci gaba gaba da koyar da yara karatu har lokacin Auren sa yatabo, sai shi Albarka yanemin Masa auren yar liman. Gaboo, sai ranar buki akace baza a bashi. Albarka sai ya fito da kuyangar sa yace ma Ibrahim tsoho ya nemi daya daga cikinsau, daga cikinsu yayi aure.

Muhammadu Bello Gidan Sarkin Ladanai 70 years

Shi wanda ya soma zuma garin nan sunansa Isau. Shi kuma Abubakar ya zama kamar Waliyyi ne a waccan zamaninsa. Saboda lokacin da yake da rai, idan za'a yi amacca dashi akeyi sannan ayi la'asar dashi a Zaria. Hasali ma lokacin da Za'a gina masalachin Jumua na Zaria Zamanin Sarkin Zazzau Abdulkareem shine yanuna Alkiblar Massalacin. Bayan da aka gina massalachin

shine ya zama ladanin Masalachin. Idan yadawo daga massalachi bai da wani aiki sai koyarwa. Akwai lokacin da yatafi aikin Macca, ya dade yai wajen shekara bakwai. To a wannan dawowa ne yazo da mauludi, da ake yi watan Rabiul Awwal a Zaria.

Bayan rasuwar Mallam Abubakar Ladan, sai kuma Mallam yaro yagajeshi. Daga Mallam Yaro sai Mallam Balarabe wanda aka nadashi Sarki Zazzau Ja'afaru ya nadashi Naibi mai yin sallar Azuhur, La'asar da Maghriba. Bayan sa sai aka nada Mallam Mani (Usman)kanin Mallam Balarabe, ya zama Sarki Ladanai.

Bayan Usman Mani sai kaninshi Mallam Alu. Bayan sa sai Alhaji Mallam Umman ya shekara hudu, Bayan Rasuwar Mallam Ummaru sai aka nada Muhammadu Bello wanda yanzu shine sarkin ladanai, yana kuma da shekara shidda awannan matsayi.

Shi Mallam Isau ance Asalinsu mutanen Kano ne.

246

No 15K\FADA
ZARIA CITY KDS.
SIGN
DATE

Kakaki

Zuriyar

M. Ibrahim Tsoho

Na

Dogara Bashir Dalhat

GODIYA

Godiya ta tabbata ga Allah madaukakin Sarki da ya bani ikon hada wannan littafi da nufin karfafa dankon zumunci da aka sanmu, mu mutanen Kakaki, da shi.

	M. Abdul'ahadi	0^{0}	0^{0}	0^{0}	0^{0}	0^{0}	0^{0}	0^{0}	0^{0}	0^{0}
	M. Abdurrashid	7^{0}	5^{0}	5^{0}	3^{0}	0^{0}	0^{0}	0^{0}	0^{0}	20^{0}
$3^{3}+2^{2}$ 5^{5}	$25^{25}+13^{12}$ 38^{37} (1)	$98^{22}+89^{21}$ 187^{13} 114		369 + 292 661^{27} 634		251 + 265 516^{2} 514		$4^{0}+5^{0}$ 9^{9} 9		1416^{144} 1272

TARIHIN GALADIMA AHMADU DA DANSA UMARU WALI



NA

ABDULKADIR BELLO.

SADAUKARWA

INA FARAWA DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI.

Wannan littafi na sadaukar da shi don tunawa da marigayi Sarkin Katsinan Hausa Muhammadu Dollo da Kwamanda Marigayi Sarkin Fulani Katsina Malam Dandubu da Marigayi Malam Ahmadu Yero da marigayi Malam Umaru Barmado (Diyan) da marigayi Malam Abubakar da marigayi Mal. Mijinyawa (Kauran) da marigayi Malam Dauda Gidado (Galadiman Gaya) da Allah ya yi masu rahama cikin littafin Aljanna a watan Agusta, 1993 a dalilai dakacin da nake bisa ra'ayin wannan littafi, wanda kuma ya taimaka mani wajen yin bayani mai ma'ana a kan labarin Galadiman Katsina Malam Ahmadu da 'ya'yansa. Allah shi gafarta masu, shi kuma nawawa Kabarinsu shi ya sa Aljanna makomarsu da mu baki daya, amin.

ASALIN GALADIMA AHMADU

Shi dai wannan bawan Allah, watau marigayi Galadiman Zazzau Malam Ahmadu an haife shi a kasar Barno ne kuma shi kansa ya haifi wasu daga cikin 'ya'yan da ya haifa a kasar Barnon ne a wani gari da ake kira Misau. A cikin 'ya'yan da ya haifa a Misau din akwai Dikko da Muhammadu Modibbo da Shehu Usman Uda da Umaru (Wali) da sauransu. A nan za a ga cewa, iyayen Galadima Ahmadu da kakanninsa duk sun fito daga kasar Barno ne. Saboda haka rayuwar Galadima Ahmadu tayi tasiri kwarai da Barnon. Don haka ne muka ga ya kamata mu dan gutsuro kadan daga cikin tarihin Daular Barno, kafin mu fara gabatar da tarihin Galadiman Zazzau Malam Ahmadu.

TAKAITACCEN TARIHIN BARNO

Barno na daya daga cikin manyan dadaddun dauloli a duniya. Abin da ake kiran wadannan mutane da suka kafa wannan daula ta Barno shine **SEFAWA.** Sai da sefawa suka shekara dubu daya cif suna mulki babu yankewa har zuwa shekara ta 1846 (*miladiyya*). Wannan sarauta ta sefawa tana da tasiri kwarai da kasashen larabawa da addinin musulunci, don shi ne addinin da yayi tasiri akan mutanen, dafili kenan ma da masana tarihi suka ce, tsarin sarautar Barno tun a wancan lokaci a iya gwada shi da kowane irin tsarin sarauta mai ma'ana a duniya. Masana tarihin sun nuna cewar addini ya zo Barno ne a tsakanin karni na goma zuwa na goma sha daya na *miladiyya.* Kafin karni na goma sha tara Barno na daya daga cikin fadadan dauloli na

duniya. Tsawon daular Barno ya kama ne tun daga MURZUK a can cikin Hamada har ya zo Kano. Ta barayin Arewa kuma tun daga Agadas har ya hada da wajen gabar da kogin Biniwai. An sami kabilu daga kasashe daban-daban wadanda suka zauna a kasar Barno kuma suka kasance kamar 'yan asalin wannan wurin.

TAKAITACCEN TARIHIN SEFAWA

Wanda ya kafa wannan daular ta SEFAWA wani Yarima ne da ake kira Seif bin yazin, ya fito ne daga yemen. Babu bakikanin shekaran da suka zo, amma babu shakka masana tarihi sun yi ittifaki a kan cewa, kafin karni na goma sarauta ta fara kafuwa a Barno. Sefawa sun kafa wurin ne daga gabas da inda ake kira tafkin cadi a yanzu. A wajen karni na goma sha biyu zuwa na goma sha hudu sarauta ta kafu kwarai a Barno, a wannan lokacin ne ma sarakunan Barno suka fara zuwa Makka ko wacce shekara, kuma suka fara gine-gine Madarasa (makarantu) a can kasar Masar, don karatu a mazhabar Malikiyya, kuma da gina masaukin baki don masu zuwa ziyara Masar daga kasar Barno. A wanan lokaci ne sarakunan Barno suka fara yake-yake wanda ya jawo fadada kasa, shi ne dalilin da ya sa Barnon ta zama daya daga cikin manyan daulolin duniya ta fuskar fadin kasa. Abin daya kara taimakon Barno ta fuskar fadin kasar shi ne, a wajen tafkin Cadi lokacin da Sefawa suka zo, kasar na da albarka kwarai da gaske, kuma tafiya ba wuya don tafkin Cadi babban ruwa ne a wannan nahiya, kuma fili ne babu sagagin itatuwa. A wannan lokaci kuma tafiya da dawaki a Barno na da sauki kwarai. Wannan shine ma

dalilin da ya sa dawaki suka taimaka kwarai ta fuskar yake-yaken da Barno ta yi. Sannan kamar yadda muka tsakura daga baya, akwai tasiri na addinin musulunci a kan mutanen Barno, saboda wannan dalilin ne irin sarautar da sefawa suka kafa musulunci ya riga ya tsara shi tuni. Yadda wannan tsari yake kuwa shine: Sarki shine shugaba to banda Sarki akwai wazirai akwai su Talib akwai masu Baitil Mali da sauransu. Haka abin ya dinga tafiya, kasar Barno na ta kara fadada. Kafin karni na goma sha hudu kasar Barno ta kai Turgan kusa da Libya, har ta kawo Kano da wasu wurare. Kafin karni na goma sha biyar manya-manyan sarakunan Barno suka fara tasowa, kamar su Mai Idris katakarmabe da su Mai Idris Aloma.

Barno ta kafa hurdar jakadanci da kasashen duniya da dama, ta kuma aika da jakadu zuwa wajen Maroko (Morocco) da Tunisiya da Libya har zuwa Istambul, ta ci gaba da gina makarantu da sauransu. Mutane sun yi ta shiga kasar Barno daga kasashen larabawa da sauran kasa shen Musulmi don yada addinin Musulunci, suna kuma koyarwa, kuma ana koyar da su. Haka kabilar Fulani ma sun shiga Barno ne tsakanin wannan karni na goma sha biyar zuwa sha shida na (Miladiyya).

To amma, kafin farkon karni na goma sha tara. Barno ta shiga wasu matsaloli da dama, kuma makasudin wadannan matsaloli shine siyasa, tashin hankali yayi yawa, kowane Yarima yana son ya zama

Sarki watau "Mai" a harshen kanuri, saboda haka wannan matsala tare da wasu suka jawo tabarbarewar arzikin Barno kwarai da gaske. To a daidai wannan lokaci mutanen Barno na da kishin Ilmi sai karatu ake ta yi tare da wa'azin addinin Musulunci,watau karantarwa ya fadada.

To ana cikin wannan hali na karatu da wa'azi a kasar Barno, sai wani aikin alhairi ya bullo ta wajen yamma, shine bullowar Shehu Usman dan Fodiyo. Karatu da karantarwa suka kara bunkasa har zuwa farkon karni na goma sha tara (1804) da aka fara Jihadin Shehu Usman dan Fodiyo. To a wannan lokaci, fulanin da ke tsakanin Barno da kasar Hausa sun taimaka kwarai ta fuskar wannan Jihadi har suka kaima daular Barno hari har sau Uku. A irin wadannan hare-hare da aka kaiwa Barno ne har "Mai" na sefawa ya gudu yaje ya buya aka ci shelkwatar Barno watau Gazargamu. Daga baya "Mai" na sefawa ya dawo, sai aka sake kai hari ya sake gudu, daga nan ne sai ya gayyaci wani malami da ake kira Muhammad al-Amin al-Kanemi (wani kanenbu ne) anda yaje yayi karatu a kasashen duniya daban-daban har zuwa Masar, da ya dawo ya zauna a inda ake kira Gala, anan ne yayi ta karantarwa.

Shi El-kanemi, malami ne babba har akwai littattafan tarihi da suka yi maganar makabila tsakaninsa da su Shehu Usmanu da Sarkin Musulmi Muhammadu Bello; kan cewar Barno kasar Musulmi ne bai kamata akai musu jihadi ba. Shi kuma Shehu da Sultan Muhammadu

Bello suka ce tunda Barno suna hadawa da ayyukan da suka saba wa addinin Musulunci kuma suna kauce ka'idar da addinin Musulunci ya shimfida ai ya kamata a kai musu jihadi. An sha makabala sosai, da dauki ba dadi a tsakaninsu. Muhammadu El-kanemi na nan na kokarin ganin cewar sarkin sefawa ya tabbata a mulkinsa haka dai abin ya dunga tafiya, a hankali a hankali har Sarkin sefawa ya zama bashi da wani karfi, Mal. Muhammad al-amin al-kanemi ya fi shi karfi saboda dimbim mabiya tun daga wajen shekara ta 1821. Sannu a hankali mutanen al-kanemi suna ta kara karfi har suka kori sefawa suka maye gurbinsu a cikin karni na goma sha tara, a 1846. Tunda wannan daula ta al-kanem ta kafu, ita ce ke tafiya har zuwa yanzu.

A lokacin da aka yi jihadin shehu Usman Fulanin Barno sun taimaka wa jihadi shehun, dangane da haka ne masana tarihi suka kasu biyu. Wasu na ganin saboda kabilanci ne suka taimaka ma shehun mafi rinjaye kuma sun nuna cewar, saboda fulanin masan ne dangane da shri'ar musulunci, sun san abin da yake daidai da wanda ya kauce wa shari'a.

Koda yake akwai wahalhalu da Fulanin suka sha a karkashin mulkin Sefawa, to amma ba Fulanin ne kawai suka sha wannan wahala ba. sai dai ko wata kila don kansu ya fi wayewa. Fulanin sun wadatu da ilmin addini sun gane cewar Musulunci ba ya son zalunci da sauransu, shi ne ya sa suka tasar ma mutanen Sefawa.

Babu shakka, Fulani suna da yawa a Barno kuma suna zaune a Barno sama da shekara dari Uku (300) kafin jihadin Shehu Usman dan Fodiyo. Amma dai mafi rinjayen jama'a a Barno su ne Kanuri. Koda yake Kanuri din nan mutane ne iri-iri da suka zo daga tafkin Cadi suka taru suka zama Kanuri. Sannan akwai kabilu kamar su Kanembu da Margi akwai su Mandara ga Gamargu da Shuwa. Akwai kuma Kotoko da Bura da Babur da sauransu da dama. An kiyasta kabilu ba za su kasa hamsin a kasar Barno ba, wanda yake yanzu yana da wuya ka tsaya ka tsefe tsakanin wannan da wancan don sun dade suna auratayya a tsakaninsu, wanda yin hakan ya dada jawo hadin kai da karin kullin zumunci tare da zama abu daya, watau Barebari.

TAKAITACCEN TARIHIN MALAM MUHAMMADU FATE KAKAN GALADIMA AHMADU

A irin wannan hali na zaman zamanta kewa da ci gaba da Barno ta kasance a ciki tun shekaru daruruwa, Allah ya yi isowar kakannin Mal. Muhammadu Fate, wanda ba ma iya fayyace shekara ko karnin da suka zo, sai dai a bisa mafi kyawun zato sun zo ne a karni na goma sha biyar zuwa sha shida.

Ga dai-yadda nasabar Galadima Ahmadu take da Malam Muhammadu Fate; shi dai Galadima Ahmadu dan Umar dan Abubakar dan Muhammadu Fate. A yadda tarihi ya nuna, shi malam Muhammadu Fate kakanninsa sun fito ne daga kasar Larabawa a wani gari da ake kira Iraki. An sami wani juyin zamani wanda yake mutanen kasar Iraki sun ta fita daga kasar kungiya-kungiya don yada addinin Musulunci, ko don wasu fitinu a lokuta daban-daban. A cikin irin wannan juyi ne aka sami wani ayari wanda ya nufo kasar Afirka ta yamma, a karkashin shugabancin mutane daban-daban, har jagorancin wannan ayari ya zo kan Malam Muhammadu Fate.

Wannan ayari da Malam Muhammadu Fate ya shugabanta, ya bi ta kasashe daban-daban har Allah madaukakin Sarki ya kawo shi daular Barno a wajen karni na sha shida, a lokacin daular Sefawa. Inda wannan ayari ya soma zama ya dan jima a cikin daular Barno, shi ne wani gari da a lokacin ake kira Laraba-Gaidam, a wannan lokaci garin wani bawan Sarkin Barno ne, da ake kira Kakemi. To a wannan zamanin an ce mutanen garin ba su son baki, saboda haka wannan kungiya ta su Muhammadu Fate ta sami mishkiloli da dama. Ana nan akan haka ne har Allah ya yi tashinsu zuwa wani gari da ake kira Kukawa, Ganin Mal. Muhammadu Fate masani ne a fannin shari'ar Musulunci, sai mutanen garin suka ga ya kamata a rike shi don ya zama Alkali a wannan gari na Kukawa.

Malam Muhammadu Fate; na Alkalin Kukawan ne, Allah ya kawo karshen rayuwarsa a duniya. Ya rasu ya bar 'ya'ya da jikoki. A cikin 'ya'yansa akwai Malam Ibrahim Ardo da Malam Abubakar wanda shi ma ya kasance yana daga cikin litattun mutane da suka wadatu

da ilmi a zamaninsa. Su Malam Abubakar na zaune a garin Kukawa har kuma suka kara yaduwa a saukan garuruwan kasar Barno, wasu suka nufi Gujba wasu Funne wasu suka nufi kasar Misau d.s. A cikin wadanda suka je Misau akwai dan Malam Abubakar wanda ake kira Malam Umaru, shi ma ma'abucin ilmi ne kabilarsu ne ake kira Fulanin Misau, wasu kuma kan ce Filata Barno.

Su Malam Umaru na zaune a kasar Barno ne, sai suka sami labarin fullar Jihadin Shehu Usman dan Fodiyo a kasar Sakkwato. Suka je suka yi mubaya'a tare da nuna goyon baya da taimaka wa Fulani jihadi, karkashin jagorancin Gwani Muhtari. Bayan an kare jihadin, sai su Malam Umaru suka sake komawa Kukawa daga nan kuma sai Misau.

ZUWAN MALAM AHMADU DAN UMARU ZAZZAU NA FARKO.

A lokacin da Malam Umaru ke Misau din ne, aka ce, diyar Wamban Zazzau Malam Muhammadu Sani dan Yamusa (wanda ya zama sarkin Zazzau daga bayal da ake kira Yadammo, ta sami ciwo irin na tabin hankali, aka yi ta nema mata magani amma ba a dace ba. A cikin wannan hali na neman magani ne aka ba shi Wambai Muhammadu Sani shawarar, da ya aike wajen dangin mahaifiyar yariyar da labarin halin da yariyar ke ciki. Wambai Malam Muhammadu Sani din kuwa ya aika da labarin Misau wajen su Malam Umaru a cikin kimanin shekara ta 1841. A wannan lokaci Malam Umaru yana da zurfin shekaru kwarai, saboda haka, sai ya aiki dansa mai suna Malam Ahmadu don ya yi ma Yadammo magani, ko Allah Ya sa a dace.

Lokacin da Malam Ahmadu ya isa kasar Zazzau a cikin wannan shekara ta 1841-1842 ya yi kokarin saduwa da mara lafiya. Wambai

Malam Muhammadu Sani ya yi maraba da shi, ya kuma yi masa bayanin yanayin ciwon da ke damun yariyar, sannan ya yi masa jagora zuwa ga mara lafiyar, Malam Ahmadu ya dafa kanta ya yi mata addu'a ya kuma ba ta magunguna kamar yadda tsohonsa (Malam Umaru) ya umurce shi. Ba a dade sosai ba sai Allah ya ba ta lafiya. Daga wannan lokaci Wambai Malam Muhammadu Sani ya bukaci Malam Ahmadu da ya tsaya ko da na shekara guda ne don ya yi karatu a wajensa a wasu fannonin addinin musulunci da na lugga da sauransu, sannan ya taya Wambai adu'a akan al'amuran da ya sa a gaba. Har sun fara karatun' zuwa wani lokaci, sai labarin rasuwar Sarkin Musulmi Abubakar Atiku dan Shehu Usmanu ya zo musu da kuma nadin sarkin Musulmi Aliyu Babba dan Sarkin Musulmi Muhammadu Bello. Sai Malam Ahmadu ya sanar da Wambai Malam Sani cewar, yana son ya wuce Sakkwato don ya yi ta'aziyyar Sarkin Musulmi Malam Abubakar Atiku kuma ya yi mubaya'a wajen Sarkin Musulmi Malam Aliyu Babba. Daga nan kuma zai koma Misau, don ya sanar da mahaifinsa cewar Yadammo ta warke.

DAWOWAR MALAM AHMADU DAN UMARU ZAZZAU.

Malam Ahmadu, ya tafi Sakkwato kamar yadda ya daura aniya daga Zazzau. Bayan yin ta'aziyya da Mubaya'a da ya yi a Sakkwato sai ya koma Misau, to ya koma Misau din ba dadewa sai Allah Ya yi ma mahaifinsa Malam Umaru rasuwa, a tsakanin shekara ta 1842 zuwa 1843 (Miladiyya). Da labarin rasuwar Malam Umaru ya isa fasar Zazzau, sai Wambai Malam Muhammadu Sani ya aike wa Malam Ahmadu

da sakon ta'aziyya da kuma son ya dawo Zariya. Malam Ahmadu ya amince ya komo kasar Zazzau ya taras da Wambai Malam Muhammadu Sani a garin Taba suka ci gaba da karatu tare da rokon Allah kan bukatarsa. Allah Ya karbi adduarsu suka kara wadatuwa da ilmi, kuma Allah ya yi ma Wambai Mal. Muhammadu Sani dan Yarhusa Sarkin Zazzau cikin shekara ta 1846, shi kuma Sarkin Zazzau Malam Muhammadu Sani a cikin wannan shekara Allah Ya kaddara ya yi ma Malam Ahmadu Galadiman Zazzau.

GIDAN GALADIMAN ZAZZAU MALAM AHMADU.

Bayan Sarkin Zazzau Malam Muhammadu Sani ya nada Malam Ahmadu Galadiman Zazzau, Galadiman ya zauna ne a gidan sarautar Galadiman Zazzau na wannan zamanin. Gidan na gabas da gidan Sarkin Zazzau ne. Amma kuma Galadiman na da gidansa a Unguwar da a yau ake kira Albarkawa lamma inda gidan yake yafi shahara da Famfo) a cikin garin Zariya. Shi wannan bawan Allah ya kasance yana daya daga cikin manyan Malamai kuma manyan Hakimai a zamanin Sarkin Zazzau Malam Muhammadu Sani. A yadda tarihi ya nuna, hakika Galadima Ahmadu ya kasance mutafannini ne (masanin ilmin fannoni daban-daban) saboda haka ya kasance mai yawan almajirai. Wasu daga cikin dalibansa na Zazzau sun hada da; sarkin Zazzau Malam Muhammadu Sani da Moyi dan Salanke Mal. Sada. Sannan akwai Dallatu Tagwai dan Hammada da Malam Yaya da 'yayansa kamar su Muhammadu Modibbo (Turakin Galadima Ahmadu) akwai Shehu Usman da Malam Umaru (Wali) da wasun su da dama wadanda ba za mu iya ambata ba.

RASUWAR GALADIMAN ZAZZAU MALAM AHMADU.

A lokacin da Sarkin Hadeja Buhari dan Didi ya fita daga da'ar Sarkin Musulmi, Aliyu Babba. Sarkin Musulmin, ya aiki Wazirin Sakkwato zuwa gabas (Hadeja) don ya fitar da Buhari ya nada dan'uwansa Ahmadu Dodo. Bayan komawar Wazirin Sakkwato, sai Buhari Dan-dibi ya sake tayar da kayan baya yai tawaye. Ganin haka ne Sarkin Musulmi ya aiki Wazirin Sakkwato Malam Abdulkadir dan Gidado don fada da Buhari tare da sauran garuruwa kamar su; Kano akwai Katsina da Bauchi. Zariya ma ta aika da nata rundunar mayakan karkashin jagorancin Galadima Ahmadu da Madakin Zazzau dan sarkin Zazzau Sani. Wannan yaki da aka fi sani da yakin Buhari, an yi shi ne a cikin kimanin shekara ta 1853 (Miladiyya) kuma a wannan yakin ne aka kashe Galadima Malam Ahmadu. Marigayin ya rasu ya bar 'ya'ya da dama. Babbansu a maza shi ne Muhammadu Modibbo (wanda tun Galadima Ahmadu na da rai ya yi masa sarautar Turakin shi dalilin kenan da ya sa ake ce da shi Turakin Galadima). Akwai Shehu Usman da Haliru (Alkali) da Bello. Sannan akwai Umaru (Wali) sai Abdullahi (ana ce da shi Dan-Daudu, Wazirin Magaji mai-kawari) sai Abdulkadir da sauransu.

'Ya'yan Galadima mata kuma akwai Goggo Dikko da Guggo Rakiya wacce ta auri Moyi dan Salanke, sauran sai Guggo O'O (Fadimatu) da Dada matan Larabawa wacce ta auri Dallatu Tagwai dan Hanumada daga baya kuma ta auri Sarkin Larabawa a Sakkwato.

SARAUTAR KANENSA GALADIMA ARDO.

Bayan rasuwar Galadima Ahmadu, sai kanensa wanda yake shakikinsa ya zo Zazzau daga Misau don yin ta'aziyyar Galadima

Ahmadun, ana kiran kanon nasa Ardo, wanda daga baya sarkin Zazzau Malam Muhammadu Sani ya yi masa Galadima, watau ya gaji wansa Malam Ahmadu kenan. Allah bai ba Galadima Ardo haihuwa ba har ya rasu (a zamanin Sarkin Zazzau Malam Abdussalam) wanda ya gaje shi kuma shi ne Galadima Hamman dan Bafayo Magajin Gari.

ZAMAN GALADIMA AHMADU A KASAR ZAZZAU.

Zazzau ita ce ta zama gida a wajen Galadima Ahmadu, tun daga kusan tsakiyar karni na goma sha tara na Miladiyya, mafi yawan 'ya'yan Galadima duk sun rayu ne a Zazzau a cikin karni na goma sha tara. Saboda haka Zazzau ita ce ta zama gida a wajen zuri'ar Galadima Ahmadu. Don haka ne muka ga ba shi yiwuwa mu ba da tarihin Galadima Ahmadu, ba tare da mun dan tsakuri tarihin Zazzau din ba.

Garin Zariya, za a iya cewa yana tsakiyar arewacin Nijeriya ne. Garin na zagaye da ganuwa mai kimanin fadin kilomita goma sha hudu da rabi. A da wannan ganuwa na da kofofi tara ne daga baya aka rufe daya suka zama takwas. Masana tarihi sun nuna cewar wata Sarauniya ce da ake kira Bakwa Turunku (wasu kuma sun ce namiji ne,watau Sarki kenan) ta gina Zariya a tsakanin karni na goma sha shida zuwa sha bakwai. Garin kanshi ake kira Zariya amma masaurantar garin ana kiran ta Zazzau. An ruwaito cewar a wajen shekara ta 1536 (Miladiyya), akwai wata Sarauniya da ake kira Bakwa Turunkwu wacce ita ce Sarauniya ta farko a Zazzau kuma sai da ta yi kimanin shekaru talatin tana mulkin, wacce ta zama Sarki na ashirin da biyu a tsarin mulkin Habe na Zariya. Inda Bakwa ta fara zama shi ne wani gari da ake kira Turunku tsohuwa, kudu da birnin Zariya na yanzu. Tarihi ya nuna cewa ita ce ta

kori Jikunawa ta mai,da birnin Zazzau wurin da yake a yanzu. Sarauniya Bakwa Turunku tana da 'ya'ya biyu mata Amina da Zariya. Sarauniya Amina ita ce ta gaji Bakwa ta yi yake-yake da dama a ƙasar Hausa dalilinta ne ma,aka samu ganuwar Amina. Sannan ƙaramar 'yar Bakwa Turunku, ana kiranta Zariya wanda daga gare ta ne garin Zariya ya sami wannan suna. Kasar Zazzau ta bunkasa har ta zama daya daga cikin muhimman kasashen kasar Hausa. Koda yake babu tabbaci dangane da tarihin Zazzau na farko-farkon amma dai Zazzau kamar sauran garuruwan kasar Hausa, masarautar ta samo tushe ne kamar yadda aka ce, daga wani mutum mai suna Bayajidda, wanda ke da tarihi daban daban a kasar Hausa. Duk da yake ra'ayoyi sun bambanta dangane da ko wane ne Bayajidda dukkan ra'ayoyin sun hade kan cewa ya zo Barno inda ya auri 'yar sarkin Barno mai suna "Magira". Daga baya Bayajidda ya sami labarin za a kashe shi ya gudu daga Barno ya taho Garun-gabas, a inda nakudar haihuwa ta kama matarsa mai tsohon ciki, ya bar ta a nan ya yo kudu har ya iso garin Gaya har zuwa Daura. A Dauran ne, ya kashe macijiya ya auri Sarauniya Daurama ta hada masa da kuyanga,har ya zama Sarki. Bayan wani lokaci Daurama ta haifi Bawo. Bayajida ya ci gaba da rikon sarauta. Bayan rasuwarsa Bawo ya gaje shi. Bawo ya haifi 'ya'ya shida wanda suka hada da wansa na Garun-gabas "Biron" suka mulki garuruwan Hausa guda bakwai, wadanda suka hada da; Gunguma na Zariya sai Bagauda a Kano da Kumayau na Katsina akwai Doma a Garun-gabas sai Zaman Kogo a Rano da Gazaura a Daura. Dan Bayajida kuma tare da Kuyanga ya haifi 'ya'ya bakwai wadanda suka mulki garuruwan da ba Hausa bakwai ba; wadannan garuruwa sun hada da Kebbi da Yauri da Zamfara sai Gwari da

Kwararrafa sannan ga Nupe da Ilori.

Wannan masarauta na Zazzau na daya daga cikin garuruwan da ake kira Hausa bakwai. Tarihi ya kuma nuna cewar an sami sarakuna sittin ne cif na Habe a Zazzau. Sarki na farko shi ne Gunguma, Sarauniya ta farko kuma ita ce Bakwa Turunkwu, sarki na karshe kuma a tsarin sarakunan Habe ana kiranshi Makau. Wanda a zamaninsa (Makau) ne jihadin Fulani ya zo Zazzau. Makau ya fita ta wata kofa da aka camfe ta da cewar tana da kwankwamai, sai aka toshe kofar daya bi da zai fitan. Dalili kenan da kofofin Zariya suka tashi daga tara suka koma takwas.

ZUWAN JIHADIN SHEHU USMAN KASAR ZAZZAU.

Shehu Usman dan Fodiyo, Allah ya yarda da shi, ya fara jihadi ne a 1804 (Miladiyya). Shehu ya sanya al'majiransa suka zama sarakuna a kasashen Hausa, a cikin shekaru daban-daban bayan jihadin. A cikin shekara ta biyu da jihadin aka nada Malam Sulemanu a Kano, kuma bayan shekara uku da fara jihadin shehu aka ci Katsina aka nada Umaru Dallaje har ila yau, a wannan lokaci ne Shehun musulmi suka yi yaki da mutanen Barno aka nada Malam Zaki Kanuri. Malam Yakubu a Bauchi akwai Buba Yero a Gwambe da Modibbo Adama a Adamawa sannan Ishaka a Daura, da sauransu. A cikin shekara ta hudu da jihadin Shehu aka nada Malam Musa a Zazzau. To wannan jihadi na Shehu Usmanu, Allah shi yarda da shi da aka fara a 1804, shi ne ya kawo karshen mulkin Habe a Zariya. Sarkin Zazzau na Habe Makau ya bar Zariya kuma zuri'arsa ne suke sarautar Abuja. Sarkin Zazzau na Fulani kuma ya kama. A Zazzau dai gidajen sarautun Fulani guda hudu ne. Wanda ya fara sarautar a daular Fulani shi ne sarkin Zazzau Malam Musa (Fulanin Mali)

wandaya gaje shi shi ne Malam Yamusa (Fulanin Barno) sannan sai Malam Abdulkarimu (Fulanin Katsina) da Malam Abdulsalam (Fulanin Sakkwato). Ana kiran wadannan gidajen sarauta da sunaye kamar haka: Mallawa da Barebari da Katsinawa da Sullubawa.

JADAWALIN SARAKUNAN FULANI NA ZAZZAU DAGA 1804

SUNAYEN GIDAN SARAUTU	SUNAYEN SARAKUNA	SHEKARAN SARAUTA	YAWAN SARAKUNA
MALLAWA:-	MALAM MUSA	1808 - 1821	4
	SIDI ABDULKADIR	1860	
	ABUBAKAR	1873 - 1876	
	ALIYU DAN SIDI	1903 - 1920	
BAREBARI:-	MALAM YAMUSA	1821 - 1834	9
	HAMMADA	1846	
	MUHAMMADU SANI	1846 - 1860	
	ABDULLAHI YAYI	1863 - 1873	
	ABDULLAHI SAU BIYU.	1876 - 1881	
	YERO	1890 - 1897	
	KWASAU	1897 - 1903	
	DALHATU	1920 - 1924	
	IBRAHIM	1924 - 1936	
	JA'AFARU	1936 - 1959	
KATSINAWA:-	MALAM ABDULKARIMU	1834 - 1846	4
	SAMBO	1881 - 1890	
	AMINU	1959 - 1975	
	SHEHU	1975 -YANZU	
SULLUBAWA:-	MALAM ABDULSALAM	1860 - 1863	1

A halin yanzu an sami jumlan Sarakunan Fulani goma sha takwas a Zazzau, tun daga Malam Musa Bamalle har kuma zuwa mai Martaba sarkin Zazzau na yanzu Alhaji Shehu Idris wanda yake ya fito ne daga gidan sarautar Katsinawa.

Kasancewar Zariya daya daga cikin cibiyar nazarin addinin musulunci a kasar Hausa tun kafin jihadin Shehu Usman dan Fodiyo har zuwa yanzu, an sami makarantu da dama na manyan malamai wadanda ba zai yiwu in kawo su duka ba. Kadan daga cikinsu akwai:-

Makarantar gidan limamin Kona a Limanacin Kona sai makarantar Liman Gabdo da liman Durum ga ta Malam Ahmadu Adani a Zage-Zagi. Akwai makarantar gidan Limamin Juma'a a unguwar Juma da makarantar Salanke Malam Iyal dan Ibrahim tsoho a Kakaki. Sannan kuma akwai makarantar Malam Umaru Wali dan Galadima Malam Ahmadu a Albarkawa (Famfo) da Amaru. Akwai kuma makarantar Malam Rilwanu a Kofar doka, akwai makarantar Malam Moyi dan Salanke Malam Sada a Unguwar Alkali (Gangaren Tukurwa) sannan ga makarantar Malam Shitu dan Malam Abdulra'uf a Kusfa, ga ta Malam Salihu Lukmanu a Unguwar Alkali da makarantar Malam Abubakar Jakada a Kaura, ga makarantar Malam Yahuza bin Sa'ad a Iyan Juma da makarantar Malam Na'iya dan Malam Mayaki a Unguwan Nufawa, ga makarantar Malam Musa na magajiya da makarantar Malam Sambo mai-casa'in a Unguwar Karfe (sha-dantse) da makarantar Malam Muhammadu na Likoro. Da wasu da dama a cikin birni da kauyuku wadanda ba zai yiwu mu kawo su duka ba.

Wadannan makarantu da muka ambata tare da wasu da yawa da ba mu ambata ba a cikin birnin Zariya da Kauyuka, wasu daga

cikinsu sun faru ne tun kafin jihadin Shehu Usman dan Fodiyo, wasu cikin karni na sha tara karnin jihadin Shehun, wasu kuma cikin wannan karni da muke ciki wato karni na ashirin. Duk wadannan makarantu tare da wadanda ba mu ambatan ba, sun ginu sun ba da ilimi gwargwadon hali, an kari juna birane da kauyuka. Wadannan makarantu su suka sanya garin Zariya shahara da ilimi na addinin musulunci da Larabci.

SARAUTAR MALAM UMARU DAN GALADIMA MALAM AHMADU.

Zazzau dai kamar yadda muka yi bayani, za a ga cewar ta hada manyan mutane cikin birni da kauyuka a zamunna daban-daban. Kowane daya daga cikin manyan da suka gabata da irin zamanin da ya fi fice, imma mai sarauta ne (sarki), Ko Malami, shi dai wannan bawan Allah mai suna Malam Umaru dan Galadima Ahmadu ya yi fice ne a zamanin sarkin Zazzau Malam Muhammadu Sani (1846-1860) wanda kuma yai daidai da lokacin da Baffansa Galadiman Zazzau Ardo, ke sarauta. Koda yake, a daidai lokacin Galadancin Ardo, Malam Umaru yana tsakanin kasar Sakkwato da Gwandu yana karatu a cikin manhajan Shehu Usman dan Fodiyo da Shehu Abdullahi bin Fodiyo, sai sarkin musulmi Aliyu Babba, ya shawarci a yi ma Malam Umaru sarautar mahaifinsa watau Galadiman Zazzau. Amma a wannan lokaci an riga an yi ma Baffansa sarautar Galadiman, watau Galadima Ardo (wanda ya rasu a zamanin sarkin Zazzau Malam Abdulsalam 1860-1863). Saboda haka sai Sarkin Musulmi ya shawarci Sarkin Zazzau Malam Muhammadu Sani (1846-1860) da ya sami wata sarautar da zai ba Malam Umaru, sai Sarki Sanin ya yi ma surukin nasa Malam Umaru sarautar wali (don Walin yana aure da 'yar Hammada dan Yamusa,

mai suna Maryamu ana ce da ita Guggo Babba wasu kuma kan kira ta Guggon Mama.)

TAKAITACCEN TARIHIN RAYUWAR MALAM UMARU WALI.

A lokacin da aka yi ma Malam Umaru Walin Zazzau, aiki ya karu masa kenan a bisa da, domin ga aikin koyarwa ga kuma saraута. To da yake mun gangaro har zuwa nan, ya kamata mu dan waiwaya baya kadan don gutsuro abin da ya saukaka daga tarihin Malam Umaru Wali. Shi dai Malam Umaru Wali duk rayuwarsa tun daga haihuwarsa har zuwa wafati ya yi ne a cikin karni na goma sha tara na Miladiyya. Amma farkon tashin Malam Wali, ya tashi ne a wajen mahaifin tsohonshi Malam Umaru a garin Misau, bayan rasuwar Kakan nasa.kuma ya koma wajen Mahaifinsa Malam Ahmadu (Galadiman Zazzau). An ce, Malam Umaru Wali ya haddace Alkurani tun bai balaga ba kuma ya yi wannan karatu ne a wajen Mahaifinsa Galadima Ahmadu, daga nan kuma ya fara karatun littafai na Fikhu da Tauhidi da Lugga da sauransu; har kuma ya kai munzalin da ya fara zuwa daukan karatu a waje, a kasashe daban-daban kaman kasar Barno da Adamawa da Gwambe da Zazzau da Sakkwato d.s.

NEMAN ILMIN MALAM UMARU WALI.

Makasudin irin tafiye-tafiyen da mutanen da sukan yi don neman ilmi, shi ne, a wancan zamani za ka ga wani malami ya fi shahara a wani fannin ilmi na musamman, to don neman wannan ilmin sai su je su sami Malamin duk inda yake da zama don su yi karatu a wajensa. Misali a kasar Barno Malam Umaru Wali ya yi karatun Lugga a wajen wani Malami almajirin Shehu Umarul Futi. A

Sakkwato kuma ya yi karatu a cikin Manhajan Shehu Usman dan Fodiyo da na Shehu Abdullahi bin Fodiyo, kuma a nan Sakkwato din ya ci gaba da karatu a fannoni daban-daban a wajen wasu Malamansa kamar su; Malam Muhtasiru da Malam Tukur dan Binta. A Zazzau kuma ya yi karatu a wajen malam Yaya da Salanke Malam Sada. A takaice dai Malam Umaru Wali ya yi karatu a wurare daban-daban sai dai yawancin karatun nasa duk a gidansu ya yi, har kuma Allah Ya sa ya kafa tasa Makarantar a Zazzau, a cikin karni na goma sha tara na (Miladiyya).

TAKAITACCEN TARIHIN KAFUWAR MA'AHAD UMARU WALI.

Ma'ahad ta Malam Umaru Wali no daya daga cikin Makarantun da suka yi fice a kasar Zazzau a cikin karni na goma sha tara. Wannan makarantar kuwa ta kasance a gidansa ne (wanda mahaifinsa Galadima Ahmadu ya' gina) da ke Unguwan da a yau ake kira Albarkawa (Famfo) cikin birnin Zariya. Yana wannan Unguwar ne sai wata rana ya tashi zuwa kilisa, za shi kallon Kogi yadda ruwa ke wucewa, sai ya ga wuri a wata Unguwa da ake kira Amaru, a cikin Zariya. Wannan wuri duk an dake shi yai kyau kwarai da gaske, kuma ya ba shi sha'awa, sai Malam Wali ya tambaya ko wane ne ke da wannan wuri? sai aka sanar da shi cewar na wani mutum ne mai suna Cigoji, kuma asalin wurin, tilin rawan takai ne da Habe ke yi a lokacin Sallar Gani. Malam Wali ya nemi ganin Cigoji, domin ya nuna masa sha'awarsa ga wannan wuri. Bayan sun sadu, sai Cigoji ya ce zai sayar wa Malam Wali da wurin in yana da bukata. Daga karshe aka kulla ciniki, Malam Wali ya sai wuri.

Bayan sayen wannan wuri ne, ya gina gida wadataccen gaske da Masallaci, ya taso daga gidansa na da, don wurin ya yi masa kunci da matsatsi saboda yawan jama'a da baki masu karatu. Allah madaukakin Sarki kuma Ya kaddari Malam Umaru Wali da tarewa a gidansa da ke wannan Unguwa ta Amaru. Allah Shi ne masani. An ce, a lokacin da Malam Umaru Wali ya tare a wannan gida nasa da ke Amaru, mutane na ta fadin albarkacin bakinsu, cewar ya je ne don ya kebe ya sami daman rokon Allah sosai, don ya zama Sarkin Zazzau. Saboda wai an ce wanda ya zauna a wurin zai zama Sarki. To tunanin mutanen kenan. Bayan tarewar Malam Umaru Wali sai karatu ya kara kafuwa aka ci gaba kamar yadda aka saba, dalibai suka yi ta bullowa daga sassa daban-daban na kasar nan da makwabtanmu. Allah Ya albarkaci makarantar da irin wadannan dalibai masu bambancin harshe wadanda suka hadu da Hausawa don neman ilmi kuma suka fi kowa wadatuwa da ilmin addini a wannan zamani a kasar Hausa. A daliban akwai Filani da Barebari da Hausawa. Saboda zaman tare na neman ilmi, akwai masu sarrafa harshen Larabci da Filatanci da Barbarci da kuma Hausa. Babban abin shi'awa shi ne, shi kansa Malam Umaru Wali ya wadatu da duk wadannan harsuna, kuma yana karantarwa a cikinsu (Amma harshensa na asali shi ne Filatanci). Wannan, na daya daga cikin dalilan da suka sa makarantar ta yi yawan dalibai.

TALIFOFIN MALAM UMARU WALI.

A duk inda aka sami wanda yake da dalibai daban-daban, musamman wadanda suka danganci wadannan harsuna da muka zayyana. Za ka taras cewar makarantarsa ta sanu kwarai musamman a kasar Hausa, bare kuma har Allah Ya sa shi wannan Malami Allah Ya ba

shi ikon yin talifofi littattafai. Wannan kan sa a kowane Karni ya zama abin tunawa duk lokacin da aka duba aikin da ya yi. Ta wannan, fuska ta rubuta littattafai, Malam Umaru Wali ya yi talifofi da dama, Ga wasu daga cikin sunayen litattafan da Malam Umaru Wali ya wallafa, kamar yadda Malam Maccido Ibrahim ya jero su a litattafinsa da yai bahasi a kan Umaru Wali a 1982 . Miladiyya.

1. KITABU BAYANI MAZAHIBIL A'IMMATIL ARBA'ATI. Wanda ke magana a kan mashabobin nan guda hudu watau Maliki da Shafi'i da Hambali da Abu-Hanifa.

2. TUHFATU ASGARIL'DALIBINA LI'AMIRIL MUMININA FI ILMIL JIHADI. A wannan litafi Malam Wali yai bayanin kyakkyawar niyya saboda jihadi da falalan karfafa ma mutane gwiwa saboda su yi jihadi da hujjojin da suka nuna jihadi wajibi ne da gargadi ga wanda ya gudu ma jihadi da sakamakon wanda yake mujahidi.

3. MUDIHATUL ABDALI KITABUN FI ILMIL SARFI. Wannan littafi yana koyar da ilmin Tasarifi da ilmin larabci, watau sanin yadda asalin kalma take da yadda ake tsago wata a jikinta.

4. AL'ALAKUN NAFISI AL'MU'ALLAKU ALA JAYADIN NAHWIYIL MUHAKKIKI . (Fannin Nahawu. Amma littafin na magana ne a kan matsayin kalmar "Lau" yadda ta ke a larabci).

5. MUFHAMUL BALID FI ILMIL NUJUM. Wannan littafi na fahimtar da ilmin taurari ne, ga mutum mai raunin fahimta.

6. MIFTAHUL MUGLAK FI ILMIL MANDIK. (Mandik yana koyar da ilmin sanin hikima na kowane irin fanni; da Imam Gazali ya ke cewa wanda ba shi da shi ba a sakankancewa da ilminsa.

7. KITABU RIJALIL SANAD (ARRISALATUL MAI-MUNA). A wannan littafi Malam Wali ya yi bayanin wanda ya karbi darika ne a hannun shi; watau Shehu Muhammadul Hashimi Al-waddayi(mutumin Waday a cikin Cadi a yanzu) shi kuma ya karba daga shehinsa Imam Habib shi kuma ya karba daga shehinsa Umarul Futi shi kuma ya karba daga shehinsa Sharifi Muhammadul Gali shi kuma ya karba daga uban Abbas Shehu Ahmadu Tijjani.

Hanya ta biyu da ya karbi darika Umarul Wali ya karba daga shehinsa Ibrahim Al-Barnawi (mutumin Barno) shi kuma ya karba daga shehinsa Muhammadu dan Muhtar Asshanjidi shi kuma ya karba daga shehinsa Ahmadu Tijjani karami wanda ya rubuta littafi (MUNYATIL MURIDI) shi kuma ya karba daga shehinsa Muhammadul Habib shi kuma ya karba daga uban Abbas Shehu Ahmadu Tijjani.

8. KITABU MA'ADINIL MA'ALIBI DINIYYA. Wannan littafi, yana magana ne a kan dalilan da ya sa ake haduwa wajen yin zikiri da bayyana shi da ake neman dalibi ya yi da dalilan da suka wajabta ma mutum ya koma ga Ubangijinsa da dalilai 24 wadanda suke gadar da kekashewar zuciya da abubuwan da suke rushe aikin ibada da karkasuwan darajan mutane wajen bin Ubangiji da rukunnen musulunci da abubuwan da ke kawo basira da kara imani da tuba da kuma sharuddan tuba.

9. MABLAGUL AMANI FIBAYANI UMURIL AULIYA'I WA AHMADID TIJJANI (ALFIYATUT'DARIK). A kan hanyan Tijjaniya ce, wannan littafin na magana ne akan Waliyai da karamominsu da tarihin Shehu Tijjani da suffan Muridi (dalibi).

10. KITABU BU'U BU'U (FI ILMIL ARUL). Shi kuma wannan littafi, asalinsa amsar wasikar wani malami ne da ya rubuto ma Malam Wali wasika daga Kano amma ba mu san sunan malamin ba. Littafin na koyar da ilmin Aruli (watau sanin ma'aunin waka) yana kuma koyar da ilmin luguden harshe.

WADANNAN LITTAFAI BA SU A HANNUN ZURIAR MAL. UMARU WALI A DUNKULE LITTAFAN KUWA SU NE.

11. MUFHIMIL BALIDI FI ILMITTAUHIDI.

12. KIFAYITUSSALIKI FI ILMIL-HISABI.

13. ADIMUL MISLI (littafin kimiyya ne).

14. KURAL FADALI (littafin sanin Tarihi).

15. RISALATU TAHSALILUN AMANI FI WASAYA SHEHUNA AHMADU TIJJANI (wannan littafin wasiyyoyin Shehu Ahmadu Tijjani ne).

16. ATTANBIHATIL-AL-ANIKA (littafi ne na Wa'azi ko fadakarwa).

17. TAS-HIRUL ASAGIRI LIMA FIL YAWAKITI WAL JAWAHIRI (Sharhi ne a kan littafai guda biyu na SHA'ARANI).

18. TA'ANISUL IHWAN FI TARIHIL SUDANI ,yana magana a kan tarihin kasar bakar fata ko jama'an Sudani.

19. AS-HALUL MASALIKI IFA KAWA'IDI AL-IMAMU MALIKI FI ILMIL KAWA'IDI (Littafin shara'a kan hanyar malikiyya).

20. ILAHU AL GASSI WASSAMIN (Sharhin littafi da ake kira Jawharul Maknuni.

21. LUBABU ILMISSIYARI (Yana magana a kan tarihin halifofin manzon Allah guda hudu Abubakar da Umar da Usman da Aliyu. Wani yankin littafin na nah a Gidan Tarihi da ke Kaduna watau, "National Museum and Monuments").

22. MASA'ILU ABDULKADIR BINIL MUSDAFA (Wanda yake, tambayoyin wani malami ne mutumin Sakkwato, Malam Walin ya amsa ya kuma kara da nasa tambayoyin duk ya hada ya amsa ya maishe shi littafi).

23. ILMIN-NAFIS FI TAZKIYATTI NUFUS (A kan hanyar tasawwuf ne).

Iyakan abinda ya saukaka daga gare mu kenan.

AL-MAJIRAN MALAM UMARU WALI.

Babu shakka a bahasi irin wannan zai yi wuya mutum ya kawo ayyukan da wani bawan Allah ya yi gaba daya, sai dai kawai mutum ya kawo abin da ya saukaka. Kamar yadda muka gani daga baya cewar Malam Umaru Wali ya yi littafai da yawa don taimaka wa addinin Musulunci, tare da fatan za su amfani na baya. To haka kuma Walin ya yi kokarin karantar da mutane da dama wadanda su ma suka karantar da wadansu mutane a zamaninsu. Misali, in ka debe 'ya'yan Malam Umaru Wali kamar su Malam Ahmadu Guruza da Malam Aminu da Malam Aliyu da sauran 'ya'yansa baki daya, Malam Wali ya horar da dalibai masu yawa wadanda suka yi fice a bangaren ilmi, ko da yake akwai sarakuna amma wannan bai hana an san da su ta fuskar ilmi ba kamar; su Sarkin Zazzau Malam Kwasau dan Yero da Sarkin Zazzau Malam Aliyu dan Sidi sannan ga wadansu Malaman; kamar su, Malam Sani na Kofar-Doka da Alkali Ahmadu Lugoge da Malam Sambo mai-Casa'in da Galadima Adamu dan Dokaje. Haka kuma akwai mutane kamar su Malam Garga Alkalin Nafada Gwambe da Malam Hussainin 'Boko (Sakkwato) da Wazirin Kano Gidado da kuma sauran

dalibansa da dama a wurare daban-daban musamman wajen kasar Gwambe da Adamawa wadanda ba mu ambata ba duk muna fatan Allah shi saka musu da alhairi, shi kuma sa suna tare a aljanna.

GARIN KAURAN WALI.

Wannan makaranta ta Malam Umaru Wali ba ta tsaya a cikin garin Zariya kawai ba, har ta dan matsa kadan ta ci gaba a wani kauye da a yau ake kira Kauran Wali. Malam Umaru Wali ya yi wannan gida na garin Kaura ne saboda canjin zamani da rikice-rikicen siyasa a zamanin Sarkin Zazzau Malam Sidi Abdulkadir.

Shi dai wannan gari na Kaura, ainihinsa garin Habe ne. A wancan zamani an ce duk garin ba mai kulle, zuwan Walin ne garin ya shiryu aka koma ma addini tsantsa. Har Malam Wali ya gina gida da masallaci a Unguwar Makera da a yau ake kira Unguwar Wali, daga baya kuma sunan garin ya tashi daga Kaura, ya koma "Kauran Wali", wadda a yanzu ta ke cikin karamar Hukumar Makarfi, da ke Jihar Kaduna. A wannan gari ne Malam Umaru Wali ya ci gaba da talifofinsa, koyarwa da Noma har ya yi zama irin na Tasawwuf (watau kebewa don neman kusantuwa da Allah).

KAFA GARIN RAHAMAN WALI.

Malam Umaru Wali bayan yin gidan Kaura ne ya je Sakkwato, wajen Sarkin musulmi Umaru dan Aliyu Babba ya yi masa izinin kafa Rahama. Lokacin da Malam Umaru Wali ya kafa garin Rahama, bai kafa da kowa ba daga bayinsa sai almajiransa. Wannan gari ya fara bunkasa tun Malam Umaru Wali na da rai amma bai tare ba aka ce, ya ce "ga gari yai gari amma la'asar ta yi". Shi ma wannan

gari na Rahama ana ce da shi Rahaman Wali, a yanzu yana cikin karamar Hukumar Makarfi ne na Jihar Kaduna.

A wata ruwaya kuma, an ce bayan sarautar Sarkin Zazzau Malam Sambo dan Abdulkarim, sai Sarkin Musulmi Umaru dan Aliyu Babba ya aiki Wazirin Sakkwato da takarda cewa ya ba Malam Wali sarautar Zazzau sai Walin ya nuna rashin sha'awarsa amma ya nuna goyon bayansa da a ba Madaki Malam Yero dan Abdu, don ya yaba hankalinsa. Allah kuma Ya kaddara Sarkin Musulmi ya amince ya ba Malam Yero dan Abdu sarautar Zazzau. Da su Malam Walin za su dawo daga Sakkwato sai Sarkin Musulmi Malam Umaru dan Aliyu Babba ya yi ma Malam Umaru Wali izinin kafa garin Rahama tun da ya nuna masa yana da sha'awar noma.

RASUWAR MALAM UMARU WALI.

A cikin shekara ta 1897 (Miladiyya) Allah Ya yi ma Malam Umaru Wali rasuwa, a gidansa da ke garin Kauran Wali, kuma a gidan nasa aka rufe shi. Allah shi gafarta masa tare da sauran iyaye da kakanni da jama'an Musulmin da suka riga mu baki daya, amin.

Sanin kowa ne cewar, musamman a kasar Hausa akan rika bayyana karamomin manyan mutanen da suka gabata; ta wannan fuska mutane sun ta bayyana irin karamomin da Malam Umaru Wali yake da su, wanda ba za mu iya kawo su a nan ba. Amma an yi ittifaki cewa Mal. Umaru Wali ya kebanta da abubuwa guda Uku. Watakila ma wannan ne ya ja hankalin Alkali Malam Umaru Ibrahim (Jikansa) har ya rubuta wata Kasidar tuna dangi. A cikin Kasidar ya bayyana cewar; mutane kan ce rayuwar Malam Umaru Wali ya taka tudu Uku,

kuma kowane Gangare (tudu) da akwai dansa da ya fi kefanta da shi. Bangarorin kuwa su ne siyasa da ilmi da Tasawwuf.

'YA'YAN MALAM UMARU WALI MAZA

(i) An ce a lokacin da Malam Umaru Wali yake sha'anin mulki ya haifi dansa mai suna Malam Ahmadu Guruza. Wanda ya ke bayan karatu shi ne halifan Malam Umaru Wali a Gangaren siyasa don da farko ya yi magatakardan sarkin Zazzau Malam Kwasau dan Yero (Wanda ya ke surukinsa ne yana aure da kanuwar Sarkin Zazzau kwasau din, da ake kira matar kawu, 'yar Sarki Zazzau Yero)Daga matsayin magatakardan Sarki kuma, aka yi ma Malam Ahmadu Guruza Turaki Karami, Hakimin Igabi a zamanin Sarkin Zazzau Malam Aliyu dan Sidi. A wannan lokaci ne kuma aka yi masa sarautar Waziri a Zazzau, kuma shugaban Majalisar Sarkin Zazzau, a shekara ta 1910 Miladiyya. Bayan wannan sarautar ce kuma aka yi ma Malam Ahmadu Guruza sarautar Makama Karami hakimin Soba, duk dai a zamanin Sarkin Zazzau Malam Aliyu dan Sidi. Har kuma Allah ya dauki kwanansa, a farkon Sarautar Sarkin Zazzau Malam Dalhatu dan Yero a shekara ta 1921. Allah shi gafarta musu baki daya, amin.

(ii) Misalin mataki na biyu kuma shi ne, lokacin da Malam Umaru Wali ya fi karkata ga sha'anin ilmi, sai ya haifi da sunansa Malam Aminu, wanda yake shi ma ya fito ma'abucin ilmi ne, a zamaninsa yana daya daga

cikin fitattun mutanen da suka wadatu da ilmi a kasar Zazzau. Shi ma ya rasu ne, a zamanin Sarkin Zazzau Malam Dalhatu dan Yero kimanin shekaru biyu bayan rasuwar dan'uwansa Makama Malam Ahmadu dan Wali. Allah Shi nawwara kabarinsu shi kuma kyauta kwanciyarsu, amin.

(iii) Sai misalin mataki na Uku, lokacin da Malam Umaru Wali ya karkata ga sha'anin Tasawwuf (watau kebewa don ibadar Allah). Sai ya haifi dansa mai suna Malam Aliyu, shi kuma Malam Aliyu shi ne aka ce a wajen Zuhdu (gudun duniya) da Takawa (tsoron Allah) shi ne za a fi iya kwatanta shi da Malam Umaru Wali. Saboda haka mutane sun karfafa cewar Malam Aliyu Waliyyi ne kamar mahaifinsa, to amma shi Malam Aliyu ya rasu ne, a zamanin Sarkin Zazzau Malam Aliyu dan Sidi, watau ya riga yayyensa rasuwa. Allah Ya sa Aljanna ce makomarsu da mu baki daya, amin.

Bayan wadannan abubuwa uku da Malam Umaru Wali ya kebanta da su, wanda ga dukkan alamu an sami wadanda suka gaje shi daga cikin 'ya'yansa Uku da muka lissafa, har ila yau akwai wasu 'ya'yayen nasa, kamar su; Malam Muhammadu Magaji wanda banda karatu ya yi sha'awar noma kwarai kuma Allah Yai masa arziki a cikin wannan sana'a ta Noma. Daga baya kuma, Sarkin Zazzau Malam Dalhatu dan Yero ya yi masa magatakardan Magajin-gari Abdu dan Maikawari. Ya koma Faki yana magatakardan ne ma ya rasu a zamanin Sarkin Zazzau Malam Ibrahim dan Kwasau. Allah shi gafarta masu, amin.

Sannan sai ɗansa Malam Haliru wanda daga farko Sarkin Zazzau Malam Dalhatu ya so ya yi masa Alƙali, amma ya nuna ma Sarkin rashin sha'awarsa da wannan mukami, sai Sarkin ya yi masa magatakarda karami, har ya kawo zamanin Sarkin Zazzau Malam Ibrahim ɗan Kwasau yana maga-takardan. Turawa suka ce dole sai mutum ya san alƙaluman boko. Saboda haka ne, sai aka ce dole su Malam Haliru su zo a koya masu boko,da jin haka sai Malam Haliru magatakarda ya ce don Allah Sarkin Zazzau ya sawwaƙe masa aikin, don ba zai yiwu yana da gemu cike da furfura ya tsaya yana koyon boko ba. Sarkin Zazzau yo ce zai ba shi wani aikin, ya ce ya ha ƙura. Ba a daɗe ba shi ma ya rasu. Allah shi sanyaya musu, amin.

Sannan sai karaminsu a maza wanda ake kira Malam Musa (Dan-Galadima) wanda ban da karatu rayuwarsa ta fi karkata ne a noma da kiwo a sana'ance, abinda ya yi kenan har ya koma ga mahaliccinsa' a zamanin Sarkin Zazzau Malam Ibrahim ɗan Kwasau. Allah Ya sa Aljanna makomarsu da mu baki ɗaya, amin.

'YA'YAN MALAM UMARU WALI MATA.

To wadannan da muka ambata mutum shidan da suka gabata, su ne 'ya'yan Malam Umaru Wali maza,sannan akwai 'ya'yansa mata, guda biyar, wadanda za mu yi bayaninsu yanzu in Allah Ya yarda.

'Ya'yan Malam Umaru Wali matan dai guda biyar ne to amma a nan za mu haɗa su da gidajen mazansu ne don fayyace inda zuri'arsu take. Da farko dai akwai; Fadimatu (Guggon Nasare) da ta auri Makama Ja'afaru ɗan Abdu, a Kaura. Sai Maryamu da ta auri Abdun Guggo ɗan Magaji Kari, a Madaka, sannan sai Halimatu Jaɓɓa

da ta auri Magajin Gari Maikawari dan Yero, sannan sai Aishatu (Ajuji) da ta auri Mu'azu dan Yero, a Kaura, sannan sai autarsu Hadizatu da ta auri Sarkin Zazzau Malam Dalhatu dan Yero. Idan an lura za a ga cewa duk wadannan matan sun yi aure a cikin garin Zariya ne.

Koda yake, wasu daga cikin 'ya'yan Malam Walin mata, mazansu na farko sun riga su rasuwa, saboda haka sun sake aure a wasu wuraren. Kamar Fadimatu (Guggon Nasarel daga baya, bayan rasuwar Makama Ja'afaru ta auri Hussainin Boko dan Muhammadu Tukur na Sakkwato. Haka ma Halimatu Jabba daga baya ta auri Dan-Galadima Zubairu dan Yero, a Rimin Bindiga a Zariya. Sannan ita ma Guggo Ajujin (Aishatu) ta auri Malam Rabi'u Kudingi, mutumin Kudingi ne cikin kasar Zazzau.

Duk cikin 'ya'yan Malam Umaru Wali mazansu da matansu ba wanda ya ketare zamanin Sarkin Zazzau Malam Ja'afaru dan Is'haku (1936-1959). Allah Shi gafarta musu da sauran daukakin al'umman musulmi baki daya, Shi kuma kyauta tamu mutuwar bayan tasu, amin.

To wannan shi ne takaitaccen bayani daga barayin mai rubutu daga abinda muka gani daga rubutattun tarihi da wanda muka ji daga shugabanni, kan tarihin Galadima Ahmadu da dansa Umaru Wali. Muna fata, 'yan-uwa masu sha'awan tarihi za su ci gaba da dorawa a kan abinda muka tsaya ko yin karin bayani a kan abinda muka rage. kuma su yi mana gafara ga abinda ba su ji dadin fadinsa ba.

ALHAMDU LILLAHI RABBIL ALAMIN WASSALATU WASSALAMU ALA NABIYIL KARIM MUHAMMADU RASULILLAHI (S.W.A.).

AYYUKAN DA AKA DUBA.

—— Abubakar Aliyu Assakafatul Arabiyya fi Najeriya, 1850-1960, Jami'atul Azhar Alkahira (Egypt) Nov. 1967 Ph.D Thesis.

—— Hogben and Green, The Emirates of Northern Nigeria (Oxford), 1966.

—— Ibrahim Maccido Musahamatu Umarul Wali Zariya, fi Mayadinil ilmi Wassakafati Wattarbiyyatil Islamiyyati Jami'atu Bayero, Kano 1982 (B.A Dissertation).

—— Jummai Zainab Dikko (Mrs) "Contributions of four reputable scholarstic quarters of Zazzau with a particular reference to two prominent Scholars of the nineteenth century in the development of Islamic Education of the Emirate" ATC/ABU, Zaria June 1989 (B.A Dicssertation).

—— Junaidu M., Tarihin Fulani, Zariya, 1976.

—— Madauci Ibrahim Bagudu "History of the Lands of Zazzau" 19... (Pamphlet).

—— Smith M.G., Government in Zazzau, 1800-1950 (Oxford) 1960.

—— Usman and Alkali (Editors) Studies in the History of Pre-Colonial Borno, Zaria 1983.

—— Darasin Dalibai na Hausa (107) B.U.K., 1987.

—— "Details of the installation ceremony of Alhaji Lawal Sambo, Director of Immigration as Walin Zazzau," on Friday 25th January, 1985. (Pamphlet).

—— "Details of the installation ceremony of Alhaji Salman Giwa as Galadiman Zazzau", on saturday 20th April, 1985 (Pamphlet).


—— "This is Kaduna State (Focus on) Zaria, Government Printer, Kaduna.

—— Gaskiya ta fi Kwabo "Tarihin Shehu Umaru Wali Umaru" Daga Gousu Ahmadu, 9 ga Satumba, 1993.

—— Zuma "Tsarin Sarautun Gargajiya a Mulkin Fulani a Zariya" Daga A.M. Hayatuddini, Zaria. 28 ga Yuli, 1985.

ABDULKADIR BELLO
MARIS, 1994

BISHIYAR DANGI



DEDOGPTV
20 OC
LISR

MABUDI

ALK - Yana nufin Alkali

G - Wannan na nufin Gwaggo a wasu wuraren Kuma Gwaggon.

* - Wadanda suka rasu bayan rasuwar Iyayensu amma basu da 'ya'ya.

( ) - Shekarun da ke cikin baka biyu, na nufin shekarun da mutanen suka rasu ne.


(a.b.c...) Sunayen da ke dauke da bakake zurfan da aka samu ta auren zumunci ne, don haka ne aka takaita, don kar mutum daya ya fita a wuri ...biyu. Bakin da MAHAIFIYA ke dauke da shi shine DANTA ke dauke da shi. d-s ?—— da sautansu

(|) Wannan alama na nadar da Da da Mahaifi/Mahaifiya ne.

• Sunayen da ke cikin baka biyu, na bayanin sunan yanka ne, ko kuma sunan rana na Sunayen dake kasansu ko kuma samansu.

• Ba a ko ina ne sunaye ke jere a kaidar shekaru ba.

ABDULKADIR BELLO
MARIS, 1994



BISHIYAR DANGI

NA

GIDAN GALADIMA AHMADU

DAGA

ABDULKADIR BELLO

Ban yarda wani mutum ya sake yin hoton wannan bishiya ba. Ko da kuwa warka daya ne, ba tare da izini na ba. In kuma mutum yayi hoton, to ya san da zaman yaci amana.

kunatu) da ta auri Malam Aliyu Zinau, kanen Alkali Ahmadu Lugegen ne.

Samun kuma marigayi Makama Ahmadu Dan wali, ya rasu ya bar 'ya'ya maza biyu; sai Malam Muhammadu Bello da sarkin ruwa Malam Ibrahim.

Ita kasar Firzan tana daya daga cikin garuruwar da suka hadu su kayi Libya. Babbar birnin Firzan ana kiran ta da suna Sabha. Birnin na da jama'a kamar dubu dari da tamanin da biyar, tana kudu maso yammacin Libya, mafi yawan jam'an garin musulmai, kuma larabawa da gurgubin kabilar Barbar, babban sana'ar su, kiwon dabbobi da 'yan kadan masu noma, a inda aka samu halin yin noman.

Kasar Firzan har zuwa karni na bakwai Girkawa ke mulkin ta. Mulkin Girkawa yazo karshe a lokacin da addinin musulunci ya samu nasara a cikin 640AD. Samun wannan nasara ta zama dalilin da kasar ta zama karkashin daular musulunci. A wurin karni na goma sha shida Turkawa suka kama kasar ta zama karkashin mulkin su. Kuma wurarren karni na goma sha takwas sai kasar Firzan ta zama mai dan cin gashin kanta a karkashin Bey.

Kasar dai duk yawancin ta rairayin hamada ne. Duk da haka, akwai jama'a a cikin ta tun zamanin zamunna, akwai kuma wasu 'yan wurare kamar a Kufra inda ake noma, ga kuma jama'a dake yin kiwon dabbobi, wasu kabilar larabawa da ake kira Badawi sune ke kiwon dabbobi tsakanin rairayin hamada da wurarern da ake samun ruwa, kamar yadda Fulanin nan ke kiwo, sai dai su wadannan Badawi sun fi yin kiwon tumaki maimakon shanu.

Tun lokacin da musulunci ya shigo aka kori Girkawa, musulunci ya fara tasiri a kasar, saboda haka, Firzan ta dade da addinin musulunci, amma bata zama wata cibiya na musulunci ba. Duk da haka masu zuwa aikin Hajji da kasuwanci daga yammacin Afrika suna bi ta kasar zuwa Makka da Turabulus.

A tsakiyar karni na goma sha tara lokacin 'yan mulkin mallaka, wani Muhammad al-Mahdi al-Sanusi ya nuna ki gare su da kuma Turkawa. Ya samu nasarar da ta kai duk kasashen Libya suka yarda aka nada shi sarki a 1911 AD (Firzan a lokacin turawan Faranshi suke mulkin ta, daga baya duk aka yarda aka ba al-Sanusi mulki). Soja sunyi juyin mulki a kasar inda suka ture al-Idris a 1969 AD kuma har zuwa yanzu soja ke mulki tare da Col. Muammar Quthafi a shugaba.

BABI NA UKU

ADDININ MUSULUNCI A KASAR HAUSA

MUTANEN AREWACIN NIJERIYA

Mutanen Arewacin Nijeriya sun fito daga jinsi dabam-dabam na jama'a hade da Barbar, Yahudawa, Larabawa wanda suka taso daga kasar Arewacin Afrika, hade da kuma wadanda suka fito daga daular musulunci na Andalusiya, Alkahira, Sham da sauran su, gauraye da bakaken fata 'yan asalin kasashen Sudan, da kuma fararen fata da auratayya ta hada.

KASAR HAUSA

Kasar Hausa na barayin kudu a yammacin Afrika. Shi wannan rukuni ya ratsa Afrika daga kogin Atlantika zuwa kogin bahar maliya, kuma yana tsakiyar rairayin hamada ta arewa, da kurmi na kudu. Masana tarihi na Larabawa da masane zane-zane na kirar ta kasar bakar fata -Bilad al Sudan-. Kasar Hausa na da tsawo kamar mil dubu daya da dari biyar daga yamma, da mil dubu biyu daga gabas.

ASALIN HAUSA DAKWAI

Tarihin da akafi badawa a kasar Hausa shine, cewan Abu Yazi dan Abdullahi Sarkin Bagdaza, wanda a Hausa ake ce mashi Bayajidda yazo Barno tare da jama'arsa, ya auri 'yar Sarkin Barno, daga baya ya gudu a saboda gudun makirci. A Biran ya bar wannan matan inda ta haifi da namiji. Shi kuma ya noto Daura, anan, saboda aikin jaruntaka da yayi ma mutanen garin, Sarauniyar Daura ta aure shi. Itama ta samu da, Bawo, wanda ya haifi 'ya'ya shida, hade da dan da aka haifa a Biran suka zama sarakunan Hausa Bakwai.

MUSULUNCI A KASAR HAUSA

Cikakken yaduwan addinin musulunci a Afrika ana lakaba shine da Uqba bn Nafi. Ya kafu a Kairawan a shekarar 670 AD. Musulunci ya shiga kasashen bakar fata ta hanyar 'yan kasuwa masu hulda da kasashen Hausa. Sanan nan hanyoyin 'yan kasuwa akwai wanda ta taso daga Sijilmasa zuwa Tangaza da Agadez zuwa daular Ghana, dayan kuma daga Sijilmasa zuwa Gawo da Tumbuktu, ga kuma wata data hada Nijeriya daga Libya ta hanyar Firzan zuwa Barno.

A cikin kasashen Hausa tarihi ya nuna musulunci yazo Kano zamanin Sarki Yaji (1319-85), a Katsina, musulunci yazo kusan dai-dai da Kano. Zariya kuwa sai wurin karni na goma sha shida, sai kasar Zamfara da Gobir, a Yawuri kusan karshen 1578 AD.

Duk inda addinin musulunci ya kafu sai harshrn larabci ya yawaita, kuma littafan ilimi da malamai su yawaita, don wadan nan ababe wani bayayi sai da wani, don haka ba'a raba daukaka da yaduwar musulunci daga watsuwar larabci da makarantu da littafan addini. Saboda haka wadansu wurare suka zamo wurin koyar da addinin musulunci da yada shi.

BABI NA HUDU

ZUWAN USMAN DN ISMA'IL KASAR ZAZZAU

Shi dai Usman bn Isma'il kamar yadda muka fada shine yazo kasar Zazzau, to shi kuma mahaifin shi a Firzan Isma'il bn Yahya. Da Usman bn Yahya yazo Zazzau an saukar dashi a wani Anguwa da ake kira yanzu da Anguwar Katuka (Zage-Zagi). Wajibi ne anan mu dan bada tarihin kasar Zazzau.

Kasar Zazzau tana tsakiyar Arewacin Nijeriya, tana da fadin kasa muraba'e dubu goma sha uku, garin ada tana zagaye da ganuwa da kofofi tara, yanzu sun zama takwas, domin rufe daya da aka yi. Masana tarihi sun fada cewan Sarki Bakwa a cikin sarakunan Habe shine ya gina birnin Zariya ya shiga. Wannan kasa ta Zazzau na daya daga cikin garuruwan da ake kira Hausa Bakwai. Tarihi ya nuna cewan anyi sarakunan Habe sittin. Na Karko Gunguma na karshe Makau wadda jihadi ta kora yaje suka kafa Abuja (Sulcja).

Shehu Usman dan Fodio (Allah Ya rahamseshi) ya fara jihadi a 1804 AD. Ya sanya almajiran sa suka zama shuwagabanni a kasashen Hausa, a cikin shekaru daban-daban lokacin jihadi. A cikin shekara hudu da yin jihadi aka shugaban tar da Malam Musa a Zazzau. Kuma duk lokacin da bukatar nada sabon Sarki ya taso ana zabo shi daga gidajen sarautar Fulani wanda suke Mallawa, Bare-Bari, Katsinawa da Sullubawa. Masu zaben Sarki na daga cikin Limamai, 'Yan Majalisa, da Hakimai na Zazzau.

Duk da cewan kasar Zazzau ta karbi addinin musulunci bayan Kano da Katsina, ta zama cibiyar nazarin addinin musulunci a kasar Hausa tun kafin jihadi.

Zuwa yanzu, ana samun makarantu da manyan malamai da dama da suka sa kasar ta zama wurin zuwa domin su samu ilimin fanonin addinin musulunci, mutane daga kusa da nesa na zuwa.

Lokacin da aka kammala jihadi zuwa yanzu, sunan Zariya ta daukaka wajen hanyar bayar da ilimi, don haka malamai da almajirai da yawa suke nufota. Sakamakon haka aka samu karuwar gidajen ilimi. Wasu daga cikin gidajen suna bada ilimi tun kafin jihadi, wasu sun fara cikin jihadi, wasu kuma bayan jihadi. Duk wadannan makarantu sun gina sun bada ilimi gwargwadon hali. Wadannan makarantu su suka sanya Zariya ta shahara da ilimi na addinin musulunci da larabci, har suka sa ana ma Zariya lakabi da sunan " CIBIYAR ILIMIN ADDININ MUSULUNCI".

Allah Ya yiwa Usman bn Isma'il rasuwa a cikin zamanin mulkin Sarkin Zazzau Isyaku Jatau (1782-1802). Allah ya jikan sa, Ya rahamsheshi, amin.

-8-

BABI NA BIYAR
HAWAN HALIFAN MALAM AHMADU ADANI

Zazzau kamar yadda mu kayi bayani a sama ta kunshi manyan malamai cikin birni da kauyukan ta a zamunna daban-daban. Malaman nan kowan nansu akwai zamanin fichen shi. Malam Ahmadu Adani yayi fice daga zamanin Sarkin Zazzau Muhammadu Sani (1846-60). Domin a cikin wannan lokacin bayan rasuwar mahaifinsa (Isma'il bn Ahmad), ya haye gadon koyar da karatu da bada ilimi a gidan sa a Zage-Zagi.

Malam Ahmadu Adani ma yabi sahun iyayen sa wajen kin karbar wata sarauta, amma, shima ya kasance yana bama sarki nasa shawara a duk lokacin da bukatar haka ta taso (abinda ya hana su karbar sarauta, rikicin tane tasa iyayen su barin garin Firzan. Saboda haka, da suka iso Zariya tun kafin jihadi, dai suka bi maganar ma'aiki cewan: Mafificin jama'a shine wanda ya koyi karatun Alkur'ani ya koyar dashi). Don haka, suka tashi tsaye wajen neman ilimin addinin musulunci da koyar da shi, da yada shi.

Malam Ahmadu Adani ya taimaka wajen habaka makarantan ilimi a gidan su. Shine ya fara karatun Tafsir a zuaren su (Bubban Zaure), a kullum da safe cikin watan Azumi -Ramadan- wanda har yanzu ana karatun. Kuma an hakikance, cewan, Malam Ahmadu Adani ya kure wajen Mada-ar Rasuluh da jawo fasahohi da kimiyoyi cikin Alkur'ani,kuma ya kasance mufassirin na Alkur'ani, mai kuma bada ilimin Fikihu, Tauhidi, Lugga da sauransu. mutane da yawa sunyi ittifaqi cewan shi Waliyi ne.

A lokacin sa mutane kanzo daga birni da kauye don daukar karatu da kuma neman tubarraki. Wasu da yawa daga nan, ya basu wuri suka zauna , wasu a kusa da gidan shi, wasu kuma a nesa da gidan sa. Kuma har yanzu zuri'ar wadannan jama'a suna zaune tare da zuri'ar sa.

-19-

Da tantama Iallai Malam Ahmadu Adani shi fito da Anguwar Zage-Zagi (Anguwar Katuka) yasa aka santa a Anguwa dake bada ilimin addinin musuluncI, wanda har yanzu akwai gidaje a Anguwar dake bada ilimi, walau na zuri'arsa, ko kuma na jama'an da su kazo kusa da shi.

Allah Yai gafara agare su da duk muminai a ranar da hisabi take tsayawa, amin. Allah Ya sa Aljanna ce makomarsu da mu baki daya, amin.

-10-

BABI NA DAYA

RASUWAR MALAM AHMADU ADANI

Allah Ya yima Malam Ahmadu Adani rasuwa a farkon zamanin Sarkin Zazzau Yero (1890-97). Marigayin ya rasu yabar 'ya'ya bakwai, maza biyar, mata biyu. Ga mazan: Malam Aliyu (M. Barau), wanda ya gaji mahaifinsu, ya ci gaba da bada ilimi, sai Malam Ibrahim (M. Balarabe), shi kuma shine ya gaji Malam Barau wajen karantarwa kuma shima ya dada karfafa girma gidan sosai, daga shi sai Malam Zulqifil shima ya bada ilimi matuka a gidan su, sauran su sune Malam Abdurrahman Allah bai ba shi daman koyarwa ba domin ya rasu kafin yayyen sa, karamin su wanda aka haifa bayan rasuwar Malam Ahmadu Adani shine Malam Muhammadu Zangina. A 'ya'ya mata kuma yabar Fadimatu wadda tayi aure a Baddaga da Rabi wadda tayi aure a kwarbai ita ta haifi Na'ibin Zazzau na yanzu. Allah Ya jikan su, Ya rahama masu, amin.

Shi dai wannan bada ilimin addinin musulunci bai tsaya akan Malam Ahmadu Adani ba da 'ya'yansa, aikin ta ci gaba. Lokacin da Malam Zulqifil ya rasu Malam Muhammadu Firabri dan Malam Ibrahim da aka fi sani da suna Malam Sharubutu ya ci gaba da bada ilimi addinin musulunci dai-dai gwargwadon sa, bayan rasuwar sa Malam Aliyu dan Malam Zulqifil ya ci gaba da bada ilimin. Allah Ya jikan su, Ya gafarta masu, amin.

Kamar yadda muka fada ana ma Zuriya lakabi da cibiyar ilimin addinin musulunci, kuma ta cika da manyan malamai ton kafin jihadi har zuwa yanzu. Ga wasu daga cikin manyan malaman da gidajen ilimi

Akwai makarantar gidan Limamin Kona, wannan gida ilimi ya bunkasa tun kafin jihadin Usman dan Fodio da shekara dari da sittin. Wanda ya kafa wannan gidan ilimi shine Sheik Haruna bn Jibrin. Malaman wannan gida sun shahara wajen ilimin Tafsir, Hadis,da sauran su. Ga kuma gidan Juma, shi wannan gidan ilimi ya kafu ta hanyar Malam Abubakar, sun shahara wajen ilimi Fikihu da Hadisai na Bukhari da sauran su, suke Limancin Juma;a, kuma yawancin Alkalan Lardi daga gidan suke. Sannan ga gidan Malam Umaru Ahmad a Kofan Doka wanda suma sun taimaka suna ta yada ilimi, su kuma sun kware wajen tafsir Jalalaini. Ga gidan ilimi na Malam Umaru Wali na Albarkawa, gidan da ya shahara wajen Fikihu da sufanci da sanin ilimin Furu'a, sun kuma kawo ma Zariya wani fannin ilimi da ba'a saba dashi ba sai daga zuwansu, kamar ilimin Mandik, wannan gidan ya barma na littafai fiye da ko wani gidan ilimi a Zariya. A Kakaki kuma ga gidan Salauke Mal. Iyal dan Ibrahim Tsoho, gidan da Allah Ya albarka da masana Fikihu. Can cikin Kusfa akwai gidan Malam Shi'itu, wannan gidan ilimi yayi suna wajen ilimin taurari da sufanci. Sannan ga wasu gidaje masu yawa kamar gidan Malam Sambo Mai Casa'in a Anguwar Karfe, ga makaranrat Malam Musa a Magajiya, gata Malam Abubakar Jakada a Kaura, sannan ga na Malam Yahuza a Iyan Juma, ga ta Malam Na'iya a Anguwar Nufawa, Akwai makarantar Malam Moyi a Anguwar Alkali, da wasu da dama a cikin birni da kauye wadanda ba zamu iya kawo su ba, duk su suka taru suka sa Zariya tayi farin jini wurin malamai da almajirai. Allah Ya saka masu, amin.

APPENDIX 13

KATUKAN ZAZZAU USMAN TSOHO SABULU 1804-1816

Mallam usman Tsoho shine tushen gidan sarautar katuka dake Anguwar Katuka a Zaria, kuma shine na farko da Mallam Musa yafara nada shi Katuka a 1804. Usman Tsoho yafito daga gidan sarautar habe na Kano wato gidan Kutumbi wanda yayi sarautar Kano har tsawon shekara ashirin da bakwai (27 years) . kuma Kakan Usman Tsoho shine sarkin na takwas a gidan kutumbi.

A lokacin da yake sarki sai sabani ya shiga a tsakanin shi da danshi wato Hamza (kuma shi Hamza shine ya haifi Usman Tsoho). Ganin yadda abin yayi karfi tsakanin shi da ubanshi sai yayi Hijira ya koma dawakin Tofa inda anan ne ya haifi Tsoho da Hamza, bayan rasuwan shi sai Usman Tsoho yaci gaba da rikon gidan kuma ya cigaba da noma da karatu.

A chikin shekarar 1798 ya tafi Sakkwato (Sokoto) in da yasadu da Mallam musa (sarkin Zazzau) ya kuma gabata da shi wurin Shehu Usman don yayi mubaya'a, a sannan ya dawo Dawakin Tofa, bayan Komawanshi Sakkwato (Sokoto) na biyu a shekarar 1804, sai Mallam Musa Yace mashi ya koma Gida ya shirya zai same shi don taho Zazzau don jaddada Addinin bisa umurnin Shehu Usman Ibn Fodiyo.

Daga nan Mallam Musa ya dawo ya fada ma dan uwanshi (Hamza) cewa ga yadda sukkayi du Mallam Musa saboda haka mai ya gani? Da ganan sai Hamza yace mashi ai nima zan bika cikin wannan ayari.

Da isowar Mallam musa sai suka kama hanya zuwa Zazzau suka kori Makau daga nan Mallam Musa ya bashi sarautar Katukan Zazzau kuma ya nada din uwanshi Hamza sarautar Dallatun Zazzau.

Wadannan sarautu na katuka da Dsallatu duka an fara yinsu akan wadannan mutane a cikin shekarar 1804.

Katuka Usman Tsoho ya samu shekaru har goma sha uku tare da Mallam Musa akan wannan mukami sarauta na katuka. Anyi kuma sarautar katuka har guda shidda a gidan kamar

Katuka Abdu	-	Abdukareem – Mamman Sani
Katuka Muhammadu	-	Mamman Sidi – Abdul Qadir
Katuka Usman II	-	Abubakar
Katuka urwatu III	-	Sambo
Katuka Shittu	-	
Katuka Abdu	-	Kwassau Ali dansidi shekara daya bayan nadashi.

Daga kan Katuka Abdu ba'a kara yin sarauta a gidan ba sai danshi Mallam umamaru da aka bashi sarautar mai Anguwa, zamanin sarkin Zazzau Kwassau zuwa zamanin Ali dan sidi ya rike wan nan mukami tun daga shekarar 1899 har zuwa 1906.

Da ganan kuma sai aka sami canji sarauta a gidan, inda aka soma sarautar fagachi. Wanda bada ita ga Muhammadu Dan mai Anguwa Ummaru (Fagachin Zazzau Muhammadu) har yanzu kuma suake rike da sarautar fagachi.

Katuka Abdu jikan Katuka Usman Tsoho ya zauna a wani gari da aka kira da suna kafin Katuka a lokacin sarkin Zazzau Mamman Sani daga baya kuma ya taso boda shekaru, sai aka kai kaninshi Katuka muhammadu.

Haka kuma Katuka Abdu ff ya zauna a wani gari da ake kira da suna kafin Katuka a lokacin sarkin Zazzau Mamman Sani daga baya kuma taso ya dawo Zaria ! bayan dawonshi sai aka kai kaninshi jiroye don rikon garin ba'a dade ba yayi haifi sai aka karbi rikon aka ba wani.

Muhammadu (Jirayi) shine aka baiwa sarautar Katuka amma ba'a nadashi ba rasu a zamanin sarkin Zazzau Abubakar.

APPENDIX 13
ANGUWAN MAGAJIN ASKA

Alhaji Ummaru magajin Aska age 70 years.

Ita wannan unguwa tananan tun kafin ayi jihadi, sannan kuma ba arabu da masu yin sanar ta Aski a unguwa ba. Ita wannan sarauta ta magajin asaka ba a san zamanin wani Sarki aka soma yin taba.

Kuma sarautar suna nan tun kafin a kafa birnin zaria. Mutanan gidan kuma suna daurin karaya da kuma Wanzanci. Ance wai Asalin zuriyar mutumen daga borno ne ba za a iya sanin magajin askan da a ka soma a a gidan tun farkon tarihi, wadandi za'a ya tunawa sune.

Magajin Aska Alhaji Maigari	Locacin Sarkin Zazzau Hamada
Magajin Aska Abdullahi	Zamanin Sarkin Zazzau Abdullahi
Magajin Aska ummaru	Baasan Zamanin wani sarki bane
Magajin Aska Ishulu	Lokacin Sarki Zazzaua Yero
Magajin Aska Abdullahi	Lokacin Sarki Zazzau Kwassau
Magajin Aska Bagi	Lokacin Sarki Zazzau Alu Dan sidi
Magajin Aska Abdullahi	Lokacin Sarki Zazzau Ibrahim
Magajin Aska Ummaru	Lokacin Sarki Zazzau Ja'afaru

APPENDIX 14

LADAN WAKILIN KAHU ANGUWAR KAHU

Age 94-95 years.

Kakan wakilin kahu Aneemasa Maaji ne, su Fulani ne wadanda suka taso da ga wajen Kano sukazo Zaria suka zauna kafin a yi Jihadi, lokacin Sarkin Zazzau Ishaqu Jatau. Maaji yana da yaya guda biyu ne, Muhammadu kwairinga da Ahmadu. Dukkan mutanen unguwan sun dauko salsalane daga wandanan mutane; kamar Hako.

1) Muhammadu mai kwairinga yana yaya guda uku, (a) Hamza (Hassan) wanda yana soja (b) Ibrahim (c) Nuhu.

2) Ahmad kuma yana yaya kamar su (a) Shehu (b) Hussaini (c) Umma (d) Dallatu (e) Buhari (f) Alu. Zuriyar gidan sunkoyo sanaar kahu ne. a zamanin Sarkin Zazzau Yamusa, sukaje Kano suka koyo sanar kahu. Shi kahu mashifindin doki ne. Saboda bukatarsa da sarakai sukeyi sai ya zama sanaar mutanen unguwan. (a) Shi hamza yana da yaya kamar (1) Yau (2) Ladi (3) Zainab (4) Sarki (5) Aisha (6) Sariki (7) Aisha (8) Aliyu (9) Mai wada (10) Gaude (11) Gwamma (12) Sa'a (13) Hafsatu (14) Saidu (15) Abdullahi (16) Talatu (17) Halimatu (18) Rabi (19) Safiya (20) Isa (21) Salamatu (22) Bilkisu (23) Abdulmimuni.

(b) Ibrahim ya haifi (1) Hamza wakilin kahu na yanzu (2) Mai gamma (Salihu), (3) Yayan Uwa (4) Maimuna

(c) Nuhu yana da sa guda daya (1) Bau

Jikokin Ahmad sune Shehu wanda ya haifi (a) Mustapha, (b) Abubakar (c) Muhammadu Magira (d) Muhammadu Kwairinga (e) Mohammadu Inuwa (f) Zulai (g) Hajara (h) Madinatu (i) Jaafaru.

Hussaini shi ya haifi (a) Binta (b) Safiyatu (c) Shehu

Umma bata da yaya

Balhatu Bata yaya

Buhari bai da yaya

Alu ya haifi (a) Salamatu (b) Barakatu (c) Abdullahi;

Yayan Hamza guda Ashirin da hudu ne, sune

Yau - ya haif (a) Hauuwa (b) Nuhu

Ladi - Bawa da Lamido

Zainab - Abbas da Zara

Sarki (a) Lawal (b) Jaafara (c) Munkaila.

APPENDIX 15

GIDAN TAKARAWA MUHAMMADU LAWAL, AGE 73 YEARS

Kakan mai wani gidan sunnan sa Muammadu Takaru. Takaru yana nufin Mahaddacin Alqurani ne. Su Fulani ne na Tofa, dalilin tasowarsu lokacin da Shehu Danfodio ya soma Jihadi sai Takaru yaje yayi masa murna Amma saboda Rikici na Jihadi sai ya taso daga Kano ya nufo Zazzau. Ya sauka a zabi. Suna daya daga cikin wanda suka gina ganuwar zabi. Daganan bayan kamar shekara biyu sai ya shigo Zaria. Sai Sarki ya bashi wuri yayi gida kusa da fan madauchi. Suna zaune a Zaria a kaci garin da yaki. Shi Takarau da shi da kaninsa suka zo Zaria. Kaninsa ya tafi kiwo, tun fitarsa kiwo har yau bai dawo ba. Daganan sai Takaru ya dawo wannan unguwa ya mutu ya bar yaya guda uku.

(a) Usman wanda yazauna a zabi

(b) Muhammadu Gidado

(c) Mallam Yero

Shi Mallam yero Yana ya ya kamar su (a) Samaila (b) Adamu (c) Abdullahi. Shi Mallam Yero yana da bayi sai yayi ma Galadima Dokaje magana cewar yanason ya sami fili yayi noma. Sai Galadima Dokaje yaba Mallam yero da zuriarsu wuri idan an fita daga bayan gari. Banyan an tsallake wani Rafi, yace tun daga nan abinda yayi kudu, na baka su kuma suka maidashi Rumada.

GIDAN MARINA:-

Saidu Aliyu 54 years 10th January, 1998

Asalin maigidan Anacemasa Muhammadu Na atala. Yazo daga Barno ne saboda neman ilimi. Da ya zo Zaria sai ya zauna akofar Galadima, yayi shekara kamar takwas ya na zaune yana karatu a karkashi Mallam yamusa kafin yayi sarki. Tun dama ya san Mallam Yamusa tun a can Barno. Lokacin da zai Aure, shine ya taso ya zauna a wannan gida. Wanda ya aure itace yar gidan dokadawa (Jikan Galadima Dokaje) anace mata Hassatu. Ita dayar matar kuwa mutumiyar kaura ce.

Bayan ya sami ilimi ya zama Babban Malami, yana zaune a fada sai sarki yace masa wani sarautar zai bashi sai yace ya nason yaci gaba da sana'ar da yasaba acan garinsu. Dama shi marini ne, to sai Sarkin yace ina kake ganin za'yi Rijiyoyin rini. Sai yace yaga wuri a unguwar magajiya sai aka cemasa ya tambayi masu wuri da aka tambayi sai suka bada Aro.

Bayan anbada Aro sai akayi aikin Rijiyoyi. Sai ya kasance yana koyawa mutanen anguwaa sana'ar suka iya. Daganan sai rashin jituwa ta shiga da daya daga cikin dan masu wurin. Sai aka soma masu gori, sai yakoma yayi gaisuwa a fada ya fada ma sarki cewa yana son fili ne ya mallaka. Sarki ya amince yace yaje duk inda yagano yazo yaga ya masa.

Wani daga cikin fadawar sarki mutumin kofar gayan yace yana da wurin da zai sayar. A kaje a gani sai yace yayi Nisa; yana so ya dawo kusa da gida. Sai nban Alhaji Baban kumbo yace yazo a nuna masa wani wurin a can kanfage. Da yaje sai yace yayi masa nisa. Yana son yadawo kusa da gida. To a cikin yaran sarki sai shamaki yace akwai wani wuri da an wuce kadarko. Da aka kaishi ya gano sai yace, e, wannan ya matso kusa da gida. A gayama sarki yaga wuri yakuma yimasa. Sarki yace ka matso kusa yace ya matso. Akayi Aikin Rijiyan aka sama Rini a wajen. To shi yasa ake cema wurin karofin kamatso. Rijiyoyin karofin ka matso guda goma sha shidda ne. Kafin ya rasu Mallam Muhammadu Nata'ala yana yaya guda uku. Akwai (a Abubakar, (b) Muhammadu (c) Abdullahi.

Abdullahi ya haifi yaya takwas da matan daya aura maisuna Aminatu daga Anguwar lalle sune (a) Mahamadu Na atala (b) Jibrillu, (c) Aliyu (d) Samaila (e) Aliyu (f) Idrisu (g) Halima.

(b) Ramatu. A yanzu zuriyar gidan suman da gidaje sun kai shidda. An daina Rini a karofin kamatso a 1966, lokacin da aka kashe Firimiyya na Arewa.

Shi Mahammadu Nataala yazauna a lafiyar Barebari ne, Abdullahi yana kasuwanci gishiri da kanwa zuwa lafiyan Barebare.

APPENDIX 16

ANGUWAN LALLE

MALLAM ABUBAKAR AGE 47

Anguar lalle ta samu ne a lokachin da ake fatunchi na Jakuna. Idan fatake sun shigo akwai wata Rijiya a unguwan. Ita Rijiyan akwai wata itace lalli da ta kewaye ta ne. To su wadannan fatake Idan sun zo hutawa sai suce baza su tsaya ako ina ba sai a Rijiyar; ta sami suna na Rijiyar lalle. Lokachin da akayi unguwoji, ita wannan yanki sai aka dauki wannan suna aka samata.

Gidan da suka zama masu unguwar lalle shine gida na farko a unguwar, anace ma mai gidan Ahmadu Buraza. Sanar Mutanen unguwar Shine Dinki to shi wannan dinki yananan fiye da shekara dari biyu. Tun suna saka irin nada har lokacin da Bature yazo suka sami kyalle suka Rinka dinki da Hannu bayan an shata irin wanda akeso harzuwa lokacin da suk sami keke gidaje da ke unguwar sunkai kamar sittin a hallin yanzu.

TARIHIN GIDAN AHMADU GARUBA

Mafi yawancin gidajen da suke unguwan sun samu ne daga gidan Ahmadu garuba. Amma Asalin wanda ya kafa gidan anace masa Abubakar. Su fulani ne, sullubawa sun taho ne daga wajen Sokoto. Shi Abubakar yazo ne tare da dabbobinsa da Bayinsa a cikin Jamar Mallam kayi mahaifin Sarki Zazzau Abdussalami. Yazo Zaria tare da dansa Mahmud. Sannan kuma ya haifi Abubakar, sai Suleiman sai kuma Ahmadu Garba sai Asma'u sai Dabo.

Shi dabo yana da yaya tare (9) Maimuna, Hasiya, Mallam Ali, Azumi (Hurairatu) sai Abubakar (informant) Aminatu sai kuma Fadimatu, sai Halimatu. yawancin zuriar wannan Bawar Allah sune suka cika unguwar.

Gabban sana arsu shine karatun noma da kiwo.

MAKAMA DODO

Mal Ungawar Jumare Abdulqadir age 70 years Mallam Yahaya age 62 years 14/1/1998.

Shi Makama uwaisu tare dashi suka zo tare da Galadima Dokaje. Shi Makama Uwaisu kanine wajen Galadima Dokaje, sunzo tare da Galadima daga Kano, a kasar Tofa Da a ka soma Jihadi sun yi Gwagarmaya wajen tabbatar dashi a zazzau. Daga Kano suka zo tare da dawaki ta kofar Galadima sun zauna a gidan mai unguwar Jamo (magajiya). Bayan da akayi ma Galadima Dokaje sarauta, sai yanada kanin shi Uwaisu

APPENDIXN 16

ANGUWAN NUFAWA

Alhaji Shittu Jibrillu Age 75 years.

Shi gidan Allalin ja'e yana daya daga cikin tsofattin gidaje da aka gina bayan an kafa birnin Zaria. An ce gidan Amina yar sarkin zazzau bakwa Turunku ne, a halin yanzun a unguwan a kwai manya gidaje guda uku.

(a) Gidan Alkali Ja'e (b) Gidan Mallam Jibrillilu (c) Gidan Sarkin Nufawa.

GIDAN ALKALI JA'E

Kafin jihadi Akwai wani gari da akece masa Ricifa. Mallam ibrahim ya taso daganan yayi zango akofan kona. Shi malami ne ba filatani ya shahara wajen Ilmin farailu. Ya zauna awannan gida gab da za'a yi jihadi. Da yazanna, sai wani Attajiri yazo ya zauna a unguwar karfe anace masa mallam ja'e. to duk abinda wanna Tajiri zai yi sai ya shawarci Mallam Ibrahim. Shine yasa ake cemasa Alkalin Ja'e shi Mallam Ibrahim yana da ya'ya' guda biyu (a) Mamman Sani (b) Suleiman. Mamman Sani bai dabe ba, ya rasu yabar da a'guda daya. Shi kuma a Suleiman ne yana da ya'ya' kamar su.

(a) Hassan (b) Muhammadu (c) Abubakar (d) Abdullahi (e) Dembo (f) Yakubu

Shi Mallam Hassan ya haifi (a) Haruna (b) Dikko

Mohammadu ya haifi (a) Zubairu (b) Yaro

Abubakar ya haifi (a) Usman

Abdullahi (a) Dembo (B) Saadu (c) Yakubu (d) Yahaya, wadannan sune kakanin mai hada tarihi sanaar. Gidan shine karatu da fatauchin goro.

GIDAN MALAM SHITU

Baban Mallam kolo kuwa Ainihin maigidan ana cemasa Mallam kolo mutunin Bidda ne, kolo ya haifi Abdullahi da wata yarinya wanda a kece mata innausa. Mahaifin kolo yazo Zaria ne kafin jihadi, a matsayin Bawa. Bayan jihadi aka fansar da shi. Shine ya komo unguwar ya zauna. Shi Mallam Abubakar shine ya haifi Mallam ladan shi kuma ya haifi Mallam Jibrilu, shi kuma ya haifi Mallam Shittu sanar su shine karatu da saka.

APPENDIX 17

ANGUWAN MELE:

Alhaji Ibrahim Muhammadu 95 Years.

Abinda ake nufi da mele sunan mutun ne Balarabe daga Barno. Yazo zamanin Sarkin Zazzau Kwassau ne. Shine yabashi wuri a wajen. Da duk unguwan duk kududdfi ne. Matafiya yan kasuwa idan sun zo da shanusa da Rakumansu suka zauna anan wurin wanda yake ada mazaunin baki ne.

Shi Mele dan kasuwa ne, yayansa sun mutu duka sai wata yarin ya ana ce mata Maimunatu.

APPENDIX 19

KUSFA

Alhaji Muhammadu Lawal Safahuden age 55 years.

Anihin kakan wanda ya kafa Kusfa ana ce masa ne Mallam Muhammadu Manda. Yataso daga Tunisia ne saboda shi yana cikin zuriyar Alkalan Tunisia ne, na wannan zamani sai Khalifa tazo kanshi. Shi yace bazai yi ba, kaninshi yayi. Kaninshi yaki yarda in dai har yana gari. Daga nan sai yace in bani za kayi. Daganan sai yanemi larabawa masu zuwa Katsina yandoto, wajen wani Malami Alhaji Saje.

Daga Katsina sai yataso da littafen sa zuwa Zamfara. Da yazo sai Sarkin Zamfara ya tsare shi yace yayi masa Addu'a. Saboda yanajin akwai wata fitina da zata bayyana. Mallam Muhammadu Manda yace ba fitina bace haske ne zata bayyana. Da Alhaji Saje ya sami labarin cewa Sarkin Zamfara ya tsare wannan malami, sai yace ya sakammasa dan uwa. Sarkin Zamfara yaki. Sai Alhaji Saje ya kara aikawa sannan Sarkin ya yarda. Suna cikin tafiya da ayarinsa sai aka sace masa kayayyakinsa. Bai tsaaya a ko ina ba sai a yandoto. Lokacin da ya isa suka sadu da Alhaji Saje. Alhaji Saje yayi masu masauki, daganan ya bincike abinda a ka dauke masa. Sai yaga babu littafan Bukhari, da Muslim Jamiul sangir da Tambihil Jafilin dakuma wanil littafi na fannin sufi dana fannin Tauhidi. Sai ya rubuta su duka kamar yadda suke, ya kuma watsa su a kasashen Hausa. Zamanin Sarkin Katsina Muhammadu Gozo (kasan Allah) Malam sai ya bude karantaswa. Ana zuwa karatu wajensa.

Sarkin Katsina Muhammadu Gozo ya gayyace shi yayi ma kasarsa Addu'a. Sai yayi Jinkirin zuwa. Sarkin Katsina Muhammadu Gozo ya kara aikowa da sako cewa yama gaida Mallam yana kuma yin tanbihi. Lokacin da su isa da sako sai Mallam Manda yace yana zuwa su tafi. Lokacin yana karataswa ne sai ya shiga gida, Sarkin Katsina kuwa kawai sai ya ganshi a gidansa. Yacema sarkin ka roke mu muyi maka addu'a kasa tayi Albarka. Sai ya daga Hannu yayi masa Addu'a, sai suka yi sallama. Mallam ya taka kofa sai gashi ya dawo gida.

Mallam yana nan a yandoto wajen Alhaji Saje ya haifi yayansa guda takwas, maza biyar mata uku. Dagananan sai Allah yai Masa rasuwa. Daganan sai dansa Mallam Abdurauf ya gaje shi shi kuma yacigaba da koyarwa.

Daganan sai Shehu Usman ya bayyana lokacin da yayi karfi, sai ya kira Mallamai kasar har da shi Mallam Abdurauf ya roke su da su taimakeshi da Addu'a don a kau da mulkin Habe. Anan garin Shehu Abdurrauf kuma ya haifi yayansa kamar Mallam Yusuf, Mallam Shittu, Mallam Aliyu da shauran su.

Dagannan sai Shehu ya sami Rinjaye. Ya ce ma Mallam Abdurrauf gawani gari yaje ya rika karban zakka yace bai yarda ba shi yana san yayi noma ne.

Yaci gaba da Noma a nan kauyen Madaro (Sokoto). Daganan sai Sarki Abdulkareem ya nemi Shehu yana son Mallam Abdurrauf da Mallam Shittu su kawo masa haskensu a Zaria. Shehu ya yarda. Shehu yaga ya masu suka yarda zasu Zaria. Mallam Abdurrauf yasa Mallam Shittu yazo Zarian yaga wuri sai yazo Zaria. Da yazo Zaria sai aka saukar dashi a wani gida. A Albarkewa gidan sarkin ladanai. Yana zaune a gidan mutane suka ga karatu wajen yaro. Cikin su har da Mallam Musa na Gidan Fulani. Mallam Shittu yana zaune ya samu shekara sai yayi ma Mallam Abdulkareem wani littafi anace mata <u>karimiyya.</u> Datakai hannun Abdulkareem sai ya rike wannan littafi bai kuma sallame shi. Malamin sai yasake yin wata littafi anace mata <u>kirimiyya.</u> To sai Mallam Abdulkareem ya sallameshi ya koma Sokoto a shekara mai zuwa sai suka dawo da Mallam Yusuf.

Da suka dawo sai suka zauna anan gidan nan na Albarkawa. Shi Mallam Musa yace ma Mallam Shittu akwai wani gida na Sharifi kusa dashi. Wannan gidan baifi karfinsha ba. Ya nemki izni wajen Sarkin ya bashi dama ya shiga gidan kusa da bakin kasuwa. Abdulakareedm ya yarda ya bashi wannan gidan shi wannan gidan gidane na wani boka wanda ya tara Aljannu yana meman Abinci dasu. Yawan Aljannu da suke gidan sun kai dubu da goma sha daya. Bayan ya mutu an rufe gidan ne da kayan. Sunan malamin, shine Mallam Tankari ya zone daga karau karau.

Mallam Shittu sai ya kari Aljannu da ke gidan gaba daya sai ya gyara gidan ya zauna da iyalansa. Ana nan sai ya kara samum wani gida, yasa babban dansa anace masa

Mallam Junaidu. Sunayen yayasa sune (a) Junaidu (b) Wa'alamu (c) Abdurauf (d) Sharihu (e) Yaskilu (f) Yusha'u (g) Wakashatu (i) Mansur (j) Muhammadu (k) Abdulkareem (l) Mammu. Sannan kuma akwai mata guda goma sha daya. Shi Mallam Shittu ya rasu zamanin Sarkin Zazzau Sambo ne dan Abdulkareem. Wanda ya gaji Mallam Shittu shine Mallam Junaidu, sai Mallam Waalamu. Daganan kuma sai Mallam Haji wanda zamanin sa wannan gidan ya shahara kwarai ne wajen Fanin Fiqh sufi Tauhidi, Hadith da mandiqi.

Shi kuwa Mallam Hajji Yayi Bunkasa zamanin Sarkin Zazzau Dalhatu ne har zuwa Ibrahim. Shi Mallam Hajji ya haifi yaya sun kai 130, wadan su daga cikin su akwai (a) Mallam Ikiramatu (b) Maurufi (c) Saluhu (d) Alkilu (e) Dahiru (f) Dayyatu (g) Muhammadu (h) Mammu (Shittu) (i) Atiku, (j) Habibu (k) Ali.

Almajiran Mallam Shittu su ne Mallam Saadu, Usman, Yaskilu, Yusha'u, Wukashatu kusfa. A cikin birnin Zaria kuwa Almajirasa su ne (a) Maaji Ishaku, Musa na Majayiya, Isa na Fadama, Mallam Sambo mai casa'in, Mallam Muhammadu Makole, Mallam Naiya, Mallam Nuhu.

LITTAFAN DA YARUBUTA

(1) Mallam Shittu ya rubuta littafi guda dubu daya da dari daya da goma shadaya a rayuwarsa, kadan daga cikin su, sun ne:

(a) Jiddil Azizi (b) Raiyya (c) Sunisiyya (d) Lammiyya yayi ma Sarkin Zazzau Abdusalam (e) Karimiyya (Abdulkareem) Sanissiyya (Sarkin Zazzau Muhammadu Sani) (f) Jimiyya, Daliyya, Mallam Shittu ya Shekara 95.

APPENDIX 20

GIDAN FULANI:

Alhaji Bello Yakubu, 95 Years.

Asalinsu Fulani ne wanda yakafa gidan ana kiransa Muhammadu Yaro yazo ne da ga wajen Sokoto (Yandoto) kafin ayi Jihadi. Shine ya haifi Muhammadu Dikko shi yahaifi Mallam Yakubu, Mallam Yakubu yahaifi Mallam Bello (Informant).

Shi Dikko shi Yahaifi:

(a) Abdullahi, Yakubu, Rufai, Aminatu, Khadizatu, Abdullahi.

Yakubu shi Yahaifi:

(1) Adamu (2) Muhammadu (3) Yusuf (4) Abdullahi (5) Abu (6) Maude (7) Khadizatu (8) Ibrahim (9) Aminatu (9) Bello (10) Tukur (11) Ladi.

GIDAN MARINA

ABDULKAREEM ABUBAKAR

Karofin da suka unguwan sun kai 53, Babu wanda zaice ga lokacin da akayi su.

APPENDIX 21

KAURA

Alhaji Dahiru Uba-Sarki Makera. Age 75 years. An nadashi lokachi Sarki Zazzau Shehu Idris.

SARKIN MAKERA DAGA GIDAN

Sarkin Makera Aliyu (Zamanin Ibrahim)
Sarkin Makera na maska (Zamanin Ja'afaru)
Sarkin Makera Suleman (Zamanin Aminu)
Sarkin Makera Ahmadu Zamanin Shehu
Sarkin Makera Dahiru Zamanin Shehu. Zurian wannan gidan makeran farfaru ne.
Suna kiran Azurfa da duk abinda bai shafi bakin karfe ba.

ASALIN SU

Kakaniusu larabawa ne wadan da suka zauna a Kano sannan Katsina. Daganan sukazo. Sunayen kakaninsu shine Muhammadu Sani da Dauda, suna suka zauna suka soma kira a Zaria. Watan ruwaya kuwa tace wadannan zuria na makera suna daya daga cikin tsofaffin zama a cikin kasar zazzau

RIMIN KAMBARI – IBRAHIM LADAN MAI UNGUWA.

Rimin kambari ta dauko asalinc daga lokacin da kambarawa, suka suma zama a Zaria a zamanin sarkin Zazzau kwassau. Lokacin ana yaki aka zo da su sai suka soma zama anan.

Yawan tsofaffin gidajen duk sun samu ne locacin sarki Zazzau kwassau, kamar gidan

(a) Garba dan sarki
(b) Gidan makaranta
(c) Gidan dangaladima abbas
(d) Gidan galadima salhatu. Galadima daji zamanin sarki Zazzau Ibrahim.

ANGUWAN SIRDI
ISMAILA ABUBAKAR 25-1-98
MAHAMMADU MUSA S/SIRDI – AN NADASHI LOKACIN JA'AFARU
ALHAJI HUSSAINI UMMARU – 50 YEARS.

Unguwar ta dauko Asaline saboda gidan sarakunan sirdi da yake a unguwan shi sirdi anayin sa ne da itachen gyeyya, da kashin shanu, idan aka shafe shi, sai a dinka da fata. Manyan gidaje unguwan sune, (a) Gidan Dangaladima Zubajru. (b) Gidan Birde (c) Gidan Bindiga (d) Gidan Sirdi (e) Gidan Masaka.

GIDAN SIRDI

Nan ne gidan da sarkin sirdi yake. Ita sarautan sarkin sirdi an soma bada ita ne tun daga lokacin hibe. A lokacin sarakunan habe, gidan dan wake suna suke sarautar sirdi. Bayan jihadi sai gidan sarkin sidi na yanzu suka karba, gidan ne babba wanda jama'an da ke gidajen yanzu sunyi kashi biyu dapa cikin uku na mutanen da ke unguwan. Amma sarki sidi kuma yace an soma sarutar sarki sidi ne lokacin sarki Zazzau Abdulkareem ba lokacin Habeba. Yagaji sarautar kuma ne wajen mahaifisa hamza.

Gidan Sarki Bindiga sunzo ne lokacin sarkin zazzau Abdullahi, sannan kuma suna cikin yan bindigan sarki zazzau kwassau.

GIDAN BARD

Anihin mutanen gida mutanen ningine. A lokacin da aka zo yakin Ningi Zamanin Sarki Zazzau sambo a ka kama kakanninsu a matsayin bayi. Sannan kuma lokacin Sarkin Zazzau Yero yai ma Abdullahi sarautar barde. Shi barde Abdullahi shi ya haifi Muhammadu, Muhammadu ya haifi Usman, shi kuma ya haifi Ismaila. Ismail ya haifi Abubakar. Abubakar kuma ya haifi Ismaila (informat). Wanda yake Dogarine a fadan sarki yanzu yayan sa yanzu guda uku ne (a) Fatimatu (b) Ladi (c) Abubakar.

GIDAN DANGALADIMA ZUBAURU

Anihin mai wurin a nace masa jan malamine (shine kakan musa gada gada). Abdullahi lokacin da yake sarki shine ya karbi wurin daga wurin jan malami. Daganan sai sarkin zazzau yero ya karbi wajen. Daga yero sai dan galadima zunairu. Shi zan malami yana da bayi da gida ne. ya rasu lokachin sarki zazzau kwassu ne. shi jan malami asalin sa madugu na nututnin matumin babban gwani.

GIDAN SAKA

Ba za a iya sanin lokachin da su ka zauna a unguwan ba. Amma ana kyautatan zaton cewa lokacin sarki zazzau Abdullahi ne. suna kuma daga chikin bayin sa ne sana'ar su shine yin saka ta shuruwa. Anihin mai gidan anace masa Mallam Usman. Shine ya haifi Abubakar da kanunsa Ummaru (uban Maibada Tarihi).

BABBAN GWANI

Shi Babban Gwani Muhammadu Durugu ainihinsa Mutumin Tunisiya ne. dalilin da yasa yabar Tunisiya shine saboda sha amin mulki. Kakansa M. Abdu shine ya fito daga gida ya tsaya a wani gari mai suna Shehu Talha. Yayi aure ya haifi Mallam Ali. Yana ganin a kazo za'a koma da shi dansa. Sai Mallam Abdu yace bazai samu daman komowa bi sabda amfanin da ya shuka, sai ya tura yarsa wanda take bin Mallam Ali a maimakonsa. Sai aka hadata da aure da yan uwansa.

Da kaka tayi ya sami amfanin gonersa, ya sayar, sai yayi amfani da kudin sa zuwa birnin Katsina. Bayan zuwarsa Birnin Katsina sai ya rasu yabar Mallam Ali. Shi mallam Aliyu ya sami mata ta wajen sarkin katsina, Gozo. Da wannan matan ya haifi Mallam Mikailu. Shi kuma Mallam Mikailu ya sami mata a Katsina. Katsina annan ne kuma ubangiji masa rasuwa. Mallam Kikailu yabar Katsina yazo Zaria zamanin sarkin zazzau makau. Dagananya sami labarin Shehu a Sokoto. Sai mikailu da ummarun Dallaji suka hadu a sakkwato. Bayan sun yi masa mubayaa. Bayan haka sai Shehu yace da Mallam Mikailu su koma kano. Sai Mallam Mikailu yace ma Shehu ni mai sania ai ko ina zan iya zama. Sai Shehu yace menene sanarka sai yace sanaa ta itace gini, sai shehu ya kara tambayar Mikailu wani irin gini ne. yace kamar ginin daki, da massalaci da gidaje.

Sai Sarki Musulmi Bello yasa a gina ma shehu massalachi, Ginin Hubbare zamanin shehu Muhammadu Bello. Bayan haka shine, yagina unguwar sabon gari a Sokoto.

Bayan Hubbare sai Liman Dabo na Kano yace yanason Mikailu ya gina mashi gida a Kano, Sarkin Musulmi Bello ya yarda. Bayan wannan gida a Kano sai yace yanason ya bar kano, yayi noma saboda da Damina ta samu. Liman Dabo ya ki saboda gidan shi bai Shekare ba. Shi kuma ya dage akan zai tafi shine sai yabar dansa Mahmuda, sai ya koma Sokoto.

A shekaran da aka nada Abdulkareem ya roka a bashi Mikailu ya gina masa gida Zaria. Bayan ya gama gidan (shine Takon giwa a cikin gida) sai yaroka ya barshi ya gina massalaci. Dalilin dayasa yake son a gina massalachi saboda shi mai sanyin jiki ne. bayan shekara ta zagayo sarakuna sun taru a Sokoto sai yakara tambayar sarkin Musulmi. A bashi mikailu. Sai ya yarda, da suke zo Zaria babban gwani ya gina massalachi cikin kwana daya, mutane dubu suna bashi kasa yana gini. Bayan an gama shine Abdulkareem ya duba shi sai yace masa. Babban gwani shi kuma sai yace. Allah Gafarta Mallam, a kwai wani Babban Gwani Banda Allah. Bayan da a kagama Sarkin Musulmi yazo ya buda massalachi addu'a.

Bayan Addu'ar sai Sarki Abdulkareem ya roka da a bar masa Babban Gwani, a Zaire. Shi kuma Babban Gwani yace sai dai inda zai kar masa gidansa, (wadda a lokachin

a gwai jabbone ke gidan), bayan an karbi gidansa sai, Dokjo da Jabbo yayi kara – lokachin Sarki Muhammadu Sani, cewa an kwace gidansa, shine akaba, Doko, Sayen Doko, yarika kiwo. Daganan sai aka gina ma doko gida, shi jabbo Fulani ne da ga Katsina Asalin su.

Bayan ya zauna a Zaria sai Sarki Birnin Gwari ya aiko da cewa yana son ya gina masa shigifa. Sai ya tafi ya gina ma Sarkin B/Gwari barau gida yakuma gina masa massalachi. Amma saboda kishi kada a gina ma wani irin sai Sarki Birnin Gwari yai *nufin kashe babban Gwari. Da daddare sai M. Muhammadu na Birnin Gwari yazo yagaya* na Mikailu cewa sarki zai kasheka bayan ya sallemeka. Da sa yayi, sarki B/Gwari yaba mikailu bayi, maza biyu mata hudu, keson kudi, doki da kelkendi.

Suka kama hanya suna tafiya akusa da kogin garin da akece masa damari yace masu sanka su jirashi zai yi alwalla yayi sallar walha. Daganan yatafi abinsa. Bayan yatafi wadanda zasu kashe su saka zo a lokachin ya riga yatafi. Shine takai ta binsa har Dogon Dawa tsakanin Birnin Gwari da Zazzau. Yawancin mutanen unguwan yanzu *sunacikin zurioin Mallam Mikailu ne.*

APPENDIX 21
ANGUWAR ZARIA
Mallam Dalhatu Balarabe 65 Years:-

Ita wannan un fuwar dalilin dayasa ake cemata ung uwar Zaria shine Sarkin Zazzau zai yi tafiya wadda yake unguwar Babba shine zai tafi fada ya zauna a majalisar Sariki a makofin sa. Irin Hukunce - Hukunce da Sarki zai yi shine zai yi; shine ake ce masa Sarkin Zaria.

Wanda ya fara Sarkin Zaraia shine sarki Zaria Abdulsalam, da sarautar ta tashi daganan sai sarautar ta koma Gidan Sarki zaria Haruna wanda ake ce ma gidan Baban gona. Daganan ta tashi ta koma gidan Sarki zaria yaro (Ibrahim). Da'ganan ta zo gidan Sarki Zaria Lawal (Dankumbo). Daganana sai ya koma gidan mallam yaro wanda ake ce masa Dabo (Ibrahim).

Bayan sarautar tazo lokacin turawa sai aka kashe sarautar Sarkin zaria, sai aka maida ta sarautar mai Ungwar. Da Lawal da dabo su suka soma zama masu unguwar. Bayan su kuma sai Muhammadu Ciroma sai, sai yazama mai unguwar. Zaria dagashi sai mai unguwar Ibarhim (Gidan Lawal).

Daganan kuma sai abun ya canja. Sai akayi mai unguwar guda hudu kawai a Zaria. Sai aka kashe mai unguwar sai akayi Gora, unguwowin guda hudu kuwa sune Kwarbai, kaura, Iya da Juma.

GIDAN ABDULSALAM SARKIN ZARIA

(a) Shi gidan Abdulsalam yana daga cikin tsofoffin gidan a unguwar Zaria. Da aka raba gidan an yi gidaje sama da goma filin, shi Sarki Zaria Abdulsalam yazo Zaria ne zamanin Sarkin Zazzau Abdulkareem su kuma suna cikin jama'arsa

(b) Sarkin Zarcia Haruna shi kuma yarike sarautar ne lokacin Sarkin Zazzau Abdullahi.

Sarki Zaria Yero. Sunan kakainsa shine Alhaji Baba Danbajuwa, mutumun Kano ne, yazo daga lofan Fulani. Shi Mallam Yero ya riki sarautar Sarkin Zaria zamanin Sarki Zazzau Sambo.

Yana da yaya kamar (a) Dalhatu (b) Muhammadu (c) Jibrila
Shine kuma dalhatu shine ya haifi (a) Muhammadu (b) Suleiman (c) Ibrahim
(d) Safiyatu (e) Aishatu.

Shi kuma Muhammdu shine ya haifi (a) Raliya (b) Salamatu (c) Muhammadu (d) Ahamdu.

Shi kuma Suleiman shi ya haifi (a) Bello (b) Ibrahim (c) Ummaru (d) Dalhatu (Informant) (e) Muhammdu Ibrahim shi kuma shine ya haifi Safiyatu.

TSOFOFFIN GIDAJE

Kufan iya. Salin wannan gida gidan na wadanda sakayi sarautar Madaki. Madaki Na Karshe a gidan shine Madaki kyakyarro. Bayan da akayi Jihadi shine Sarkin Zazzau Abdulkarcem ya aba Babban Dansa gidan, shi wannan dan na shine a kace masa iya Alu. Dalilin dayasa ake cema gurin nan kufin iya.

GIDAN MASU FAWA

Masu Fawa sunzo ne sun zauna Lokacin Sarkin Zazzau Sambo ne. Asalinsu sun taso ne daga mahuta kusa da kasan Giwa. Wadanda suka gina gidan sune Usman da Musa, Duk Zuriyar da suka zaune a wadannan gidaje Na sune.

(b) MUSU SAKAN SAKI

Zuriyar Gidan Asalinsu Mutanen Hadeja ne. Suna daga cikin Jamar Iya Alu ne. Wanda yazo a nace masa Muhammadu Fari, ya Hadu da iya Alu a lokacin shina Almajirine. Shi Iya Alu shine ya zaunad dashi anan unguwar yana kuma tukmka mashi igiya na daurin dawaki.
A zamanin da Iya yake mulkin sa.

Cikin yayan Muhamadu fari akwai (a) Jibrin (b) Musa (c) Abdurrahman (d) Aliyu (e) Hindatu (f) Musa.

1. Shi Jibrin yana da yayanshi kamar su (a) Rilwanu (b) Dudu (c) Ibrahim (d) Aminatu (mother of the informant).
2. Shi Musa yana da yaya kamar (a) Muhammadu (b) Usman (c) Khalilu (d) Ahmadu Tijjani.
3. Shi kumar Abdurrahman yana da yaya kamar su Aliyu, Asharu da Asabe.

4. Aliyu shi kuma yana da yaya kamar su Ahmadu Rufa'i da Hauwalu.

Wadan nan gidaje sune sukeyin Regar saki baki.

MANYAN MALAMAI

Malam Tafida shi kuma Fulani ne daga Katsina ya zama kasaitaccen Malami ne, lokacin Sarkin Zazzau Sambo. Gidan ana ce ma sa gidan makaranta, a halin yanzu.

GIDAN MALLAM ALHAJI

Yanzu anacema gidan gidan Mallam Muhammadu shi dan Mallam Alhaji ne, zamanin da ya shahara shine zamanin Sarkin Zazzau Alu. An taba ce masa za'a yi masa muhuti ya gudu saboda baya so.

MALLAM FATE

Shi Mallam Fate lokacin da ya shahara shine lokacin Sarkin Zazzau Alu ne.

KOFAR JATAU

Yadda wani labari yace shine akwai wani Sarkin Zazzau anace na sa Jatau gidanshi yana ana bayan wata Itaciyar Bakko, kufan gidan Sarkin Kofa kenan.

Amma kuma ciroman Zazzau yace lokacin Sarkin Zazzau Jatau shine yaba da yammata guda biyu aka rufe kofa dasu, wanda ya sa kofa ta tsaya. Saboda haka, a ke cewa kofan Jatau.

Kusa da kofan Jatau akwai wata kofa da ake ce mata kofar Matarkwasa. Tarihinta na cewa idan aka gina ta sai ta Rushe. Da aka tambayeta, sai tace Ita bazata tsaya ba sai an bata dan Sarki. Saboda haka sai aka rufeta bayan jihadi. Ita a matarkwasa aljanna ce fara. Ita a wannan kofa tannan da kwarkwamai har yanzu.

ANGUWAR FATIKA

Alhaji Adamu Aliyu. Age 70 Years.

Wanda ya kafa wannan unguwar wani Hakimi ne da yake mulkin garin fatika lokacin Habe. Yanzu gidan wannan Sarkin na fatika ya zama kufai.

A cikin Tsofaffin gidajen da aka kafa bayan Jihadi shine akwai gidan Sarkin Shanu Adamu.

GIDAN SARKIN SHANU ADAMU

Ainihin wannan gidan na Sarkin Shanu Adamu ne, anyi masa sarautar ne zamanin Sarkin Zazzau Kwassau. Daga Katsina ya taso da bayinsa da shanun sa, da tumakansa. Sai ya zauna a Hunkuyi (Gidan Tsamiya). Daganan sai ya matsa zuwa kyaure duk gonakinsa anan suke, shi Mallam Adamu ya haifi ya'ya'guda biyu ne da Halilu da Abubakar.

Abubakar Dan Mallam Adamu, ya auri yar wajen Sa'i Dalhatu ne. Bayan auren ta Sai Dalhatu sai yabashi wannan gida. Bayan an bashi gida, sai ya kasance yana zuwa cikin birnin Zaria yayi kwana bakwai sannan sai ya koma. Daga baya lokacin Sarkin Zazzau Kwassau sai ya taso ya dawo cikin Zaria.

Shi Abubakar ya haifi ya'ya'kamar Aliyu Karinmatu, Kande (Halilu), Aliyu, Adamu, Muhammadu Bello, Hawwa'u, Hannatu, Ibrahim.

Sauran Tsofaffin Gidaje a unguwan shine Gidan Joje, Gidan Salenke, da gidan Dikicon Rimi.

GIDAN JOJE YUSUF ADAMU (10-2-1998)70 YEARS.

Wanda ya kafa gidan Joje shine Mallam Adamu. Yana kuma daga cikin Jama'ar Iya Alu ne. She kuma Iya Alu dan Sarkin Zazzau Abdulkareem ne. Su zuriyar gidan Joje sun taso ne daga Dutse Gadawur cikin kasar Kano. Sanarsa itace karatu. Yana da yaya guda goma. Biyar mata da kuma biyar maza. Sune kamar su (a) Isiyaku (b) Usmani (c) Yusuf (d) Hamza (e) Dalhatu cikin mata kuma akwai (a) Fadimatu (b) Lami (c) Lanti (d) Gude (f) Kande. Akwai kuma malamai a unguwar kamar su Mallam Bello, Mallam Hudu, Mallam Abubakar, Mallam Namadu.

Mallam Bello

Yayi karatu ne lokacin Sarkin Zazzau Ibrahim da Ja'afaru. Yayi karatu a kerkashin Mallam Yahuza da Mallam Hudu. Mallam Bello ya fito daga cikin gidan Mikailu ne.

Mallam Abubakar

Mallam Abubakar mutumin Fatika ne yazo da karatunshi ne lokacin Sarkin Zazzau Ibrahim shie yagina gadan.

Mallam Mahmuda

Shi Mallam Mahmuda shine ya zauna agidan sunan ubansa Mallam Alhaji, shi Mallam Mahmuda shi ya kaifi Mallam Dangoma. Ya kuma kasaita ne lokacin Sarkin Zazzau Ibrahim zuwa Ja'afaru.

RIMIN DANZA

GIDAN KIRA

Ibrahim Abdullahi. 120 years 11-2-1998.

Tun farko kakaninsu ba'a anan suke ba sunzone. Kafin zuwan su Zaria babu sana'an guda uku. Sune (a) Kira (b) Saran Kofatan Dawaki (c) Ba Sankira. Lokacin Sarkin Zazzau Abdulkareem sai ya aika wajen Sarkin Katsina cewa yana son wadannan mutane. Sai aka zo da kakaninsu daga Katsina. Da sukazo sai akace a zo da su nan unguwar. Wadanda su kazo daga Katsina sune (a) Abdullahi da Kerau.

Kerau shi ya haifi

(a) Abdullahi (b) Bawa (c) Ladi.

Yayan Abdullahi kuwa sune

(a) Fimata (b) Bature (c) Ibrahim (d) Yaryaya.

Shi Abdullahi, ya tashi yabar unguwar, yaje ya zauna a wani gari a Saminaka daga nan sai yadawo suka zauna a Palladan.

Sanaar su itace kira. Inda kuwa suke samun fama shine garin Kuriga da kauyen Tami.

Aliyu Abdu 55 Years

Haruna Abubakar 50 years 6-3-1998.

Riman Danza

Ta dauko suna ne saboda akwai wata Rimi da ta taso daga Danza aka wayi gari aka ganta a unguwar. Su gidan Makeran Unguwar sunzo ne daga Katsina lokacin Sarkin Zazzau Kwassau. Abinda yataso dasu kuwa daga Katsina shine kira. Wanda suka taso daga Katsina akwai (1) Mamman (2) Ibrahim (3) Tanko.

1) Mamman Yayansa (a) Abu (b) Abdu (c) Nuhu (d) Labaran.

2) Ibrahim (a) Ladan (b) Danwada (c) Hauwa (d) Salamatu.

3) Tanko (a) Yayya.

Jikokin Mamman ta wajen Abu (a) Ali (b) Haruna (c) Mailafiya (d) Ibrahim (e) Mairo (f) Shehu (g) Amina.

Jikokin Mamman ta wajen Abdu (a) Magaji (Abubakar) Sule (b) Danlami (c) Tanimu (d) Ma'niwa

Jikokin Mamman ta wajen Dalhatu (a) Laraba (b) Rakiya (c) Hajara (d) Dangude (e) Dije (f) Ladidi (g) Aishatu (h) Shaibu (i) Labaran.

Nuhu - Ummaru, Sani, Ladi, Uwaliya

Labaran - Hamidu, Rakiya, Gashi, Aminatu, Audi.

IBRAHIM

LADAN - Abdullahi, Ahmadu, Ubaliya, Habibatu, Saratu, Uwaliya, Salamatu, Rakiya.

Dan Wada - Ahmadu, Lawal, Dukkan su suna zaune unguwar ne.

APPENDIX 23

ANGUWAN IYA

Abdulazeez Balarabe 84 Years

Mai Unguwa Dauda 85 Years.

Ita dai Anguwan Iya ta faro ne a lokacin Iya Muhammadu Hankarau. Shi Kuwa Iya Muhammadu Hankurau yana daya daya mallamai wanda suka zo Zaria daga Katsina tare da Sarkin Zazzau Mallam Musa. To a lokacin da Sarkin Zazzau Mallam Musa yake nada sarautu sai Mallam Mughammadu Hankarau yace akwai wata sarauta ta wata yar sarki mai arziki a kudaru sunanta Iya to shi wannan sarauta yake so a ba shi. To a lokacin nan sarkin Zazzau Musa yace masa Haba Mallam Hammammadu yaya zaka amshi sarauta ta mace kace kana so bayan ga sarauta kala kala. Sai shi Mallam Muhammadu yace shi dai wannan sarauta yake so. Kuma ya hakura da ita. Dalilin kenan da ake kiransa Iya Hankurau; sobada cewa da yayi ya hakura da wannan sarauta. Shi Iya Mallam Muhammadu ba inda yafara zama sai nan anguwan iya. Ainihi gidan sa kuwa da gidan wani arne ne wai shi Sarkin Noma Mutumin yana da arziki sossai. To sai suka kore shi ya zauna gidan kusan duk Anguwan Iya tana cikin gida sa ne. Iya Mohammadu Hankriu yana da girma a birinin Zaria domin kuwa tun daga anguwan Iya har zuwa kwaba duk suna karkashin sa ne. Hasali ma babban dansa Lamido shine ya kafa kwaba ya koma can da zama wanda a har yanzu dangainsa suna zaune a kwaba. Iya Muhammadu Hankurau yana da yaya masu yawa daga cikin su akwai Lamido wanda ya haifi Fate Rufai da Nuhu. Akwai kuma Iya Abdul Aziz wanda ya gaji Muhammadu Hankarau. Bayan Abdulazeez ba a sake yin Iya ba sai lokacin Sarkin Zazzau Ibrahim inda ya nada Muhammadu Bello a iya. Shi ko Muhammadu Bello dan kanin Abdulazeed ne.

Wani abu kuwa shi ita sarauta Iya ta anguwan Iya ba Iyan gari bane. Ita wannan sarauta dai ta Iya ance da ita Iyan kurama ce.

Muhammadu Hankarau yana da yaya kamar su (1) Makaman Iya Ibrahim (2) Iya Abdul Azeez (3) Lamido (4) Sidi (5) Yakubu (6) Musa (7) Baban Bakko (8) Galadima Suleman (9) Iya Abdullahi.

Makaman Iya Ibrahim shine ya haifi (1) Baban Alhaji (2) Musa.

Abdul Azeez (Iya) shi kuma shine ya haifi makaman Iya Adamu (2) Madakin Iya (3) Turakin Iya.

Lamido shine ya haifi (1) Aliyu (2) Nuhu.

Sidi bai haifu ba.

Musa shi ya haifi Aliyu da Yakubu.

Suleiman shine ya haifi Mohammed Bello (2) Yaro (3) Dalhatu (4) Goma.

Bayan Iya Hankarau ya rasu wanda ya gajeshi shine Iya Abdulazeez lokacin Sarkin Zazzau Sambo sai kuma iya Abdullahi yayi sarauta ne zamanin Alu dan Sidi ne. Bayan iya Abdullahi sai Muhammadu Bello wanda a ke kira Kwassau shine yake rike da Zaria da kewaye kamar sarautar Dan Madami a yanzu, yayi lokacin Sarkin Zazzau Ibrahim ne. Bayan shi ba sake yin Iya ba sai dai Marafa shi kuwa Marafa Jika iya Abdullahi ne.

APPENDIX 24

KOFAN KUYAM BANA

Abdullahi Hayatu age 63 years

Tosfaffin gidaje a unguwan sune

(a) Gidan Gimbiya yar Sarki.

(b) Gidan Falken gonja

(c) Gidan Sarkin Malamai

(d) Gidan Mallam Habu.

GIDAN MALLAM HABU

Asalmsu muanen wajen Sokoto ne. Sunan mai gidan Mallam Mohammadu Sambo, yayi karatu a makaranta daya da Shehu Dan Fodio. Kafin ayi Jihadi ya kan zo Zaria yana koyar da karatu. Idan ya zo ya kan sauka ne a gidan Limamin kona daga baya yazo ya zauna a cikin Zaria, lokacin da ya zo ya soma zama ne a Limanchin kona. Amma da kasuwa ta matso kusa da gidan shi sai yaji tsoron kada yayan shi su kiyin karatu sabo da haka sai ya koma kofan kuyambana cikin yaya Mallam Sambo akwai (a) Mallam Rashidu (b) Mallam Muhammadu Mazawaje (c) Mallam Abubakar (d) Mallam Abdulrahaman Sayudi (e) Hammadu (f) Bukhari Akwai kuma mata kamar su khadizatu (Goggon Bakin kasuwa) da Salahatu (Goggon madaka).

Shi kuma Mallam Rashidu ya haifi (a) Hamada (b) Maliki (c) Saidu (d) Habibu (e) Mal. (f) Shua'ibu. Shi kuma Mallam Muhammadu Mazawaje shi ya haifi (a) Mohammadu Lawal (b) Muhammadu Sani (c) Jabiru (d) Mallam Bashiru (e) Baba Waihi (Sambo (g) Muhtasibu

Dukkansu kuma suna da yaya da jikoki.

GIDAN SARKIN MALAMAI

Ainihinsu Fulani daga waje sokoto, sunzo ne Zaria lokacin Sarkin Zazzau kwassau, kakan su da yazo ana cemasa Muhammadu. Shi Muhammadu yana da yaya guda uku (a) Dan Takko (b) Dandaba (c) Abdu Mai munku. Shi Dantako yana da yaya kamar su (a) Maiwada Bello. Shi kuma Dandaba yayansa sune (1) Abu, (2) Dabo, (3) Zubairu. Sannan kuma yayan Abdullahi sune (1) Dije, (2) Lawal (3) Hashinimu (4) Isiyaku yasoma zamana gidan Limamin kona. Daga baya, yazo ya zauna a cikin Zaria, kafin a yi Jihadi. Lokachin da ya zo ya soma zama ne a kusa da Imaidin kona amina da kasuwa ta matso kusa da gidanshi sai yaji tsoron kada yayan shi su kiyin karatu saboda haka sai yakoma kofan kuyambana cikin yayan Mallam Sambo akwai (a) Mallam Rashidu (b) Mallam Muhammadu Mazawyi (c) Mallam Abubakar (d) Mallam Abduralman Sayadi (e) Hammadu (f) Bukhari. Akwai kuma mata kamar su Khadizatu (Goggon Bakin kasuwa) da Salihatu (Guggon Madaki).

Shi kuma Mallam Rashidu ya haifi (a) Hamida (b)Maliki (c) Saidu (d) Habibu (e) Mal. (f) Shuaibu. Shi kuma Mallam Muhammadu Mazwaje shi ya haifi (a) Mohammadu Lawal (b) Muhammadu Sani (c) Jabiru (d) Mallam Bashiru (e) Bala Waihi (f) Sambo (g) Muhtasibu.
Dukkan su kuma suna da yaya da Jikoki

SAI GIDAN FALKEN GONJA: see main text.
Babbu sanar mutanen unguwan shine karatu noma da kuma ferra.

Sauran Unguwoyi kanar su unguwan Mallam Sule da Dan Jinjiri an samu su ne bayan Jihadi. A unguwan Mallam Sule akwai tsofifi gidaje kamar:
(a) Gidan Mallam Sule
(b) Gidan Yarbawa.

Shi Mallam Sule Babba Malami ne wanda yazo Zaria lokacin Sarki Zazzau Yaro. Sannan kuma yarbawa sun soma Zaria ne zamanin Sarkin Zazzau Abdullahi (bayan ya sake dawowa) adnda ya soma zuwa ana cemasa Balogun. Yazo shi kadai sannan yakuma ya sake komowa yazo da iyalansa. Yanzu tattaba kunnensa ne a unguwan. Sun zo ne suna sayarda fatanchi, zannuwa da goro su sayar su koma.

Shi kuma Anguwa Dan Jinjiri ya samu ne saboda zaman wani Sharifi a gidan zamanin Sarkin Zazzau Yaro.

APPENDIX 25

ANGUWAR KOFAR DOKA (YUSUF ALIYU KOFAR DOKA)

Ita wannan unguwa tasamu ne saboda kofar ganuwa, wanda take kusa da unguwan. It wannan kofar an sameta suna kofar doka, sabo da dalilai guda biyu. Nafarko shi ne kusa da kofar akwai Itacen doka a wajen.

Nabiyu kuwa shine sabo da kofa ce da take da tsaro domin ba a yarda wani yashigo bayar isha ba. Tana da mai gadi wanda aka ajiye don yayi gadin wannan kofa .Shi maigadin kofar doka yana daya daga chikin jarumai yar sarki Zazzau Bakwa wanda akece mata Zaria. Da suka zo zaria shi akabai tsaron kare garin daga fuskar Arewa yana da bayi wandanda suke taimaka masa yin wannan aiki na tsaro. Zuriyar gidan doka yanzu basu, sunkare. Amma kufan gidan shine wanda akayi Primary na jushi a wurin. Dalilin da yasa kuwa zuriyansa basa nan sabodda yawancisu babannine.

Bayan Jihadi an samu karuwar jama'a, a unguwar kamar su gidan kakanni mallam Ja'afaru driver wadanda ba a san in da su ka zoba. Da kuma zuriyar mallam Sani.

Shi Mallam Sani suna daga cikin Zuriyar ko kuma mutanen Shehu Usman Dan Fodio, sunzo lokacin da aka yi jihadi.

Daganan kuma sai gidan yari jabbuje shi kuma mai tsaron Sarkin zazzau Abubakar ne, wato dogari ne, su Asalinsu zabermawa ne wadan da sukazo zamanin Mulkin sarkin Zazzau Abubakar.

Danganin kuma sai gidan Sarkin Zazzau Abubakar, gidansa shine inda Prison na yanzu yake, asalin filin kuwa filine na Sarkin Zazzau Sidi Abdulqadir bayan da ya rasu sai Sarkin Zazzau Abubakar ya mallaki filin, zuriyar Sarki Zazzau Abubakar sunanan a kofar doka a halin yanzu.

TARIHIN GIDAN MAI UNGUWA

Bayan wannan sai gidan Ummaru, shi yayi zamani da Sarki zazzau Abubakar ne matsayin majidadin da. Shi Ummaru yazo Zaria tun lokacin Sarki Zazzau sidi ne daga Borno a yawonsa na fatauchi, yauri Amina daga Lokoja, sune suka zauna Agidan Sarki :aka haifi Hassan, ya haifi Aliyu, da Muazu. Hassan shi kuma ya haifi mai unguwa na yanzu, da muazu na biyu da Qassimu. Har yanzu Zuriyar mutanen su nan. Daga cikin zuriyar sune a yanzu aka sami mai unguwa na yanzu.

ALLAM IBRAHIM (YARO) ABUBAKAR.

57, KOFAR DOKA, GIDAN Mallam Sani.

Shi Mallam Sani Dan Mallam Rilwanu ne. shi kuma Mallam Rilwanu dan Mallam Ummaru, Shi Ummaru dan Mallam Dattiya ne, shi kuma Mallam Dattiya Dan Mallam Ahmadu ne.

Asalinsu mutanen yandoto ne, Daganan suka taso zuwa kasar hunkuyi suna kiwda noma da karatu. A Hunkuyi aka haifi Mallam Dattiya. Akwai sauran yaya mata da kanne na Mallam Dattiya guda uku wadanda sukayi aure a kauyukan Hunkuyi, sun zauna a Hunkuyi da misalin kamar shekara hudu a kayi jihadi, Shehu Usman Dan fodio.

Saboda jihadi ta wajen bada ilmi da Mallam Ahmadu yakeyi, a hunkuyi yasa Sarkin Zazzau Mallam Musa ya kira Mallam Ahmadu da yashigo cikin Birnin Zaria don ya cigaba dabada ilmi. Bayan da suka shigo kofar Doka anan ne a ka haifi Mallam Ummaru. Shi kuma Mallam Ummaru shi ne yazama Babban Mallami kwarai da gaske Yayan Mallam Ummaru sune (a) Mallam Sani (b) Maryamu (Uwan Mallam Abba), (c) Da Mallam aminu (d) Mallam Bello. Akwai mata guda uku sun mutu. Amma kafin su mutu sun bar ya'ya wanda suma Zariyar na su ta kare. Mallam, Aminu shima yazama Mallami yayi ta karantaswa. Mallam Aminu bayan lokacin kankune ya tashi daga Zaria ya koma kauyen Rahama wadda take wajen Dambo. Dalili da yasa ya tashi shine saboda rikicin shugabanci ta waje tafsiri Bayan lokaci kankane sai kuma ya sake Daw wa, Bayan Rasuwar mallam Abdurrahman.

Sahi Mallam Sani Babban Mallami ne Lokacin da yasoma wayo, ya soma karatu a gidan su ne, daga nan sai yatafi Gwandu, yayi shekara kamar tara yana neman ilimi, lokacin da ya dawo sai ya tarar da mahaifinsa ya rasu, saboda haka sai yace duk wani mai neman ilimi yazo. Sai ya zauna yayi ta karantaswa. Manyan Almajiransa sune kamar Mallam Naiya, Mallam yahuza, Mallam Abdurahman, Mallam Sani (Babban Dodo). Mallam Sani yayi zamani lokacin sarkin Zazzau kwassau, Aliyu Dansaidi, har zuwa Ibrahim da Ja'afaru. Shine kuma zamaninsa yake Tafsiri a massalachin Juma'a. Kafin ya yarda yayi tafsiri sai da yakafa dokoki ko Hujjoji guda uku.

1. Idan antashi daga tafsiri ba zaije fada ba, ya gaida Sarki.
2. Bakuma zai jira Sarki ba zai soma tafsirin sa
3. Sannan kuma ko akwai mai tambaya, saidai yabiyo shi gida yayi masa tambaya. Shi Mallam Sani ya shahara wajen karatun Tafsiri, Mandiqi, Nahawu, bada'I an ce ma, shi Mallam Ahmadu shine yazo da Nahawu da tafsiri a Zaria. Sanna kuma yayi kari wajen Ilmi fiqh.

Mallam Sani yana da yaya guda uku. Mallam Kasimu, da mallam Abubakar, da Mallam Ummaru, Sannan kuma yana da yaya mata sune Hannatu, Shema'u da Binta. Mallam Kasimu yanada ya mace mata Hauwa tana da rai. Ita ta auri Alhaji yero mai icce yana tadun wada. Mallam Abubakar yana da yaya, da Bello, da Sani da Aminu da ibrahim da kuma mace Rabiatu. Mallam Ummaru shine Karaminsu, wands ya rasu kamar shekara biyar da suka wuce. Yayan Mallam sune Alhaji Saadi, Gude, akwai Hari, akwai Jami.

Suna da katon goma wanda ya soma tundaga albarka cinema na tudun wada har zuwa tudun jukun.

ADAMU SHITU

Age 70 years, Kofan Doka Gidan Tafarki

Kakan Mallam Adamu shine Dikko, shi mutumin Kano ne, cikin Birin Kano, Hamayya ta sarautar ta taso dashi Kano, kafin ayi Jihadi wajen shekara dari da Hamsin Da ya iso Zaria ya bakunci Sarki na wannan zamani, da yazo sai zama bata yi dadi ba, sai yace zai koma yayi noma. Sai yadawo ya zauna a gidan Sarkin Kofa, a kofar Doka, Daga nan ya tashi ya yanki daji bayan jihadi tundaga Tudun wada har kakeyi zuwa Anguwar mai gwado da shi da yayansa da bayinsa suka mai da shi gonaki.

Shi Mallam Dikko ya mutu yabar yaya guda goma sha Bakwai sunan wasu daga cikin su, shine (1) Dahiru (Babban da) (2) Ibrahim (3) Ummaru, (4) Mai Dawa (5) Soda (6) Shittu (7) Shittu. Akwai mata (8) Gwaggon Magajiya (9) Juma (10) Ramatu (11) Aishatu (12) Mai muna (13) Muazu (wanda ya zama tafarkin).

Lokacin Sarkin Zazzau Alu aka auna filayen gonakin su a ka mai dashi barikin sojoji. Da wurin duk gonakin su ne. idan lokacin damina yayi sukan tafi can suyi noma, anacema wurin Danduwa, Bayan a karbi filin wan mahaifin su ana cemasa Ibrahim yaki dawowa.

Shi Mallam Ibrahim yana daya cikin wadanda suka kafa anguwar mai gwado Ita mai gwodo yar borice. Alokacin ana borine a wajen dare da rane. Da rasuwar Mallam Dikko yanzu zai yi Shekare dari.

Daga chikin yayansa Muazu shine ya rike saruta. Sarautar kuwa Itace ta Tafarki ya riki wannan sarauta ne zamanin Sarkin Zazzau kwassau.

Ma anar tafarki shine idan sarki zaiyi rangadi, shi tafarki zar daura sirdi ya tafi garin da sarki zai tafi, Idan yatafi sai yagaya ma sarkin ko hakimin gari cewa sarki yana zuwa rana kaza, a shirya ma sarki wuri da Jama'ar sa.

Yana cikin wannan aiki ne har turawa sukazo. A lokacin yara ake badawa suna aikin hanya. Shi tafarki shine yake shugaban cin su. Bayan an soma Hanya, Turawa suka zauna a Kaduna, shine yazama Jekada tsakanin sarki da Tafarki

Kafin ya rasu shi tafarki yan da yaya guda biyar mata guda biyu maza guda uku, mace ta farko anace mata gyato suna dada guda daya na cema sa, Ibrahim wawo. Yayi sojan Hitler, tayan yayi dan doka. Kaduna to yi aure a kofan Tukur-Tukur, yayanta mata guda biyu. Babban da Muhammadu, sai maria sai kuma kulu.

Dalhatu ya haifi yaya guda biyu (1) Shehu (2) Lawali Dahiru Ya mutu ya bar yayan shi guda biyu da sambo da shuaibu. Shi sambo yana da da guda daya ana ce masa Abdulqadir. Da kanwarsa ana ce mata Ayya. Sani kuma Abdulqadir yana da yaya maza

biyar da Atu ba aisha (3) Alhaji Tambaya (4) Shaibu (5) Isyaku (6) Garba da kuma Adamu. Sai mata guda uku.

Maidawa. Ya mutu yabar dansa guda daya ana kiransa Usamanu, Bature yana da yaya maza hudu da mata biyu. Babban khalilu (2) Isah, died (3) Alhaji Audu (4) sai ali matan kuwa sune (Anguwau Doya) Ummaru (Babban kaka) yana da mace daya maza uku (1) Yakubu (2) Yusufu (3) Hamza (4) Kubi.

Shittu ya rasu yana yaya guda bakwai maza shida mata biyu (1) Danlami (2) Abubakar, (3) azumi (4) Yarmaidawo (50 Adamu (6) Nuhu Shittu (shugaban yan taxi) (7)Jummai (8) Halliru Zuriyar Wannan gida basu da wata sana'a sai noma.

Shi Mallam Dikko da ya yazo Zaria yazo da kaninsa guda day anacema shi Alu Gambo. D ganan shi kuma ya koma Gyallesu.

GIDAN GOBIRAWA

Bayan wanna gidan a kwai kuma gidan Gobarawa. Shi Maigidan ya rasu yabar yayansa guda hudu mayayaki, Barau, Abdullahi, Dan mama da kuma mace yayya. Wannan a gida shine yana daya daga chikin tsoffin Gidaje

APPENDIX 26

ANGUWAN DAN MADAMI DALHATU YARO 29TH APRIL 1998

Anguwan Dan Madami ana kiranta Unguwan. Dan Madamin Dalitu Dan Madamin Muhammadu. Shi kuwa Dan Madami Muhammadu ubansa yazo Zaria ne tare da Sarkin Zazzau Abdulkareem. Mallami ne wanda suka karbo Tuta daga Usman Dan Fodio. Yana da kane nda ake ce masa mai unguwan Yunusa wanda suka zauna tare dashi a gida gida. An baiwa da Madami sarauta a zamanin Sarkin Zazzau Alu Dan Sidi ne. Dan Madami Muhammadu yana da yaya da yawa daga cikin yayansa akwai Maaji Yaro wanda akayi wa Ma'aji a lokacin Sarkin Zazzau Ibrahim. Kuma sai Zazzau Ibrahim ya raba gidan biyu ya baiwa Ma'aji Yero rabi. Dagacikin mutanen da suka zo Zazzau da su Dan Madami Muhammadu sun hada da gida Sa'i Mazadu da kuma gidan Galadima iya da kuma gidan fadan fada. A halin yanzu ma akwai Dangataka tsakanin gida Sa'i Mazadu da Galadiman Iya. Domin kuwa kanin Dan Madami Muhammadu wato mai unguwan Yunusa ya aure jikan Alhaji Musa, wato kakan sai Mazadu. Sidi Dan Madami Muhammadu tunda sukazo Zaria ba inda suka fara zoma sai unguwan. Dan Madami kuma tunda Dan Madami Muhammadu Allah yayi masa sarautar ba a sake yin sarautar Dan Madamin a gidan ba. Amma dansa Yaro yayi Maaji lokacin Sarkin Zazzau Ibrahim. A lokacin da sukazo anguwan akwai tsofafin gidaje suka samu. Daga cikin gidajen akwai gidan Sa'i Mazadu wanda an gina gidan tun kafin ayi gihadi da kuma fada fada da kuma gidan Alhazawa.

YAYAN DAN MADAMI MUHAMMADU

(1) Barau (2) Dalhatu (3) Ahmadu Dado (4) Yero (5) Idi (6) Mowa (7) Nana.

1. Barau - Mamuda Jamo
2. Dalhatu - Zubairu Maude
3. Amadu - Godiya Mohammadu Hajare
4. Ma'aji Yero - Amffana Sambo Dalhatu Sani, Nana
5. Idi - Bai da da
6. Mowa - Karimatu Yusuf

7. Nana - Bata da

Yunusa Mai Unguwan shine ya hada Mallam Shehu, M.G. Ibrahim, Muhammadu Jabba, Hajiya, Dauda da Magajiya.

GIDAN GALADIMAN IYA, MAI UNGUWAN MAIWADA

Asalin kakaninsu sun zo ne tare da Sarkin Zazzau Abdulkareem a matsayin malamai ne, kuma suna noma suna kiwo, kakan nasu kuwa shine Muhammadu Sani. Uban Muhammadu Sani kuwa shine Ibrahim Sarkin Dawaki wanda yayi Sarkin Dawaki lokacin Abdukareem.

Yayan Muhammadu Sani kuwa sune:

(1) Musa (2) Sulemanu (3) Halimatu (4) Lawal (5) Umaru (6) Mohammadu Bello (&) Yakubu (8) Ibrahim (9) Hafsatu (10) Ummai (11) Hadiyatu (12) Mano (13) Asma'u (14) Aminatu (15) Hafsatu (16) Fatimatu.

GIDAN SA'I MAZADU

Alhaji Musa kaka yake a wajen Sa'i Mazadu. Shi kuma Alhaji Musa yana daya daga cikin mutanen da Shehu Usman Dan Fodio ya turo su da suyi Jihadi.

Bayan anyi Jihadi yana daya daga cikin mamyan gari masu bada shawara. Ya soma rike Keffi, Doma da kuma Nassarawa. Sarautar Sa'i soma ne lokacin Sarkin Jaafaru a gidan.

GIDAN ALHAZAWA:

Mohammed Ani (Alhaji Doyara) Age 72.

Su dai sun zo ne daga Katsina. Asalinsu mutanen Kurkujan ne. Zamanin Sarkin Zazzau Kwassau suka iso Zaria. Suna koyarwa. Idan zaayi saukan karatu, shi Sarki ya kanzo da kansha tare da Sarkin Ladanai zuwa gidan. Aminhin mai gidan shine Alhaji Mallam Yahaya, Sa'i Alhaji Mallam Hailiru Sai Alhaji, Mallam Mallam Halliru, Sai Alhaji Mallam Iyal, Alhaji Mallam Tajo, Alhaji Mallam Tajo.

Abinda yasa akece masu Alhazawa shine dukansu sun tafi Macca ne a lokacin guda Mazansu da Matgan su.

GIDAN SHARIFAI

SARKIN SHARIFAI Salihu Isa

Sharifai Isa Balarabe ne mutumin liyar ne Saudi Arabia. Yana da Alaka da gidan sarauta acan. Ya bar Saudi alokacin da aka kama Ahalil Baiti ana yankawa. Ya bar kasan ya zo Barno, daga Barno yazo Kano. A ka karbe shi a Kano da gimamawa. Ganin girmama mashi da akayi ya ga zai sa shi ya rabu da Allah, sai yaga bai kyautu ya zauna a Kano ba, sai ya bar Kano yaje Katsina. A Katsina sai yaga Girmamawan tayi dai dai data Kano. Nan ma sai ya barsu ya zo Zazzau. Yazo Zaria a lokacin Sarkin Zazzau Abdulkareem ne. Sarkin Zazzau Abdulkareem ya karbe shi da hannun dama. Amma galibin mutane Zaria ba su karbe kamar yadda a ka karbe shi a Kano da Katsina ba. Galibin mutanen Zaria suna cemasa Nasara ne wasu kuma suna cemasa yahudu ne. Ganin wannan hassada sai ya ce a Zaria yaga wurin zama. Yayi Aurensa a Zaria ya haifi dansa Sharif Ibrahim. Sharif Ibrahim ya haifi yayan sa guda uku.

(a) Sharifi Salihu (b) Sharifi Hamza (c) Sayyada Fatimatu. Sharifi Salihu shine ya haifi Sharifi Isa wanda yake shine Sarkin Sharifai Zazzau ne yanzu.

SANAR SU

Sharifi Isa shi dai falke ne yana zuwa fatauchi ne kasashe kasashe. Ya saya ya sayar. Haka kuma yana dinki da gini. Wannan shine sanaar gidan tun daga zamanin Sharifi Ibrahim domin su basu zuwa gidan kowa sukai karan Allah wajen shi.

Shi Sharifi mutum ne wanda Allah ya bashi wani Muzoza wanda wuta bata kama su. Wannan Muiji za sun gaje ta ne daga kakansu Annabi Muhammadu. Saboda wannan mu'jizza ya sa suke cikin fadan sarki.

GIDAN BANBADAWA

Sun zo ne daga Katsina ne lokacin Sarki Zazzau Abdulkareem, wanda yazo shine Alhassan. Shi Sarki Banbadawa ne. Da yazo ya zauna ne a gidan Sarkin Zazzau Abdulkareem lokacin da akayi masa sarautar Sarkin Zazzau sai ya komo nan gidan. Daganan sai dansa C'indo. Sai kuma danshi Gambo. Bayan Sarkin Banbadawa Gambo said akayi Sarkin Banbadawa Dagazau. Daganan sai Sarkin Banbadawa Sule. Daganan sai Sarkin Banbadawa Gambo. Daganan sai Sarkin Banbadawa Aminu Zamanin Sarkin Zazzau Shehu Idris.

Banbadanci dai roko ne wanda ake ma Fulani da kuma sarakuna. Anayin Banbadanci da kalmar Fillanci ne. Bayan wannan, mutanen gidan kuma suna yin tukwane, murhu, kwantanniya, kaskon wuta da tuku da randan ruwa, da butoci da sauransu.

GIDAN FADAN FADA

Mallam Isa 80 years

Kafin ayi Jihadi wannan gidan Alkaline. Mallam Musa (Sarkin Zazzau) Kuma ya na zuwa gidan ya zauna yana yin Na mutane tsibbu da Addu'a. Manyar mutane suna zuwa don Mallam Musa yabasu magani.

Shi fadan fada shine ya rike ma Mallam Musa tuta lokacin da akayi Jihadi daga Kano zuwa Zaria. Bayan anyi Jihadi shine aka ba fadan fada wannan gidan wanda yawancin Anguwan suna cikin gidan ne.

Shi fadan fada Asalin sa Mutumin Kano ne. Shi Mutum ne Babba yana rike kuma da wani gari a Kano. Sunansa shine Musa. Bayan ya rasu lokacin sarkin zazzau Musa, sai a kaba kanin shi Isa Sarautar fadan fada. Shi kuma Isa shi yi hafi yaya gida hudu (a) Ali (b) Shehu (c) Shukura (d) Ibrahim shi kuma Mallam Ibrahim shine ya haifi Mallam Musa, Mallam Musa shine ya haifi Isa (informant).

APPENDIX 27
ANGUWAN ALKALI
USMAN BURSAR AGE 58

Anguwan ta samo aslaine daga alakalin da a ka samu a engin. Bayan anyi Jihadi kafin Jihadi ma ana ce anguwa Karsina wa.

Alkali Abubakar Manga shine alkali na farko a Zaria shi kuma mutumin birnin Katsina ne. Sarki Zazzau Abdulareem yace ma Sarki Katsina a bashi wanda zai masa Alkalanci. Da kyar ya yarda yazo Zaria don yayi Alkalanci shi wannan Sharraran Alkali ya roki Allah kada wani cikin Zuriyarsa yayi Alkali. Kada kuma yarsa ta zama mowa. Har yau kuwa ba sauran yayansa wanda yayi Alkalanci. Akwai wani magajin makarata wanda Alkahi manga ya amince masa kwarai da gaske, ana ce masa Mallam Abdurahman. Bayan rasuwarsa shine ya 'zama Alkali. Shi kuma shine ya haifi Alkali Gamo. Alkali Gambo mutum ne mai ilmi sosai. An haifeshi lokacin Sarkin Zazau Abdusalami shi Ambashi Alkalanci lokacin Sarkin Zazau kwassau. Da ya nada shi sai ya kasance yana Alkalanci a gida saboda baka ya sami lakabin Alkalin Garka Kuma ya kasance yana dayawan mata matarsa guda hudu da kwarakwai yana da kuma bayi masu yawa. Kuma ya dade yana da shekaru masu yawa.

Lokacin da kazo zaben Sarki bai goyi nada Alu dan Sidi ba. A wani labari ance gardama suka yi. Akan ccwa shi Alkali Gambo idan yayi Sarki ya daure shi. Da Alu Dan Sidi yayi sarki sai yasa aka rushe gidan.

Bayan ancire Alkali Gambo, sai kasa Alkali Nuhu shine ya rike har karshen Alu dan Sidi. Daganman sai Alkali Ummar Faruk. Bayan Rasuwar Umar Faruk sai Alkali yaro (Ibrahim) Dan waje Alkali Gambo.

Yayan Alkali Gambo.
(a) Alkali Yero (b) Mallam Haruna © Adamu (d) Yamusa (d) Abdulkareem.

GIDAN SU RILWANU LUKMAN
Hajiya Raliya Muhammadu 28th February, 1998

Farkon Wanda yazo Zaria ancemasa Walijo. Ya tasanc daga birnin Kebbi, yace ma Sarki Musulmi yana son yazo Zaria lokacin Sarkin Zazzau Sidi, Yazo a kabashi Masauki. Bayan kwana biyu Sarkin Zazzau ya tashi wuri a tagwayen kudidduli. Sarki Sidi kuma yaba Walijo

arsa da aure mai suna Hasiyatu. Ita Hasiyatu ta haifi Alkali Bakabe shi ya haifi waliyi Salihu. Wannan gidan an gina ma Mallam salihu ne wanda a ke kira gidan Alkali Likuman.

Shi Mallam Salihu ya haifi ya'ya guda uku, dikko, Lukuman, da Yakubu. Lukuman yayi muhuti kafin yayi Alkalanci. Yayan sa guda goma sha uke ne (1) Mallam Musa (2) Muhammadu (3) Yusuf 94) Ibrahim (5) Tijjani (6) Shehu (7) Matan Dodo (8) rilwanu (9) Asma'u (10) Sa'adatu (11) Aishatu (12) Hauwa (13) Maimunat (14) Khadijati (15) Hassanatu (16) Hannatu.

APPENDIX 27

GIDAN GWAGWA 10 - 4 - 98

Usman Ibrahim Gwaga Age 62 Years:-

Ainihinsu su mutanen Katsina ne cikin gidan Dallazawa. Da Sarautar ta tashi ne daga gidan su sune suka zo kudu. Da Sarki Shanu da Bello da kuma Dallaje. Shine asai suka zauna a inda a kayi Gaskiya corporation yanzu. Daga Baya shine suka iso cikin birnin Zaria lokacin Sarkin Zazzau Alu dan Sidi.

Shi Bello shine ya haifi Gwagwa, shi Bello kuma tela ne yana dunki yana sayarda kaya ne a hanyar Abuja wanda a ke ce ma wurin Gwagwalada. Ainihin gwagwa sunansu Ibrahim. Yanzu zuriyar matanen gida gwagwa sun kai goma a unguwar.

APPENDIX 28

GIDAN GALADIMA SALMANU.

Musa Muazu 65 years.

Kakaninnsu sunzo tare da Sarki Zazzau Abdulkareem ne, sunana kakanninsa wanda yazo ana ce masa Ahmadu. Asalinsu fulani ne daga futa toro. Sun bar nan su ka zo suka zauna a Katsina suna wa'azi; kuma Zariyan su sune suke limanci a Katsina kafin ayi Jihadi; Bayan an yi Jihadi Mallam Ahmadu ya zauna, Zaria shine ya haifi Abubakar, shi kuma Abubakar shine ya haifi Galadima Salmanu. Gakladima Salmanu Abokin Sarkin Zazzau.

Sambo ne wanda tare ne suka taso tun kanana. Sukayi ta tsahi wajen neman sarauta. Da Sarkin Zazzau Sambo yayi sarautar, sai ya nada Salmanu Galadima. Galadima Suleiman yana da yaya kamar (a) Abubakar Sarkin yaki wanda shike shine (kakan Sarki Fawa) (e) Yamusa (Kakar Alkali M/Jalal) (f) Musa (g) Nuhu (h) Muhammadu Sada (l) Bukhari (j) Yero. Cikin yayan sa mata sune (a) Kilishi Ita ta auri dan Sarkin Zazzau Kwassau (b) Fendo Itace Uwar Sidi wanda ta auri Madaki Saidu zamanin Sarkin Zazzau Alu Dan Sidi (c) Maimuna (d) Asabe (tayi Aure cikin yayan jikokin Abdulkareem aka haifi Muhammade 9Alkali yahaya), (e) Bilkisu (f) hare (tayi aure gudan magatakarda sambo aka sami mai riga. (f) Kuburatu Tayi aure a kaya Giwa yaron Galadima (g) Ta auri Mukadashi Galadima.

DETAILS OF

INSTALLATION CEREMONY

OF

ALHAJI SALMANU GIWA

AS

GALADIMAN ZAZZAU

BY

HIS ROYAL HIGHNESS
ALHAJI SHEHU IDRIS CFR
THE EMIR OF ZARIA

ON SATURDAY 20TH APRIL 1985

BRIEF BIOGRAPHY OF THE NEW GALADIMAN ZAZZAU

Born in 1929, at Giwa Zaria, Alhaji Salmanu was the son of Moh. Bello who migrated to Giwa from Zaria with his father Abubakar Sarkin Yakin Galadima in 1907. Alhaji Salmanu started early in 1956 as an employee of cotton damp at Giwa. He was transferred to Kaduna in 1958 and was appointed an LBA (Licenced Buying Agent) of the Northern Nigerian Marketing Board in 1959. It was from this time that he became widely known all over Zaria Emirate especially in villages where he was buying cotton and groundnuts. In 1975, Alhaji Salmanu abandoned the LBA business and decided to go International. He was later involved in high level construction business, with the Federal and many states governments in this country.

Contrary to his profession, Alhaji Salmanu was not from a business family, infact he is from the celebrated family of the famous Galadiman Zazzau Salmanu. History has it that his great grandfather Ahmadu came to Zaria in 1804 from Katsina to join his brother the late Abdulkarim the third Fulani Emir of Zaria. As at that time, Mallam Abdulkarim has been appointed the Sa'i of Zazzau. M. Ahmadu was the father of Abubakar Muzadu who inturn gave birth to Salmanu. In 1881, the late Emir of Zaria, M. Sambo son of Abdulkarim turbanned Salmanu as the Sarkin Bawa and after just three years gave him the title of Galadiman Zazzau. He held this title throughout the tenure of late Emir Sambo, Yero, Kwassau until 1905 during the tenure of late Emir of Zaria.. Aliyu

Abubakar, the eldest son of Galadima Salmanu was the father of Moh. Bello who was also the father of Alhaji Salmanu, the new Galadiman Zazzau. In short the present Salmanu has accented to the seat and title of the late Salmanu, history has thus repeated itself. He is married with 24 children, 9 males and 15 females.

THE DUTIES OF GALADIMA

The title of Galadima is one of the oldest as well as senior traditional titles not only in Zaria but also in all Hausa kingdoms. It's because of its importance that besides the Madaki it's only the Galadima that enjoys the patronage of the Emir's royal drums (Emir's Tambari) for a period of seven days.

During the war years, the Galadima as one of the warriors, rides immediately behind the Emir. After the war periods, the Galadima assumed the role of one of the senior councillors in the Emir's council. It's on record that of all those that were opportuned to hold this title from the beginning of Fulani rule to date, the most famous of all of them has been Galadima Salmanu.

The new Galadima is expected to use his title to protect and project the image of royalty institution as well as that of the people of Zaria both at home and abroad.

APPENDIX 28

GANGAREN TUKURWA

Alhaji Sambo Yahaya Age 78 Tanimu Bula

Asalinsu mutane Katsina ne. Daga Ruma cikin iyalan Dan waire. Wand ya taso gada Ruma anace masa Mallam Danbako yazo ne yana Malami yana ko yarda karatu. Shi Danbako shine ya haifi Mallam Achi. Shi mallam achi ya haifi yaya fuda goma maza da mata. A cikin birnin zaria sannar kuma yahaifi wadansu a garin gangara. Yayan da ya haifa sune.

(1) warka (20 Mohammadu (3) Harande (4) Yero (5) Balarabe (6) Suleiman (7) Haranda (8) Jumare)9) Abdullahi (10) Gindo

Mata kuwa sune (1) Fand (2) Kumbo (3) Sala (4) adama (5) Tsohuwa (6) Katambari (7) hafsatu. Sanan shi kuma Mulammadu yayanshi tara ne.

(1) Alu (2) Lami (3) maude (4) Utanaimu (5) Yahaya (6) Aishayu (7) Kadarko Hafsatu (8) Shamau (9) Alhaji Sani

Yayan Alhaji Tanimu sune.

(1) alhaji Wayaya, (2) Aminu (3) hafsatu (4) Saude (Taannabi) (5) Aliyu (6) Rakiya (7) Rakiya (8)Abubakar (9) Ummaru (10) Aliyu (11) Yusha'u (12) Danbala.

Cikin yayan da haifa a Gangare shine Nuhu. Shi kuma Sai yar inna

(2) Ayuba (3) Yahaya Shi kuma Yahaya shine ya haifi

(1) Mairo (2) Nuhu (3) Maude (4) Sambo (5) Kilishi (6) Ramatu (7) Duma (8) Ali (9) Bilkisu (10) Abubakar (11) sala (12 Agumi (13) Ibrahim (14) Audi.

Shi kuma Nuhu shine ya zama wazirin Zazzau lokacin Sarkin Zazzau Aminu.

Shine ya mutu zamanin Sarki Zazzau Shehu idris.

APPENDIX 30
ANGWAN LIMAN

JAAFARU Ahmadu 40 years, liman na farko na garin wanka
Isa Falalu 52 years

Abdullahi Ahmadu 62 years; Wanka, 7th January, 1989

Shi mallam Ahmadu Yazo garin wanka ya zauna ne bayan yakin Abuja lokachin sarkin Zazzau Sidi. A wannan yakin ne a ka kashe musulmai da yawa. Kafin Zamansa a Wanika ya zauna a wani gari ta a ke ce Masa karau karau.

Dalilin da yasa yabar Zaria shine mallam Sambo yace mashi fa, fada ta soma lalacewa idan zaka bar wannan gari karkayi nisa. Da yatashi sai yatafi Tukur Tukur in da gonarsa take, daganan sai kawunnsa Mallam Ladan Yace suje Awai da ganann su ka zo suka kafa garin Wanka.

Akwai gidan fagachi Ahmadu, shine dan Limamin Gabdo ne.

Daga chikin manya manyan gidaje a unguwan a kwai gidan mai gammo (2) Gidan mai unguwa Datti (3) gidan mallam Isa (4) Gidan Rajo sanna sai gidan mallam barau

Gidan Mallam Barau, 12th Dec. 1997. Age 90 years

Su fulani ne daga Borno. Da dirori da yar galla uwansu daya ubansu daya. Sun yi hammayya ne wajen sarauta basu samuba. Si suka taso da shanunsu da bayin su suka sauka a dan soshiya, suka shekare biyar, da ganan sai suka taso suka shigo zaria. Sun iso Zaria bayan anyi jahadi ne. Sannan kuma mutanen da suke unguwan suka gudu zuwa Abuja. Da , mallam Musa da Yamusa da su Dirori suka tafi Sokoto suka raka su mallam Musa da Yamusa. Shi mallam Musa shi kuma aka ba shi tuta.

Dirori Yahaifi sambo. Galla ya haifi fagachi Adamu da sa'I sambo. Lokachin sarki Abdullahi akayi ma sarautan sa'i. Abdullahi Dan Muhammadu sani. Kanuwar sambo ana cemata azumi ta fito daga wannan gidan sannan ta auri sarki Abdullahi. Sai sarkin Zazzau Abdullahi yace anada sambo sa'I don yarika sha nono. Sannan kuma yabashi Hakimcin Keffi da lafiya

Sambo shi ya haifi Adamu. Shi kuma Adamu yahaifi Mallam ummaru, (2) Ladan, (3) Balarabe (4) Bawa ta Hunatu.

Yayan fagachi adamu (ya manta lokachin dayayi fagachi), sun gidado (2) Mahmuda (3) mai gamo (4) Hafilu (5) Isa.

Jikokin Fagachi sune

Sallama (2) Na Dembo (3) sai Isiyaku (4) Sai Abdulsalami (5) sai Abu shi shine yahaifi Ahmadu. Sa'i Abu Yazama Sa'i Ne lokachin sarkin Zazzau kwassau Sa'i isiyaku kuwa da Sa'i Abdussalami Sunyi sarautar Sa'i ne zamanin sarki zazau yero zuwa kwassau

GIDAN MALLAM ISA

Wanda ya fara kafa wannan gidan shine malam Isa Yazo Zamanin sarkin zazzau kwassau ne. Kuma shi mutumin Tsafe ne. Sunzo Zaria ne tare da mallam bazanfare Zurioin da Allah ya bashi, sune Mata ta Farko Aishatu (1) laria(3) mairiga (4) dahiru (ladan) wanda yake shi jikan gidan sarkin Ladanai ne (5) maimuna.

Mata ta tahafi (10 Time (s) Shehu

Mata ta haifi uku (1) Mairiga

Mata ta hudu ta haifi (1) ummah (2) mallam Ali

Abu ladan shi yaba mallam isa Aure aka sami Aishatu. Shi mallam isa yaji labarin Abu ladan a can tsafe shine yace bari su zu su zauna a wurin Aishatu ta hafi (1) Kande (2) Barau (3) alhaji Kanlawa.

Larai ta haifi (1) Ibrahim (2) Abubakar (3) Saidu (4) Kande (5) Mairo (6) aishatu.

Mairiga ta haifi (1) Abdullahi.

Dahiru ya haifi (1) Halima

Shehu bai haihuba

Amma bata haihuba

Mallan ya haifi (1) Hassan (2) Rahinatu

Mairiga ya haifi (1) Dan lami.

Mallam Isa yazo Zaria da Karatunsa ne, a lokachin Abu Ladan wanda shike shine Ladanin Gari Shi mallam Isa yayi Zamani da kwassau har zuwa sarkin zazzau ja'afaru. Ya sami kamar shekara shidda da jafaru.

Bayan wannan gidan a kwai kuma Baban gida wanda ake ce masa Gidan Alkali Datti su mutane wadanda sukazo da ga kauyen Hunkuyi, Bayan zuwan Turawa.

APPENDIX 30 A

ANGUWAR ZAKARA

Alhaji Abdullahi Na Haruna 80 years

Ita unguwar zakara da can ita unguwa ce ta malami , masu ilimin na shanin alkurani. Akwai wani malami ana cemasa mallam Ali, to shine lokacin nan idan Almajiran sa sun zo lokacin sallah, rika daga muryar kama adan. Ranar da bashi.

Wanda yake nesa bazai jiba. To sai kaji ance yau ba zakara, ba aji kiran salla ba. Kafin kiran Anguwan da suna anguwar zakara anace ma unguwar runguwar baki.

a. Tsoffafin gidaje sune gidan mallam sambo
b. Mallam Abdu Na Gimbiya da gidan Turaki.

GIDAN TURAKI

Su Fulani toron cewa sun zo kafin ayi Jihadi suka zauna da bu kokin su.

Tare da Bayin Mallam kayi na unguwar Bishar. Cin Zurioin da suke unguwar sun samu ne daga zurioin mallam kayi. Babban sanaar mutanen engin. Shine dukanci. Daya daga cikin zurioin shine gidan Mallam Sambo. Su wadanda zuria toronkewa ne kuma iso zaria ne tun kafin ayi Jihadi.

ANGUWAR BISHAR IBRAHIM MAI DUNIYA - AGE 65 YEARS

Akwai wata Al Janna da ake ce mata Bishar. Ita wannan Aljannar tana nan har yanzo ba san inda ta ke ba. Ita Aljannar takon fito akan mace mai kyawo ce sosai. Idan mutane suka nema ta, suka matsa mata to idan tace Bishar shikenan sai ta bace.

Manyan gidaje A unguwar sune:-

a. Gidan Sarkin Zazzau Abdulssalami
b. Gidan mallam na Gimbiya.
c. Gidan wanya Adamu
d. Gidan wanya Ibrahim
e. Gidan magaji Jesambo

Sarki zazzau Abdulsalami.
Shi Abdulsalimi dan muhammadu kayi ne. Shi Muhammadu kayi ne. Shi ne ya Abdussalami da kaninsa mallam Jamo.

Yayan Abdussalami

1. Muhamman Sani
2. Usman
3. Abubakar
4. Sai Zubairu
5. Mahmadu Mizawaje

Yayansa mata sune

a. Habibatu b. Khadizatu c. Rukkayyatu d. Rahinatu

Jikokin Abdussalami ta wajen Sa'i Zubairu.
Sune Yero Zabairu
Abdusamadu Zubairu
Alhaji Ummaru Magatarka dan Iya
Rahinatu yar Lalle

1. Muhammadu Dan Abdussalami shi ya mutu bai da yaya
2. Muhammadu Sani dan Abdussalami shi yahaifi
3. Makaman Jisambo - Ibrahim
4. Alhaji Ummaru Magatarkada Iya dan Abdussalami shine ya haifi

    a. Lawal Babban Dansa shine (Secretary fr Minister of iron & Steel).
    b. Abdu Ummaru
    c. Samaila Ummaru
    d. Garba Ummaru
    e. Mudi Ummaru
    f. Bello Ummaru
    g. Mudashiru Ummaru
    h. Habibatu
    I. Balaraba

j. Hajiya Lanti
k. Ladi Madaka
l. Amfana

Makama Jiranbo yayansa sune (a) Yahaya Makama (b) Aminu Makama. Mata kuwa sune, Tunba, Uwa, Dodudu wa da Gude
Dantsoho shine ya haifi Atine da Bayi
Jikokin Abdusalami ta wajen mata sune

1. Khadizatu ta haifi Agwai Gwaggon Jaware (b) Mallam Maiwada Agwai (c) Mallam Jumare Agwai (d) Mallam Goma Agwai (e) Mallam Gambo Agwai (f) Mallam Gambo Agwai. Yanzu A Anguwu ne ake cemasa gidan fulani (g) Salihu Agwai.

2. Rukayya ta haifi makama Jaafaru (zamanin Sarki Zazzau Ibrahim ya rike wannan sarauta). Rahmatu ba ta da da ko jika. Yayynta su suka gajeta.

Daganan kuma sai Abdulkareem *yayi masa sarautar sai saman kuma yayi masa sarautar magajin* gari. Saman kuma dansa Anace masa Abdulqadir akayi masa sarautar Sarkin ya ki Daboobinsa akabashi wadansu wuri a kasar soba anace masa magada, ya ajiya dabbobinsa da bayinsa.

Abdussalami yana da kane, shine Mallam Jamo. Shi Mallam Jamo ya haifi da guda shine Mallam Dabo. Shi kuma Dabo ya haifi (a) Alhaji Dikkon Rimi (b) Alhaji halline (c) Alhaji Alu Baba (d) Alhaji Goda.

GIDAN MALLAM ABDUSSAMADU

Shi Bababan malami ne na Addini. Shi bafillatini ne, batoronke suna zaune a Zariya tun kafin Ayi Jihadi. Saboda karatunsa ne yasa Abdussalami yabada yarsa ga Mallam Sambo aure. Yana da kuma wadansu yaya mata kamar su kumbo da khidizat.

GIDAN MALLAM SAMBO

Suma Fulani ne sullubawa dagacikin manya an Malamai na unguwan. Shi Mallam Sambo shi ya haifi Mallam Turaki. Shi kuma Mallam Turaki ya haifi Mallam Yero shi Mallam Yero shi ya haifi Khadizatu.

Jamar sarkin Zazzau Abdussalami Baban yaronsa da suke zuwa wurin dash; yaki shine sallau Tajiri sai kuma. Muhammadu Gani mai jima. Dundashiru da tunga makeri da sauransu.

Akwai dagakicin yara Abdussalami wadan da suke yin Dukanci kamar dinki jaka, gafaka allo, sauransu. Aimihin maisidan ana cemasa Abubakar Alabura.

GIDA WANYA IBRAHIM

Sun shigo bayan jihadine umbutawa, lokacin sarki Zazzau Sambo. Wanya Ibrahim yayi sarauta ne lokacin sarkin Zazzau Ibrahim. Wanya Adamu shine yagaji wanya Ibrahim.

MAGAJI JISAMBO

Zamanin Ibrahim a ka fiddashi daga sarauta lokacin ja'afaru da yake abokisa ne, ya zama a jisambo abokin Sarki.

LIMANCHIN KONA:

Sunayen wasu daga cikin Limanan Kona:

1. Muhammadu Yasa - shine ya taso daga Madina.
2. Muhammadu Buhari - shine daga masar suka taso zuwa Madina.
3. Ahmadu
4. Haruna Al Rasheed sune suke kafa garin Tofa shekara dari kafin zuwan Almaghili shine (sadarul Dini, Qutubul biladi wal Amsari (kirjin Addini Kusar Burine)).
5. Hameed shine wanda Shehu Usman yazo yayi karatu wajensa.
6. Muhammadu Sani (Zamanin Makau da Mallam Musa.
7. Iyal
8. Mai Jan Riga (Abdullahi).
9. Mahmuda Sani Babban Almajirin M. Ibrahim shi banufe ne.
10. Suleman Dan Ibrahim (Mijinyawa). Kome arzikin mutum janfa da wando amma naka Babban Raiga ne.
11. Ahmed Tijjani Balarabe
12. Mallam Aliyu Ibrahim (Informant).

LIMANCHIN ALFADARAI: Gidan Alfadarai Mallam Aliyu Shekara 90

Asalin maigidan yazo daga gabas ne ana ce masa Salihu ne da Alfadarinsa ya zo. Sarkin wannan lokacin ya basu wuri da gonaki suka zauna. Yayi karatu a gidan limamin kona, sannan kuma daga baya yasamu Almajiransa. Lokacin da Shehu Usman Dan Fodio yazo kafin ayi Jihadi ya kwana a gidan Mallam Salihu kwana arbain daganan sai yatafi gidan kona. Kadan daga cikin yayyan Mallam Salihu, sune Ibrahim da Ango. Yanzu zuriyar sa suna da gida sama da ashirin a Unguwan.

LAWAL SULE ABDULLAHI, Age 36 Years

GIDAN MALLAM GAJERE:

Aslinsu mutanen Bauchi ne wajen wani gari da ake ce masa Leren Bauchi. Wanda yazo ana cemasa Jihad ba da dadewa ba. Shi kuma Aliyu ne yazo batyan anyi

Abba shine ya haifi Abdurahman, Abdurahman shine kuma ya yi haifi Suleman. Shi Suleman ya haifi Ustaz. Sanaar gidan shine noma da Almajiranci.

Ibrahim Sarki 80

Muhammadu Ladan Haruna 92 19-04-1999.

GIDAN M. HASSAN

Asalinsu daga Iraq ne sukazo Katsina saboda kasuwanci da malanta. Wanda yazo shine Mallam Bature zamanin limamin kona Mai Jan Riga (zamanin Sarkin Zazzau Dalhatu) shine ya haifi (a) Mallam Hassan (b) A'ishatu (c) Liman Kwaire (d) Musa (e) Usman da kuma Haruna (Father of the Informant).

USMAN ALIYU 50 Years

Karofin Taba Limanchi

Ana kiran wurin karofin taba, saboda akwai tushen itace Taba anan wurin. Sannan kuma akwai Rijioyin Rini sama da 100 wadanda baa san lokacin da akayi su ba.

LIMANCHIN IYA

Alhaji Gambo Sawaba 79 Years - sun 199.

Limanchi ta ka su kashi uku (1) Limachi kona (2) Limanchin Alfadarai (3) Limanchi Iya.

Limanchin Iya

Limanchin ita ta dauko Iya. Anguwan Iya ta sami suna ne saboda akwai wata yar sarki da aka taba bada aurenta ga wani malami wanda yake zaune a limanchi kona. Saboda haka sai suka bashi daga limanchin kona zuwa nan wurin da aka sa masa suna Limanchin Iya.

ANGUWAN MASA MALLAM IDI - Age 70 Years.

Da wannan unguwan yana cikin limanchin kona ne, doga baya ya zama unguwar masa. Tsofafin Gidaje su ne gidan (a) Mahauta (b) Makranta (c) Gidan Mallam Yahuza da Gidan Masa da Gidan Fulani.

GIDAN MAHAUTA

Asalin mutanen kasar Kano ne, a wani gari wai shi garun mallam. Sunzo Zaria ne lokacin Sarkin Zazzau Yamusa. Kakansa yana da shekaera 120. Ya rasu likacin sarki Zazzau Jaafaru.

Sunansa Abdullahi ne. Da yazo ya zauna ne a unguwar Rubu sai ya sami wannan gidan wanda kowa ya saya zai mutu. Yana sgyara wa sai yaga maciji, da ya bude ya gansa sai ya rika yanka Tozo kullum yana bashi. Saboda shi Mahauchi ne ya na da yaya guda uku.

(a) Muhammadu (b) Lami (c) Yar Dada.

(b) Muhammadu Shuni ya haifi (a) Goshi (b) Salch (c) Yanbiya (d) Gambo (e) Idi (f) Musa (g) Kande. Idi na shine raformnt.

GIDAN MUSA

Asalin su daga Kano ne yazo zamanin Sarki Dalhatu ne mutanen Karaye ne. Anzo dashi makaranta ne a kaba Mallam Bawa na limanchi. Sunan sa shine Mallam Abdu. Lokachin da ya isa aure akayi masa aure shine ga haifi Idrisu Yusuf, da Danjuma.

GIDAN MALLAM YAHUZA 60 YEARS

Asalinsu mutanen Yantumaki ne wagen Katsina, wadansu daga cikin yanuwansu da suka taso daga Katsina sun nufi Kano ne, wadansu suka nufo Zaria. Kakansu shine Mallam Balarabe ya na da ga cikin wadan da suka nufo Zazzau. Da su ka shigo kasar Zazzau sai suka zauna a kauyen Rahama daganan sai Kwanan Farakwai, sai Turunku. Shi Mallam Balarabe ya zone lokachin Sarkin Zazzau Muhamadu Sani. Ya kuma haifi Abdullahi, Abdullahi shi kuma ya haifi Muhammadu, shi kuma Muhammadu ya haifi Sa'adu. Shi Saadu shine ya haifi Mallam Yahuza. Zuriyar Mallam su goma sha tara ne maza tara mata goma.

Maza sune:

(1) Yusuf (2) Ummaru (3) Sani (4) Sirajo (5) Salisu (6) Mukhtar (7) Gali (8) Mustapha (9) Rashidu. Mata kuma akwai Safiya, Saudatu, Khindatu, Karimatu,

Salamatu, Khaulatu. Shi Mallam Yahuza ya shahara akan figh da Tauhidi. Ya kuma wallafa littafi sun kai Ashirin.